zuciya d kwanji1) Kyakkyawar mace matuka gaya! Fara sol, mai kyakkyawan diri na matsakaicin jiki,tsarinta ya bayyana matsayin da kuma matakin da take kai na rayuwa,wato girman nauyin aljihunta,ko kuma na wanda ya dauki nauyinta. Da ganinta mace ce mai kasaita gaske,tare da dabi'ar son mulki da nuna ita wata ce.Ga ta kuma da karamin jiki,sai wancan kyau da yanayin shan kamshinta ne kawai ke sabbaba mata kwarjini, yake sa wa babba da yaro ke shakkarta,mace ko namiji duk wanda ya kalleta sai ta tsuma shi,ya ji kamar ita ta girmi kowa a idonsa,girma ba na shekaru ba,irin na fada a ji,domin dai shekarunta talatin da biyu. Tana zaune ne akan farar kujera karkashin bishiyar dorawar turawa a wani sashe na gidan zoo da ke kano,tare da wani mutum mai alamun hakuri da fara'a,dan kimanin shekaru hamsin.kallo daya zaka yi masa ka gane inda wannan kyakkyawar matar ta ci ta tada kai. Yadda wajen yake da alamun kadaici haka fuskokinsu ke bayyana damuwa da alamun kewa,shi yasa wajen tsit yake sai kukan tsuntsaye iri iri,sannan akai akai mutumin nan kan dubi matar nan fuskarsa cike da alamun miliyoyin kauna wadda ta zarce misali,kamar

jikinsa har bari yake,amma wannan matar ko a

jikinta,tata fuskar babu abin da take bayyanawa

sai gajiya da kuma gundura. Can ya nisa a

tausashe cikin ladabi irin na kwararren masoyi ya

ce. "Kar fa wannan ya bata ranki Fatima, ma

sanki da son sanya wa kai damuwa...... Kin

sa....." Sai ya yi shiru yana dubanta kamar zata

yi magana,sai kuma ta hadiye abarta,ta kuma

kawar da kai. Ya jima yana kallonta,bawan

soyayya dai sosai,sai kuma ya sake duban

agogon hannunsa,ya kara sayke ido a kanta,a

ladabce kamar wata gyatumarsa,ya ce, "Ki yi

hakuri kin ji Binta?" Nan ma ba ta tanka ba, ba ta

ma ko dube shi ba,illa ta dan muskuta. Zai kara

magana ke nan sai ya hango wani matashi yana

nufo su,mai kimanin shekaru talatin da uku..2) .wankan tarwada mai matsakaicin tsawo da fadi,akwai alamun kan sharafinsa yake,ama'anayana jerawa da zamaninsa. Yana sanye ne da dakakkiyar shadda ruwan shanshanbale(purple),dinkin bankole da tajajjiyar suma wadda ta yi masa tsari matuka,shi ma yana da alamun fara'a,sai dai mai dakakkiyar fuska ne ta jarumai kuma irin wadanda kallonsu kawai ba zai sa ka iya yanke musu hukunci ba. Da barin jiki mutumin nan ya dubi Fatima,fuskarsa kamar gonar audiga ya ce. "Kwantar da hankalinki Binta,kin ganshi ya karaso". Ta dago ta yiwa matashin nan kallo daya,sannan ta kawar da kai gami da karamin tsaki,har ya karaso ba ta kuma sha'awar kallonsa ba. Tana jinsa suna gaisawa da mutumin,sannan ya juyo kanta da muryasa kamar wanda aka yiwa dole ya ce. "Sunnun madam" Ta motsa baki,amma sai ta hadiye amsa sannun tasa ta hanyar kyabe baki da kawar da kai,sai wannan mutumin ne ya wofintar da abin da ta yi da cewa. "Abdullahi har mun gaji da jira,ka san fa ina da sabgogin yi, ita kanta madam ba ta kaunar irin wannan jiran". "A tausashe Abdullahi ya ce. "A yi min afuwa Alhaji,na kai daya daga cikin iyalija asibiti ne,saboda tana fama da ciwon ciki. "Allah ya sauwake". Alhajin ya fada gami da sauke kallonsa kan fatima wadda ta mayar da idonta kallon wani sashen daban,kamar ba a gabanta suke ba, A tausashe ya ce. Fatima wannan shi ne Abdul da muke magana a kansa". Ta juyo ta dubi Alh a kaikaice,sai dai ba ta tanka ba. Ya kara fadada fara'arsa yana dubanta,ya ce. "Ina fatan ya yi miki?" A lokacin ne ta kuma daga kai ta dubi Abdullahi wanda shi ma yake duban wani wajen daban.tun shigowarsa kallo daya ya yi mata bai kara marmarin kallonta ba,ko yanzu da

jikinsa ya ba shi tana kallonsa sai ya kara yin kicin kicin ya ci magani sosai. Ta kawar da kai daga dubansa cikin tabe baki,har da tsartar da yawu,ta ce. "Alh ya yi mana,tunda ba a kafata zan daura shi ba". Alh ya yi karamar dariya,sannan ya basar ta hanyar duban Abdullahi ya ce. "Abdullahi wannan ita ce Fatima,wadda na fara yi maka bayani rannan,matata ce, shekarun mu goma tare,muna son junanmu kwarai! Wata kaddara mai zafi ta gifta mana na yi mata saki UKU a lokacin daya.Rayuwa ta yi wahala a gare mu,domin ba zamu iya rayuwa ba tare da juna ba.Ga shi kuma ba mu da damar kasancewa taren..3) A baya mun dan yi wasu yunkurin na yin auren kisan wuta don mu sami damar mayar da aurenmu, kawunta ya dago mu saboda yanayin wadanda muke gayyatowa su yi mana wannan aikin. Wannan karon sai muka zaboka bayan mun gamsu ka toshe waccan barakar da ta ke sa wa ana dago mu. A yanzun ina mai gabatar da kai gare ta, shin ka amince zaka aure ta amma ka sake ta cikin wata daya? Ya kamata ka dauka mana wannan alkawarin.Ni kuma na yi alkwarin biyanka ladan kudin miliyon uku,ya ya ka gani?" Alh ya yi shiru yana dubansa,inda shi kuma ya muskuta cikin nuna tsananin girmamawa ya ce. "Kamar dai yarda na fada maka rannan,na amince da muradinka......" Fatima ta tare shi tana masa kallon goma ahu. "Ta ya ya zamu gaskata alkwarin ka alhalin yanzu ka gwada mana ba ka san darajar lokaci ba, ka shanya mu kawai kamar wasu kannan yara?" Abdullahi ya yi kasake cikin dakewa da shan kamshi,yana motsa bakinsa a hankali har ya bar abin da yake son fada ya bi ruwa.sai kawai ya bige da kallon Alh,wanda yake kallonsa daya bayan daya.Tsarin nasu ya burge shi,kamar halayyarsu daya don haka ba zasu taba jituwa a inuwa daya ba. Ya dubi fatima sannan ya kara duban Abdullahi,wanda tuni ya dauki kai,ya ce. "Ai ya wuce Binta,ban zabo shi ba sai da na amince da shi.Dan manyan gida ne gidan da aka san kimar amana,kuma bai yi kankanci a ce shi kika aura ba.yana da alkibla,yana da sana'a.Ba shi cikin shirgin sawa,duk wadannan makamai ne cikin cimma burinmu wanda za su yi tafiyar ruwa da kwakawar kawu. Ba ta ko motsa ba bare ta tanka,shi ma Abdullahi sai ya ga ba shi da ta cewa. "To yanzu mene ne abin yi? Ko motsi Abdullahi bai yi ba,sai fatima ce ta dago ta harari Abdullahi,sannan ashagwabe ta ce. "Gaskiya wata daya ya yi min yawa Alh,don ko sati daya tamkar akan kaya zan yi shi..." Ya tare ta cikin tausasawa. "Na sani, amma babu wata mafita wadda ta fi wannan ita zata dauke idanun basaldawa....." Yadda ta yi kicin kicin ya sa ya dakatar da maganarsa da murya nan shi,ya ce. "To yi shuru,Abdullahi ma haka. Dukkansu sai numfarfasgin kawai suke,da alama kowa dacin rai na damunsa,sai kawai Alh ya zuba musu ido,a sanyaye ya dubi Fatima sannan ya juya ga Abdullahi a kausashe ya ce. "Wai me ye haka? Ba na son wannan cin maganin da kuke,kun san fa zaku yi ACTING ne sosai yadda da wahala a gane abin da ke binne,kun gane ko? Ko motsi fatima ba ta yi ba,sai ma kara hararar Abdullahi da ta kara yi,kai tsaye shi kuma ya yi murmushin da har kumatunsa suka lotsa,yana duban Alh ya ce. "Kar ka ji komai Alh,ai nan ba wajen da zamu yi acting din ba ne, shi yasa duk muke tsaye akan kafafunmu4) Alh ya sauke ajiiyar zuciya,ya gyara zama ya ce. "Ai shi ke nan,zaka fara zuwa zance.ke ma Fatima ki karbi shi da fuska mai kyau yadda su kawu ba zasu dago ki ba.ku yi acting sosai yadda za a zatar muku kaunar juna.ya yi kamar zuwa biyu sannan ya tura magabatansa ayi maganar aure, idan an zo sa rana,kar a sa lokacin mai tsawo kamar sati biyu haka sai ta tare". Ya saka hannu a aljihu ya ciro wasu mabudai samfura biyu,na mota da na kofa,sannan ya fito da rubutaccen cek ya hada ya mika wa Abdullahi yana cewa. "Daya makullin mota ne, ka zo office dina gobe ka dauka,ka fara amafanin da ita tun daga goben, don kawar da idon mutane.wannan mukullin gida ne,shi nake son ta tare a cikinsa tunda nasan ba ka da muhallin da zai dace da ita. Sannan wannan cek ne na kudin dubu dari bakwai ka fara hidimar auren da su dai dai matsayinka ka ji? Idan kana bukatar kari ka zo ka same ni, ladan aikinka kuma ranar da ka sallame ta,ba zaka bar gidan ba sai ta ba ka.kuma muna bukatar ka yi mata saki uku ne,ina fatan kana fahimta?" Fuskar

Abdullahi ta nuna alamun zurfafa a tunanin,yana faman juya mukullan da cek din sai da Alh ta dure, sannan ya dube shi da kyau,ya ce. "Idan haka ne gaskiya akwai matsala". Duk suka kara dubansa,har da fatima me shan kamshi,ya dan ja fasali tukunna ya ce. "Mahaifina yana da matukar dora ido akan 'ya'yansa,abun ne mai wahalar gaske ya ganni da gidan da kuma sabuwar mota bai matse ni na fada masa inda na samo su ba. Kuma wannan dalilin ne da zai kafa min hujjar hana ni auren gaba daya. Fuskar Alh ya bace ya ce. "Ayya! To ya ya za'ayi ke nan?" Abdullahi ya yi kasake sannan ya numfasa. "A bar maganar mota tunda ina da tawa, ko dai ta rainawar ce,maganar gida kuma idan zai samu tunda komai na maneji ne,me zai hana ta yi manejin a gidana? Gidan yana da yalwa dama sashen mata uku ne,sai nawa.yanzu haka matana biyu,kuma ina neman wani auren har an sa min rana,saura wata shida sai ta zauna a sashen amaryar bisa dole tunda ba daukar wani lokaci za'ayi ba,har an yi auren a gama kafin wancan auren ya zo" Duk suka yi shiru alamun shakku.Da kyar Alh ya nisa,ya ce. "Anya hakan zai yiwu Abdullahi? Ya ya za a yi ka hada fatima da wasu matan duk matsayinta? Idan a aurena ba ta san bakin cikin kishiya ba, ai bai kamata a naka ta sani ba...." Abdullahi ya yi saurin tare shi. "To Alh ya ya zaa hada wannan auren da naka? Ai bai kamata matana su dame ta ba,tunda babu wani dalili da zai sa ta yi kishi da su..... Amma in ba haka ba..... Gaskiya ina gudun bacin ran mahaifina...." Ya mikawa Alh makullan yana mikewa.Alh na nacin kallon fuskar fatima wadda ta kara bata rai,ya ce. "To me yasa zaka dawo min da cek din?" Abdullahi ya ce "Wai kafin ku yanke shawara". Da sauri Alh ya ce "A'a ka zauna mu yi komai yanzu mu gama,fatima kina jinmu fa, kina ganin zaki iya ace kin shiga cikin mata biyu,alhalin kin saba da mijinki ke kadai?" Ya karasa da zolaya. Ta amsa kai tsaye. "Ko mata goma ne a matsayin na 'yar ci rani bai kamata su dame ni ba. Ni na fi so a fi jaddada maganar iyakar kwanakin da zan yi a gidan ya sallame ni, sannan ko da wasa ba na so ya rabi dakina da sunan mijina,ya yi harkarsa kawai na yi tawa,ranar alkwari ya miko min certificate kawai"Zuciya d kwanji

5) Alhaji ya sauke ido akan Abdullahi,ya ce.

"Ka ji muradinmu". Babu alamun shakka

Abdullahi ya ce. "Na amsa". Yana rufe baki

fatima da ke kallonsa,kai tsaye ta ce. "Ban ji ka

ce ka dauki alkawarin ba, kuma da wacce alama

zamu yarda zaka cika?" Ya amsa cikin dakewa ba

tare da ya dubeta ba. "Babu wanda zai iya

shaidar abin da zuciya ta boye sai wanda ya

kage ta, sai ko in zuciyar ta dan yarjewa fudka

bayyana alamu.Amma ku yi min hukunci da auren

da na ce zan yi nan da wata shidda,Nasan kun sa

so ba karya ba ne, tunda a cikin mayensa kuke,soyayyar da nake wa yarinyar ta kai mizanin da ba zan iya rasata ta karamin dalili ba,wato aurenki". Karo na farko da suka dubi juna ita da Alhaji suka yi murmushi,ba tare da ta ware murmushinta ba ta dubi Abdullahi ta ce. "To in dai haka ne,kai dai ba ka san so ba, tunda ka dire mace biyu a gidanka ga ni ta uku zan shiga duk da in na kauce wata zata maye gurbina,na san kuma ba za a shekara ba ba tare da ka cike gurbi ba". Har yau bai juyo ya dube ta ba,sai dai shi ma fuskarsa da walwala ya amsa mata. "Ai babu wata me maye gurbinki,tunda naki wasa ne,ki kuma sa wa ranki,ina aure akai akai ne don ban dace da kawata ba,amma ita wannan ina jin a raina daga kanta zan kulle kofa,don zata iya amsa sunan mace hudu ma ba biyu ba"m Ba tare da wani shakka ba fatima ta ce. "To Allah ya sa,don ni ban ga wani burgewa ba wajen tara mata da ya zame muku kamar wata gasa. Suna dariya ita da Alh,shi kuma Abdullahi ya ki share maganarta,cikin karsashi ya ce. "Amin". Alh ya maganatu "Wai shekarunka nawa?" Ya amsa masa. "22nd na wata mai kamawa zan cika shekara talatin da uku". Cikin kada kai Alh ya ce.

"Ka ga ma 'yan watanin ka ba wa fatima saboda haka ka bata girmanta kamar yadda zaka ba ni, ko babu wannan shirin ai ba sa'ar aurenka ba ce ko? Ko kuwa mutum na auren sa'arsa?" Shiru Abdullahi ya yi,Alh ya rufe maganar da cewa. "To don Allah ka zama yaron kirki,kar ka sake inji fati ta yi kuka da kai,ka lallaba ta don Allah ka ga marainiya ce ko a zato ba na son bacin rantaZUCIYA d KWNJI.6) TUNA BAYA. Mahaifin fatima 'yan asalin karamar hukunmar gwarzo ne a cikin garin gwarzon mahifiyar fatima bafullatana ce gaba da baya kusan a wajenta ma ta gaji kashi 70% na kyawunta.A bangaren ginshira da shan kamshi kuma sai ta gaji mahaifinta wanda yake jinin sarauta. Kakan fatima wanda hakimi ne na wannan karamar hukuma,'ya'ya uku kacal ya mallaka,mahaifin fatima sai kannensa biyu,prof alkasim da karamar kanwarsy Dr maryam. Fatima ta taso ne marainiya gaba da baya.sakamakon rasuwar mahaifanta duka biyun a ranar da za'a yi bikin cikar shekarunta uku a duniya. Daga nan ne rukonta ya dawo hannun kanin mahaifinta prof,wanda a lokacin wataninsa uku kacal da aure. Kawu (prof) muntum ne mai tsantseni kwarai, kuma masanin yakamata,sai kuma ya yi dacen mace ta gari kamar shi.Don haka har zuwa

yau fatima ba ta taba dan dana wani dacin da ya yi kama da maraici ba, sai ma da hankalinta tasan cewa ba su suka haife ta ba. Gidan su gidan jama'a ne matuka,don karamcin ma'abotan gidan,don haka duk wanda zai taso a cikinsa sai ka tarar da shi wayayye ma'abocin iya mu'amala,sannan mara kyashi ko kadan,saboda sabo da jama'a". Kawu na da 'ya'ya shidda,babba cikinsu safiyya wadda ta ke kamar sakuwa ga fatima,tare suka yi fadi-tashin kurunciya,sai maza biyu suka biyo baya, Najib da Abdullahi,sai kuma Nasiba sannan auta khalid.Don haka duk cikin manyan 'ya'yansa fatima yake kallo san kuma taba bambantata cikin 'ya'yansa ba. Ya bata ilimi mai kyau kamar su,sannan ya jajirce cikin tarbiyyarta iyakar kokarinsa,duk da dai gatan da yake mata saboda maraicinta ya ba ta damar sangarta.ta zama wata me murdadden ra'ayi wadda ake shan wahalar canjawa manufa ko da karmatacciya ce. Tun fatima na karamarta kowa ya dubeta yasan an sami kyakkyawar mace mai sanumfashin maza sassarfa,kyawun da ya hadu da ilimi da kudin,sai ta zama wata zara'a cikin mata.Ta yi matukar farin jinin a wajen maza,har ma da matan da

Allah ya zare wa kyashi da hassada,don ma
kasaitarta da miskilancinta na wahalar gaske
fatima ta fita wani masoyi bai biyo bayanta ba.
Shekarar da ta kammala sakandire,kawu ya fara
koyarwa a jami'ar bayero,sai faduwa ta zo dai dai
da zama domin a shekarar ta fara nata karatun a
nan inda ta karanta (biochemistry) suka tattara
suka bar tarauni zuwa gidajen malamai na nan
jami'ar.ZUCIYA D KWANJi

.7) Dai-dai

wannan lokacin Alh sulaiman karansa ya kai
tsaiko bayan doguwar gwagwarmaya wadda
kokawar tarar da buri ya haifa. Nasa mahaifin
karamin ma'aikacin gwamnati ne,bayan ya yaki
jahilci,sai dai mai jar zuciya ne,wanda ko za a
kwanta ba a ci ba ya laminta ya gabatar da
bukatar karatun sulaiman sai kuma ya yi dace
mahaifiyarsa ta zama mai tawakkali da goyon
baya,har ya kai ga hada digiri dinsa a (business
administration). Tun tasowar Alh mutum ne mai
manyan burika,sai dai yana da juriya da jarumtar
shanye wahalhalu wajen cika su. Bayan kammala
karatunsa,ya yi zaman fiye da shekaru biyu yana
neman aiki kasancewar bai sami wanda yake buri
ba,a karshe ma kawai sai ya koma makaranta ya

yi masters dinsa akan Economic,shekaru biyu ya kuma dawowa ya zauna jiran tsammani,sai ma aikin ya fi tsauri a wannan lokacin,saboda karatunsa ya yi zurfi, guraben da zai shiga sun yi karanci. Shekara daya da wannan karatun ne mahaifin wani abokinsa ya hada shi da wani kwara,wanda harkar kasuwanci ta kawo Nigeria, inda suka fara gwada shi kan shigo da wasu injina,kwazonsa da kwarewarsa akan wannan harkar ya sanya ba a shekara ba sai da suka bude wani katafaren kamfani suka dora shi akai. Labarin ya canja,Alh sulaiman ya fara cimma wasu daga cikin manyan burinkan da suke bunne a ransa,kamar mallakar manyan motoci,kama kudi,da kosassun gidajen da suka yi kama da aljannar duniya,daga nan kuma ya fara hangen kyakkyawar matar da zata dace da shi,don tun yana sakandire ya yiwa kansa alkawarin ba zai yi aure ba sai ya mallaki gida da mota,sannan ya auri kyakkyawar mace. ***************

****************** Mahaifin Abdullahi wani shahararren malamin ne, kuma alkali ne,mai suna Ustaz ukashatu Mohammad,mutum mai adalci da yawan dattako,yana da tarin 'ya'ya maza shidda, mata ashirin da uku,wadanda matansa hudu suka

haifa masa,duk da yanzu saura uku,don mahaifiyar Abdullahi Allah ya yi mata rasuwa shekaru biyu da suka wuce. Abdullahi ne dansa na goma,kuma auta cikin mazan nan,kuma a cikin mazan nan shi kadai ne bai gado gida ba,wato karanta shari'a ko koyarwa,sai ya karanci mass communication, amma sai ya buge da aiki a (ministry of rural & community development) ya kai matakin albashi na goma. Abdullahi mutum ne mai hikima da dankaren wayo,hangen nesansa na taimako kwarai a rayuwarsa wajen mallaka masa dukkan buri.jarumi ne kwarai wanda ba'a taba gane lagonsa,ba ya fushi a inda ya fahimci fushi nasa ba shi da ma'ana,sannan ba ya dariya a inda ba a san darajarta ba.8) Don haka kankantarsa ta tsaya a jikinsa ne kawai,amma zuciyarsa dattijiya ce.azancinsa kuma tsoho ne mai rankarfe. Matarsa ta fari sadiya,wadda ya aura shekarar da ya kammala karatu ko fara aiki bai yi ba,makociyarsu ce wadda soyayya mai zafi ta shiga tsakaninsu kafin auren,wadda kuma ita ta taimaka wajen amincewar mahaifinsa akan auren sadiyar da shi,kasancewar sadiya ba ta fito gidan tarbiyar da ta gamsar da malam ba,sai dai dole kunyar idon mahaifinta tasa ya amince wanda takanas

ya ishe malam din ya ce ya bai wa Abdullahi auren sadiya. Sai dai kash! Sadiya ba ta wa masa dan malam kunya ba,sai au enta da Abdullahi ya dinga haifar da matsaloli,matsakaita da kanana,wasu kishiyoyin juna,sadiya mafadaiciyar mace mai yawan kuncin zuciya da tsarguwa.Ga kuma Abdullahi miskilin mutum kuma mara daukar raini,sannan mara daukar korafi da muhimmanci, wadannan dalilin suka sa zuciyoyinsu suka canja daga masoya juna zuwa wani abu daban. Kullum su ke nan cikin hayaniya,sadiya ta dauki kafa ta yi yaji,shi kuma ya yi zuciya ya share ta har sai manya sun shigo. Da abin ya ishi malam sai kawai ya nemar wa Abdullahi wani auren. Hindatu ke nan matar abdullahi ta biyu, wadda ya aura ba bisa doron so ba,sai dai ta sami filin karamci a zuciyarsa saboda hakurinta da saukakawa kai buri.tana nuna masa wadatarta akan iyakar soyayyarsa da adalcin da ya yi mata duk da kuwa ba ya iya boye bambancin da zuciyarsa ta ke nunawa tsakaninta da sadiya wadda za a iya kira mowarsa duk kuwa da tambelenta. Shekarun hudu ke nan da auren fari,kuma shekarun biyu da auren Hindatu,amma cikinsu babu wadda tataba

ko batan wata, wannan ma sai ya bi layi cikin matsalolin da suka dami duniyar Abdullahi.

***************************************** Alh sulaiman abokin ne na kud-da -kud ga yayan Abdullahi,mai suna Abdulawahab.sun yi karatun sakandire tare,kuma daga nan abotarsu ta samo asali. Ba za a ce abdullahi ya yi masa farin sani ba, kasancewar lokacin da ya yi wayo sosai,sabgogin sun yiwa Alh sulaiman yawa,ma'ana ya yi wuyar gani,amma ya waye da Alh ya kawo wa yayan abdullahi lokacin da ya yi aure na biyu. Abdullahi na tare da yayan nasa yana sauraron hirarasu. Abdulwahab yana zolayar Alh da cewa. "Sulaiman burinka fa kamar ya wuce mallakar makudan kudin,gidaje da motocin hawa kafin ka ajiye iyali,me kake yiwa kanka kawa ne?" Alhaji na dariya ya ce. "Wallahi har yau na kasa samun matar da zata da ce dagida na,watanin baya na so auren wata balarabiya wani abokina ya dinga kwabata,wai tatike maza suke su tsere,dole na hakura tunda an ce mutum ba ya kin ta mutane". Abdul wahab ya ce. "Haka ne, amma ya kamata ka yi taka tsantsan a cikin sha'anin mata,sun fi kowacce kawa hatsari,musamman kyawawa don yawancin su

nagartasu ba ta kai masu karamincin kyau ba,sai ka zauna da matarka mai karancin kyau ka dinga sarafa abarka son ranka,amma awajen kyakkwayawr mace ka yi kadan,komai kudinka da mulkinka,wuyarta ta kalli kanta a madubi sai ta ji ta girme idonka,kuma ko yau kuka rabu zata sami wanda ya fi ka,don haka ba ka isa ka sa ba,balle ka hana". Kamar a sanyaye Alh sulaiman ya ce. "To,Allah ya zaba manaZUCIYA D KWANJI

9) Alh sulaiman

ya hadu da fatima ne ranar bikin kammala karatunta,gaba daya ya sakwarkwarce,don fatimata kusan zarce tanadin da yake wa kansa game da mace. Sunanta ya nuna masa daga inda ta fito,sai ta kwanar masa gidansauki,domin kawu malaminsa ne tun a sakandire,sannan ya koyar da shi a digiri dinsa na farko.sun shaku matuka suna ganin mutumcin juna kasancewar kawu mai son jarumin namiji mai hazaka da juriyar cimma burin abin da ya sa a gaba.To Allah ya horewa sulaiman wannan,mutum ne mai kaifin kwakwalwa,wanda duk abin da aka zuba mata sai ta kwashe,shi yasa yake ji da shi tun a sakandire. Kwana uku da ganinta ya wanke kafa ya tafi gidan prof.bayan ya nemi izininsa a waya.

Pro ya karbe shi cikin mutumci kafin ya shiga rudanin abin da ya zo masa da shi,wato neman auren fatima. "Ko akwai matsala ne?" Alh ya tambaya saboda ganin yadda kawu ya shiga damuwa. Prof ya sauke numfashi ya ce.
"Sulaiman fatima ta dade tana dauko min magana wallahi,manyan mutanen da nake jin kunya ba zan iya kirga maka wadanda suka zo da kokon bararsu gare ni na son auren fatima ba.Amma sai ta watsa mana kasa a ido ni da su,na rasa inda yarinyar nan tasa gaba,kowa ya zo ba ta so.A bayanta fa kanwarta ta biyu ake shirin aurarwa,amma ita ko a jikinta....maraicinya ke sa ni tausayamata,amma tabbas da ni na haife fatima da na tilasta mata aurenka". Wannan to gaciyar ba ta sa sulaiman ya dauke kafa ba,sai ya ci gaba da kawo gaisuwa da rokon iri har aka kai matakin da kawu ya ba shi damar bayyana kansa ga fatima.Amma kash! Sai aka yi rashi sa'a cikin masu son ta ba ta taba tsanar wani sama da Alh sulaiman ba, ba ta kaunarsa ko kadan kuma ba ta iya boyewa kowa ma ya sani.
Shekarunsu biyu a haka, fatima ta kammala service,ta kuma nemi izinin kawu na neman aiki.A nan ne kawu ya yi ta maza ya ce sam bai san

wannan zance ba, ya ma ba ta wata guda na ta fito da miji, idan ba haka ba sai dai ta ji taron dauran aure. Fatima ta dauke maganar kawu wasa,har ta bare watan ya share a wasa,sai rana tsaka ta ga taron jama'a a gidansu,labarin ya zo mata an daura aurenta da Alh sualiman. Tarihun auren ke nan,wanda labarin zamansa sam babu dadi,Alh sulaiman ya cimma burinsa na mallakar "KYALLI HUDU". Sai dai kash! Kyalli daya ya hana shi natsuwa,wato fatima,ta hana shi kwanciyar hankali sam. Ta kwakware dukkan farin cikin da sauran kyallin suka samar masa.Ga shi Allah ya jarrabe shi da masifar kaunarta,shi yasa ta ke dama garinta a sha yadda ta ke so ko da babu gasara balle sukari. Duk abin da fataima ta shimfida kpo ba ya so sai ta aiwatar,ga jarabar kasaita kamar 'yar sarkin santanbil,sai ya yi magana hamsin fatima ba ta tsinka daya ba,idan ma ba ta so ba, sai su kwashi kwanki ba su ga juna ba,don babu ruwanta da duk wani abu da ya shafe shi, cinsa ko shansa da kula da dawainiyarsa duk ta sallamawamasu yi masa hidima. Kamar yadda bai isa sanin wani abu game da shige da ficenta ba bu ruwanta da daukar damarsa,ko yana cikin gidan sai dai ya

hangi ficewarta da mota,ko kuma duk sanda ya shigo gida ya binciki masu gadi,"hajiya na ciki,ko ta fita?" Kai kansu ma'aikatan gidan hakan na bala'in bakanta masu rai,ballantana danginsa wadanda fatima ba ta dauke su a bakin komai ba,ko gidan suka zo kashi ma ya fi su daraja a idonta.Gaisuwa kadai ke hada su, babu duka babu zagi,amma babu ruwanta da mutum har ya karaci kwanakinsa ko wuninsa ya bar gidan. Mahaifiyarsa ce kawai ta ke samun arzikin kallon kirki,shi ma a wani yanayi na kamar dole don ita kanta mahaifiyar tasa tasan fatima ta tsane ta,kamar yadda ta tsane dantaZUCIYA D KWANJI .10) Duk wadannan munannan dabi'u na fatima ba su taba rage matsayinta a zuciyar Alh ba, da zata yi mugun bata masa rai,idan ya hangi murmushinta ko tsakainta da wani ne sai ya ji ta wanke masa zuciya.Don haka duk yadda mahaifinyarsa da sauran danginsa ke nuna masa illar fatima ba ya gani,idan ma ba a yi wasa ba sai reshe ya juye da mujiya,ma'ana ya tsani me kawo sukar,har dai kowa ya fahimci shi aka daina kawo masa sukar,illa addu'ar ganewa. Duk wata biyayya da mace ya kamata ta yiwa mijinta fatima ba ta santa ba a tsakaninta da Alh kuma

ta kan yi komai domin ta bata masa, wanda tana yin hakan ne domin ya ji zafi ya saki aurenta kamar yadda ta ke iya keta idonsa ta fada masa. "Ba a nemi amincewa ta ba kafin a hada mu rayuwa tare, saboda haka har abada kada ka saka ran zaka mallaki karamar kofa ko kamar ta allura daga kofofin zuciyata.Raina ba ya sonka, kuma ni mutum ce da ban iya boye kiyayya ba"m Bai taba daukar wani mataki akan fatima ba ko da na zare ido ne, sai rarrashi da lallabawa tare da yi mata manya manyan kyauta masu motsa zuciya.gwala gwale,kadarori, manya kudade ita da duk wanda ya rabeta,amma fatima kamar dutse,zata karba ta kalmashe,idan ta ga dama ko godiya ba zata yi masa ba. A haka suka yi rayuwar,sai su kwashi watanni ba su hada shimfida ba, wanda a nan ma tana kara tafiya da imaninsa ya ci gaba da kwadayin zaman har abada tare da ita,saboda baiwar da ta ke da ita na kasancewa daga cikin matan da ake kira sa'ida. Shekarun uku tare sannan ta sami ciki wanda ya bare a lokacin da yake shiga watanin hudu,cikin shekarun ukun da suka kuma biyu bayan shidda ke nan da aurensu,ta jera bari sau hudu,har waje ya fita da ita,amma lamarin ya ci

tura.wannan ya sa ta kara tsanarsa,musamman idan yana lallabata da cewa rabo ne ya kaddara aurensu,takan ce "Rabon wahala ba, tunda akalla ko dan tsako na kasa haifa". Bayan wannan aikin da aka yi mata kawai sai ta dinga munafintarsa tana karbar allurar hana daukar ciki,saboda yadda ta tsani mutuwarta haka ta tsani haihuwa da shi, saboda ta rayawa ranta haihuwarta zata tilasta mata zaman gidansa Shakaru da suka yi goma tare,bai zama wani sabon abu da zai hana a yanzka kaza ba, don babu abin da ya canja,fatima ba ta fasa nuna masa iyakarsa ba,shi kuma ko kwayar zarra bai rage sonta ba, duk da ta dalilinta ya sami hawan jini. Kai ko a murnar cikar su shekara goma da aure wani katoton gidan gonarsa ya mallaka mata wanda kudinsa ya kai miliyo ashirin. Kuma wannan ne ya tashi mahaifiyarsa a tsaye wajen farraka su, don ta hakikance Alh zai iya mallakawa fatima dukkan dukiyarta da ya mallaka,ko da kuwa yin hakan ba zai amfane shi da komai ba. Ta dinga ziyartar bokaye da malaman surkulle amma shiru babu labari,dole ta koma wa gaskiya,ta sa aka dinga yi mata rokon Allah ana neman idan akwai alkhairi ya shirya fatima idan babu ya farraka

auren. Sai da kura ta yi kamar ta lafa,ku san Alh bai taba mallakar fatima irin yadda ya mallake ta a wannan shekarar,kai kamar ma ita ce shekarar zumarsu,wadda bai dandana a farkon aurensu ba. Fatima kan yi hira da shi ba tare da bakar magana ba,sannan takan yi masa rakiya idan tafiya ta same shi, sannan uwa - uba ta daina gudunsa a shimfida duk lokacin da ya bukace ta. Allah mai yadda ya so, ranar wata alhamis da sasanyar la'asar ta shirya ta fice bikin kanwar wata kawarta. A lokacin ne wasu miyagun ma'aikatan gidan suka sami damar shiga dakin Alh ta hanyar amfani da (master key) suka kwashe wasu makudan kuadaden waje da ya shigo da su safiyar ranar. Ya dawo karfe biyar zai fita da kudin,amma sama ko kasa ya nemi kudin ya rasa,ya shafa a gidan babu fatima.Haba! Sai hankalinsa ya yi mugun tashi,ya tabbatar kudin nan daukarsu aka yi,ya hada dukkan ma'akatan gidan ya fara surfar su da masifa. A karshe ya tabbatar musu in dai ba su fito masa da kudinsa. Ba sai ya salwantar da rayuwarsu. Ya sallame su kaca kaca bayan ya sanya masu gadi sun garkame kofar gidan tunda sun tabbatar masa babu wanda ya fita bayan Hajiya,wadda ta tuka

mota da kanta. Bai ko iya halarta sallar magariba da isha'I ba,yana ta faman safa da marwa cikin yanayn tashin h [truncated by WhatsApp]11) Alh sannu da gida". Ya juyo ya dube ta cikin matsanancin bacin rai,cikin tsawa ya ce.

"Fatima daga ina kike?" Ta yi saurin juyowa ta dube shi cikin dukan zuciyar mamaki,bacin ran da ke fuskarsa ya sa ya kara baki a idonta. Ta ga kamar babu mutumin da ya kai shi muni a duniya,sai ta ga ma babu hujjar da zai mata wannan tsawar ko wannan gizagon,kawai sai ita ma ta taso masa cikin bala'I. "Ban sani ba,idan ka halicce ni ne sai ka dauki mataki a kaina".

Haba! Ta kara hada masa bacin rai, Hankalinsa ba ya tare da shi ya ce. "Au haka kika ce? To zaman uban wa kike yi a cikin gidan tunda ban isa na yi iko da ke ba?" Ita ma cikin tsawa ta ce masa. "Kai ne ka fi kowa sani,zaman kaddara nake ba zaman uban wani ba..... Ko ka manta ne ba so da kauna ya kawo ni gidan nan ba.balle ban wani ya dinga yi min wannan ihun". Jikin Alh ya dinga bari kamar mazari, gaba daya fatima ta sauya a idonsa da zuciyarsa,ya ga ma gaba daya ba ta da wani amfani a wajensa ya fara mata bala'I. "Ke bana son isakance da rashin tarbiyyar da kika saba kin ji! Matukar ba zaki zauna a

gidan nan kamar ko wace matar ba, to tun wuri ki san inda dare ya yi miki,don ba ki da wani amfani a wajena,kullum ki dinga ficewa kina bar wa ma'aikata gida kina janyo min asara.....ke dai ba ki da wani amfani wallahi". Ta tare shi cikin hawaye saboda tana da saukin kuka,ba domin nadama ba. "Ai ni ban taba daukar aurenka wani abin a zo a gani ba,balle na yi abin da matan aure suke..... Sai ka daina yaudarar kanka da zan yi wani abu da zai yiwa ranka dadi......." Kai tsaye ya amsa ta. "To shi ke nan,tafi gidanku na sake ki saki UKU, don kin san ni ma na mayar da soyayyarkitarihi don iyayenki bace min da gani!" Shi ke nan, da shigowar fatima da saki nata ba a fi mintina biyar ba,Alh ya haye sama ya barta nan tana kuka matsannanci, sakin ya girgizata matuka! Alh ya saketa a lokacin da ta daina sha'awar barin gidansa,ma'ana ta yarda karasa rayuwa da shi duk da ba ta jin kaunar sa cikin ranta. Ita ma ba ta jima a wajen ba ta fice,tunda dama ko mayafi ba ta sauke ba, makullin motar ma yana hannunta,sai gida wai an daki kare a ka kawu ya sami bakin labari, amma bai gaskata fatima ba,sai ya kira Alh a waya,wanda har wannan lokacin yana kulle a dakinsa cikin mugun

bacin rai. ". Da gaske ne ka yiwa matarka saki uku sulaiman? "Inji kawu. Ba tare da lissafin abin da zai tafi ya dawo ba,Alh ya ce. "Kwarai da gaske,ku zo ku kwashe kayanta,ba na kaunar duk wani abu da zai tuna min na rayu da ita,mts!" Ya kife wayar cikin bacin rai. Wannan ne ya kashe bakin tsanyar kawu dangane da fadan da ya tanadarwa fatima. Ba sai ya bincika ba yasan Alh ya gama ganin damarsa bai kuma dauke shi a bakin kamai ba tunda ya iya keta idonsa ya yi masa wannan cin fuskar. Kawu ya sauke ido akan fatima,idonsa cike da kwallah ya ce. "Tashi ki shiga gida fatima,Allah ya sa hakan ne alhairi gare ku gaba daya". Washegari ranar Alh ya fito tafiya sallar asuba ya tarar da jakar kudinsa a korido,ya dauka ya shigar falo sannan ya fice masallaci. Har aka idar da sallah cikin hawaye yake, sai da ya dawo gida ya dinga mai dalilin kuka kamar wanda aka yiwa albishir din ranar mutuwa.zuciya da kwanji

12) Ya tabbatar Allah ne ya jarrabe shi akan fatima,daukar kudin nan ba ya nufin komai sai rabuwarsa da fatima,wadda a zahiri da badini ta fi karfin wadannan kudin a wajensa. Lamarin kamar alamara kamar mafarki,ya rabu da

fatima,rabuwa mai kama da alamara da ya ya zai karbi wannan kaddarar?. Kawu mutum ne mai zuciya kwarai,da sanyin safiya ya turo a tattare masa kayan fatima,Alh ya yi tsalle ya ce bai san wannan zancen ba,har sai da ta kai sun kira kawu a waya sun sanar da shi. A fusace ya kira wayar Alh ya ce masa. "Ban gane abin da kake nufi ba?" Kawai sai Alh ya sa kuka yana cewa "Kawu ayi min rai,a binciki malamai ko akwai gyara cikin lamarinmu, wallahi kawu cikin mayen bacin rai na yi sakin nan, sam hankalina ba ya tare da ni......" A kufule kawu ya amsa. "Shi ke nan,yanzu ka bar su su debi kayan in yaso idan malam sun budo maka kofar halaccin ci gaba da zamanku tare sai mu dawo da kayan". Bai jira cewar Alh ba ya kashe wayar dole Alh ya barsu suka kwashe kayan fatima tas, yayin da kamar sun bude kofar kukansa da bakin cikin sa. Rayuwa ta yi kunci gare shi matuka. A wajen fatima ma haka lamarin yake,ranar da aka yi sakin ba ta iya runtsa bacci ba. A zatonta zafinb kalmar da ya hada mata da sakin ce ta ke damunta wato. "Don ki san nima naE mayar da soyayyarki mafarki..... Don iyayenki bace min da gani". A hankali sai ta gane ba kalamar ce ta ke

son ta tashi hankalita ba,akwai batutuwa da dama, kuma na shekaru da yawa.yadda ta jima tana taka rawar da ta ke so a gida da rayuwar Alh shi kuma yana saka mata da tarin kauna da farantawa.....me yasa ya dawo daga rakiyarta yanzu? Kuma zata kuma samun namiji mai nuna mata kauna kamar Alh kuwa? Wadannan lissafe lisafe ba su barta haka ba sai da suka yi tasiri manna mata kaunar Alh,ta dinga yarda wakanta lallai ta tafka asarar masoyi. Ta rasa sukuni kwata kwata,hakki ne kawai yake dawainiya da fatima,hakki irin na mai laifi cikin ma'auratan da suka sami kansu tsakiyar kaifin almakashin saki uku! Duk da haka ba za a ce fatima ta kai Alh damuwa ba, tunda ba ta yi wani yunkurin ba, bayan na fatan ina ma jiya ta dawo yau, ta mayar wa da alh raddin soyayyarsa? Ba ta yarda ta yi zurfi cikin kaunar Alh ba sai da ya nemeta da tayin yadda za su mayar da aurensu tare da bayyana mata fatawar da ta bayyana cewa,saki uku lokaci daya sakin bidi'a ne,kuma a matsayin saki daya yake. Sai kawai ta bayar da kai bori ya hau,ta kuma iya jure tunkarar kawu da maganar,Allah ya sa kawu ba mai karamin sani ba ne, sai ya dubeta da kyau cikin nazarin ta

sosai, sannan ya ce. "To ni ban gamsu ba,ba kuma na karyata fatawar da ya kawo ba ne. Sam! Ni hankalina ya fi kwanciya ga wadda ta haramta aurenku har sai kin auri wani namijin kin tare da shi. Wadda wannan fatawar jamhurun malamai suka tafi akai kar ki kara kawo min irin wannan maganar,ban son rudu. Dole ta karkade zani ta mike cikin hawaye. Daga nan ne kuma cira kafa ita da Alh ta bin hanyar duk suka sa zata mayar musu da juna,kawu na dago logarsu saboda farin sanin da ya yiwa fatima da irin mijin da ayke zaton zata zabawa kanta. Sau hudu tana kawo masa samari zata aura,idan kawu ya saka su a kwana da tambayoyi sai ya dago su. Don haka ya tattara dukkan lurarsa akan fatima,ya alkwarta wa ransa sai iyakar inda karfinsa ya kare..Zuciya D Kwanji

13) Abdullahi ya hadu da Alh ne a wani tsadadden asibiti lokacin da ya je dubo wani abokinsa da aka yiwa aikin kaba,shi kuma Alh ya je bisa larurarsa ta hawan jini,wadda ta matsa masa yanzu. Tun da Alh ya ga Abdullahi ya dora dukkan burinsa a kansa,don ya tabbatar in dai Abdullahi ne kawu ba zai taba dago yawarsu ba tunda bai rasa komai da ake bukata kafin a ba wa mutum aure ba. Ya dinga ribatar Abdullahi

har ya samu suka kebe,sannan ya koro masa bayani. "Dan halak ke nan, shekaran jiyan nan ka fado min a rai,dama cikin satin nan nake son na neme ka". Cikin fuskar rashin fahimta Abdullahi ya ce," Allah sarki,ina fatan kalau?" Fuskar Alh na bayyana jimami ya rangwada kai ya ce. "To lafiyar mahaukaci ba,wani aikin lada da ceton rai nake son baka,don a duniya ba ni da mai yi min sai kai". Kallonsa kawai Abdullahi yake cikin rashin fahimta,har sai da ya dure sanan ya kuma dorawa. "Allah ne mai saka soyayya a zukatan bayinsa Abdul,ya jarrabe ni da son mace daya a duniya,wato matata. Wani tsautsayi yasa na yi mata saki uku. To yanzu duniyar ta yi min kunci,na gane ba zan iya rayuwa ba tare da ita ba..... Shi ne nake rokon ka tainaka ka halarta min ita". Kallon Alh kawai Abdullahi yake yana sauraron wannan rainin hankali da na wayo. Jima kafin ya shawo kan fushin zuciyarsa sannan ya yi magana mai ma'ana. "Me yasa sai ni zan yi maka wannan aikin?" Yana rufe baki Alh ya amsa. " Saboda zumuncin da ke tsakaninmu, nasan ba zaka so akan wannan lafiyata ta salwanta ba.... Kawunta ne ya matsa matukar bai ga mutum mai kamata irin ta gidanku ba,ba zai

bayar da aurenta ba, don ya sanya mana ido.....
Ni kuma wallahi ba zan iya hakura da ita ba....
Sai inda karfina ya kare wallahi...." Abdullahi ya tare shi da cewa. "Ba ka ganin hakan zai zubar da martabar gidanmu......?" Alh ma ya tare shi kamar zai yi kuka. "Ka fansar Abdullahi,ka ceci raina.wallahi na yi maka alkwarin biyanka makudan kudade...... Zan daga darajarka a garin nan sai ka shiga sahun attajirai". Abdullahi ya jima yana tunani,sannan ya dube shi da kyau ya ce. "Ka fa san halin mahaifa,babu yadda za'a yi na kawo matar da ta girme min da zummar aure bai nemi ba'asi ba. Na kuma san duk wahala dole matarka ta girme ni". Cikin doki Alh ya ce. "Au ba ka santa ba?" Kallonsa kawai abdullahi ya yi cike da takaici. To ta wacce hanyar zai san matar wani? Musamman alh kawai don yana abokin wansa? Sai ya girgiza kai kawai,Alh ya ce. "Shekarunta talatin da biyu,kuma da yake tana da kyan jiki zaka zaci ba ta fi shekaru ashirin da biyar ba".Zuciya d kwanji
.14) Abdullahi ya kara jan fasali sannan ya ce. "Da yardarta a ciki?" Alh ya yi saurin gyada kai. "Eh,idan ma ka amince sai na gabatar maka da ita kafin ku fara magana". Kai tsaye Abdullahi ya

amsa. "Ti na amince,Allah ya tabbatar maka da ita kafin ku fara magana". Kai tsaye Abdullahi ya amsa. "To na amince,Allah ya tabbatar mana da alhairi". Farin cikin Alh ya tsananta,kawai sai ya rungume Abdullahi yana godiya. A nan suka shirya haduwa da yammaci a gidan namun daji,a haduwar tsu kuma suk jaddada kudirinsu,sannan suka yi musanyar lambar waya tare da shirya a washe garin ranar abdullahi zai fara zuwa tadi.

**************** *************** Washe gari da yamma bayan sallar la'asar,fatima na kwance kan kujera 3 sitter,a kasalce ta ke kwarai,kasal irin wadda ke tasowa daga zuciya sakamakon bacin rai da damuwa. Ta sanar da mutum gidan cewa, tana da bako kowa murna yake yana dokin ganin bakon cikin zakuwa,wanda ta tabbatar da biyu suke yi... Kowa sai hidimar tarensa yake daga kan masu aiki akan abincinsa,har jama'ar gidan masu murna da doki. Wannan ya sa fargabarta ta kara tsananta..... Tasan kawu sarai akwai dora ido. Dazun da safe Abdullahi ya yi mata waya ya ce, karfe uku zai zo,amma ga shi hudu da rabi abu labarinsa,sai bacin ranta ya karu,ta kuma kara jin tsanar abdullahi cikin ranta.Ta tsani mutumin da ba ya daukarta da muhimmanci,ko

kuma ba ya girmamata. Ta lura da abdullahi mugun dan tsaurin ido ne...... Ya iya dizga mutane. To idan ma halinsa ne dizga mutane ai tana jin ta fi karfin hakan,don ba ta rasa duk wani abu da ke janye so da biyayya ba,ko ba domin Allah ba. Tana da kyau,kuma tana da kudi,sannan ta iya takunta. Da damuwar ta isheta sai ta janyo waya ta hau facebuk domin debe kewa,tsawon mintina goma,sai ga safiya kanwar momi matar kawuta shigo da karadinta "Anti wannan yayan namu zai tilasta ni kuma kwannan gidan don ba zan wuce ba sai na ganshi,don Allah ki yi masa waya ya karaso mu gaisa. Fatima ta dago ta dube ta, sai ta rasa ansar da zata bata,akan me zata yi masa waya,kuma ta ce masa me? Sai kawai ta yi shagare tana kallonta cikin zancen zuci,safiyya ta bude baki tana kallonta ta ce. "Anty..... Wannan mutuwar ido biyun fa? Duk yayan ne da wannan aikin?" Fatima ta yi murmushin karfin halin da ya yi kama da na shauki, sannan ta juya baya ba tare da ta tanka ba, safiyya ta mike ta ita tana tuntsura mata dariya. Sai shidda saura abdullahi ya iso,ya yi kiran wayarta tana ta faman kallon wayar sai da ta katse ya sake kira, sannan ta daga a kule,kum

ba ta tanka ba. Muryarsa a sake ya ce. "Fatima na iso". Haushin gatsa sunanta da ya yi kai tsayeya sa ta taso masa da bala'I. "To me zan yi maka? Kane nawa karfe nawa ka ce min zaka zo?" Ya yi sjiru,sannan ya nisa a zafafe ya ce. "Ki yi hakuri,amma don Allah ki dinga yi min uzuri,bana son masifa wallahi". Sai ta saki baki cikin al'ajabi,ta ma rasa abin da zata ce masa,koda yake ko tana da abin fadar bai ba ta damar fadar ba, tunda ya kashe wayar.......

Wannan wanne irin dan zafin kai Alh ya hadata da shi? Duk mazan da ya kawo mata a bayan masu ladabi ne,amma wannan yana jin kansa shi wata tsiyar ne.

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

zuciya d kwanji

15) Ta fi mintina ashirin tana faman sacewa tare da tunanin turbar da zata bi da wannan dan hayaniya har ta kai ga zargin kanta.Ta gama babu wani dalilin da zai sa ta dinga damuwa da zafin kansa,ya karaci jaridarsa ya gama. Ta sa baki ta yi kiran safiyya,sai gata a guje,tana zuwa ta ce. "Ya zo ko Anti?" Ta yi murmushi,tukunana ta ce. "Ya zo, sai ki shigo da shi,don na ga

alamar kin fi ni dokin ganinsa". Safiyya na dariya,ta ce. "A'a bazan fi ki ba anti,ke da zazzabi ya kusa tsegumi kawai ke dawainiya da ni in ga dai dan talikin nan da ya rikita mana ke". Fatima ta hadiye takaicinta,ta ce. "Nasan ba zan ba mara danki kunya ba shigo da shi sai ki kare masa kallo". Safiyya ta fice fatima na binta da kallo cikin kunar rai,haka kawai ta ji sam ba ta kaunar ganinsa. Tana jiyo jama'ar gidan na ta kara-kaina a kansa.Da akwai alamun sun yaba, can sai ga safiyya da sauran 'yanmatan gidan sun shigo,suna mata kaudi. "A'a Anti kin yo wawan kamun ya ya muka ganki haka? Don Allah tashi ki canja tsari,don ya gane gidan ya tarar". Ta yunkura ta tashi zaune ta rafta tagumi hannu biyu tana sauraron cagwadar da suke mata. "Na rantse Anti yanzu kika yi mijin da ya dace da ke, ko babu kudi akwai kyau da iya taku......"

"Sannan ga fara'a da iya shirya zance kalma bayan kalma...." Irin kalaman yabon Abdullahi da suke ta jero mata ke nan, wadanda suke faranta mata,sannan suka bakanta mata,karbuwar da ya yi a gurinsu ne ya faranta mata.tana kuma jin haushin yabon da suke masa don bai cancanci yabon na ko dayua,sai dai babu damar ta

bayyana. Haka suka yi ta ribatarta sai da ta canja shiga,ta yi kyau tamkar ranar walimar aurenta. Ta same shi a falon momi durkushe a gabanta,kamar zai kwanta mata saboda ladabi. Momi na ganinta ta hau zolayarta. "Kin gaji da jira kika biyo bayansa ko?" Ta yi murmushi kasaita,ba ta tanka ba ta nemi kujera ta zauna tana kallon ikon Allah. Momi ba ta jira cewarsa ba,ta juya ga Abdullahi ta ce. "Ina fatan ka shirya da kyau,wannan yarinyar shan kamshinta ya yi yawa". Ya kara kan - kan da kai,muryarsa a ladabce, ya ce. "Na sani momi,a taya mu da addu'a". Cikin fara momi ta ce. "Idan Allah ya so,kar ka ji na ce haka,fatima na da saukin kai ga wanda ya iyawa dabi'arta da tarbiyyarta,ina tsammatar muku zaman lafiya da saukin fahimtar juna,domin dukkanku kun fito daga gidan tarbiya da sanin ya kamata. "Mun gode". Kalmar da Abdullahi yake ta maimaitawa ke nan,ya yin da fatima ta yi shagare tana kallon momi zuciyarta cike da tambayoyi.A ina momi tasan Abdullahi,kuma dan gidan waye? "Don Allah ka rike amana,ka ga marainiya ce, nasan kawunta ma nasihar da zai yi maka ke nan. To kafin ka ganshi ma ni na fara yi maka. Ka rike ta amana

don Allah ku zama masu hakuri hat ku fahimci juna". Abin da momi ke ta jaddada masa ke nan, idon fatima a kanta,yayin da kunnuwanta ke sauraron Abdullahi cikin ladabi yana amsar amanar yana kuma tabbatar mata da yarda Allah ba zasu yi nadamar ba shi aurenta ba. Har cikin ran fatima ta yarda yana kirari yana dabawa kansa wuka nekawai,don bai kamata ya furta ko kalma daya a cikin maganar momi ba matukar ba zai iya toshe kunnensa daga saurare ba.
Tsawomn wasu mintuna,sannan momi ta yi musu iznin su tashi.Abdullahi ya fara mikewa,sanna fatima ta bishi a baya har zuwa katafaren falon da aka sauke shi. Suna shiga falon ya soke hannu a aljihu ya kuma canja fuska,sannan ya juya mata baya. A gajiye kuma fuskarta a bace ta nemi kujera ta zauna tana faman harara a duhu,tunda bai san tana yi ba. Suka kwashe fiye da mintina goma a haka,sai da ya jiyo maganganun su safiyya a kusa da falon sannan ya juyo ya dube ta,duba irin wanda duk kwakwar mutum ba zai iya karanta abin da zuciyarsa ta boye game da ita ba.Zuciya d kwanji
.16) Sai ta kara bata rai,shi kuma bai damu ba, ya tako har zuwa gabanta ya sunkuya

hannayensa dafe da ahnnun kujerar da ta ke zaune,yadda ta ke jin hucin numfashin sa sosai,ya dubi tsakiyar idonta da kyau, sannan ya fara magana kasa kasa. "Duk wata halitta mai motsi a cikin gidan nan tana da kirki matuka! Ba kamar ke ba ba abin ya daure min kai sosai". A tunzure ta taure shi ta mike,ta dinga nun shi da yatsa,amma ta kasa cewa komai,bakinta sai motsin yake,ya rungume hannu kawai yana kallonta,ko kadan fuskarsa ba ta sauya ba, abin da ma ya kara kular da ita ke nan. Da kyar ta hadiye ta sami abin cewa. "Oh,abin da ya kawo ka ke nan?" Ya yi saurin gyara kai tare da mokade lebe, ya ce. "Eh,tunda da fuska biyu na zo,idan muna cikin mutane nake masoyinki,a irin wannan filin ban gane sunan da zan kira kaina ba, kuma ban san matsayin da ya kamata na baki ba. Kuma ban san matsayin da ya kamata na baki ba. Ga shi kuma bana son barin lokutana su tafi a banza,shi yasa nan fada miki abin da yake hakkun.Ba laifi ba ne don ne ce,ba ki da kirki,ko kina da shi?" Zuciyar fatima ta dinga bugawa saboda tsabar bakin ciki,ita ce dazu har da girin gidinshin jin haushin ya gats sunanta,ashe rabin lamab ne cikin rashin mutumcinsa? Ta fara tafiya

da baya a hankali har ta riski wata kujerar ta zauna,sannan ta dube shi cikin yanayi barcin rai,ta ce. "Haka ne, rashin kirkina ya zarce inda kake tsammatar masa,musamman a muhallin da na tabbatar yin kirkin da barinsa ba zai amfanar min komai ba, wato muhalli irin naka,me yasa zan maka kirki? Fada min dalilin don Allah". Tana rufe baki ya amsa. "Ni ma dan ba ni da dali...." Ta yi saurin dakatar da shi da hannu hade da masifa. "Ka ga bana son rashin arziki don Allah,kirkin idan a gidanku ake rabawa gobe ka yo min guzirinsa". Ya jima yana kallonta ba tare da fuskarsa ta bayyana bacin ran da ta ke ciki ba. Sannan ya murza hannu yana fuskantarta. "Ki dinga yiwa harshenki linzami ya zama mai furta alkhairi kinji? Ko don ki ci gaba da kasancewa cikin shahararun mata a duniya masu sanyin hali da sanyi kyau,mace na da kima kwarai bai kamata ta dinga salwantar da ita wajen yin hayaniya da ihu kamar na karnuka a gaban namiji ba, mata masu irin wannan halin ina musu kallon ballagazaye wallahi....." Wannan karon zuciyarta ba ta buga ba, mamakinta da tsaurin idon Abdullahi kuma ya yi. Sauki, sai dai ya fara sa wa tana raina kanta..... Ashe tana da sauran

gibin da ba ta cike ba? Ta rasa da lafazin da zata kalubalance shi ko ta tsawatar masa, tunda nasa harshen ya fi nata kaifi..... Idan ta fadi daya sai ya fada mata goma,sai ta tsaya kawai tana kallonsa tana huci,ya bude baki zai yi magana ta dakatar da shi.A sanyaye ta ce. "Ka ga ya isa kar ka sa min ciwon kai,ban son dogon surutu". Ya fara murmushi har kumatunsa suka loba,bai tanka ba sai ya dauko magazine table ya dire a gabanta. Sannan ya zauna suna fuskartar juna, amma idanunwansu na wani muhallin daban, ita ta kurawa talabijin ido,shi kuma yana kallon tile din da ke shimfide a falon. Suka kwashe sama da mintuna goma a haka sai da ta ga ya fara hararar agogo,sannan ta harari kayan kwalam din da aka shirya masa a tsakiya dakin. A kuntace ta ce masa. "Idan fa ka tafi ba ka dan taba wani abu daga cikin kayan abincin nan da suka jera maka ba zaka bar zuciyarsu da zargi". Shi ma ya sha kamshi,sannan ya tanka. "Haka ne,sai ki dan bani wani abu na ci idan kina gudun zargin". Haba! A hanzarce ta juyo tana masa wani wulakanctaccen kallo,aka yi sa'a shi ma yana dubanta,sai ya yi saurin dafe kai,ya ce. "Ash!" Sannan ya kuma dubanta yana daga mata

hannu,ya ce. "Yi hakuri na manta sunan boyi nake amsawa a wajenki,sai dai kar ki manta Alh ya ce mu yi acting sosai,na tabbatar kuma zamu fa di assigment idan wani ya shigo ya tarar da ni ina be bude a kwanuka ke kuma kina kallon talabinjin"

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

17) Ba ta kop dube shi ba,ta zabga tsaki,ta je ta zuba masa gasassun 'yan shila wanda kamshinsu ya gauraye falon. Ta kwashe lemunkan da suka zube wanda ya fara hucewa,ta mayar fridge ta dauko masu sanyi duk ta dire kan center table.A cunkunshe ta ce. "Ga shi nan". Ya hadiye dariyar da ke damunsa,ya ce. "Don me ba zaki kawo min nan ba? Ta zabga masa harara kamar idonta zai fado,ta ce. "Don ni ba baiwarka ba ce,idan ma ba zaka ci ba,ka bar shi". Ta dauki lemon kwakwa ta wuce kujera ta harde ta fara kurba,shi ma sai ya mike ya je ya dauki lemon kwakwar.yana tsaye ya dire gwangwanin sannan ya zauna ya fara cin naman cikin gwaninta da kwarewa yana amfanin da wuka da fork. Ta saci kallonsa ta yi tsaki cikin ranta ta ce, duk yadda

aka yi ya lakanci barin matansa da gabza shi ya zagaya restaurant ya barje. Duk sai haushinsa ya kara kumeta. Yana gamawa ya koma muhallin da ya tashi, wato na kusa da ita.Bai dubeta ba,sai ya dubi a gogonsa ya ce. "To ni zan wuce". Tq yi tsaki kawai ba ta tanka ba. Ya dube ta da kyau,fuskarsa na rinewa da bacin rai, kawai shi ma sai ya zabga tsaki. Ta dago da sauri ta dube shi. Ya murza hannu rai a bace,idonsa cikin nata ya ce. "Ji nan malama, neman kudi fa ba bariki ba ne.mene ne za ki dinga yi min tsaki ke ba tsaka ba,wai ba ku kuka gayyato ni ba,ni ban miki ba ku karbi kudinku in san na yi,ina fatan ya sanar da ke ba daudar talauci ya kankare min ya dauko ni ba..... Uzurinsa kawai na kalla na karbi tayin". Maganunsa suka ci gaba da kona mata zuciya.amma ta rasa kalaman raddi, sallamarsa zata yi ya yi gaba su koma fafutukar neman wani tunda shi tsaurin idonsa ya yi yawa,ko kuma shiru zata yi masa ya ci garin? Dole shirun ta yi masa tunda shi ma yana da tasa darajar,idan an rasa shi da wuya asami kamar shi,sai ta ta buge da kallon talabijin shi kuma ya. Mike cikin sassauta murya ya ce. "Kamar yadda na fada miki dazun,ba na son fada da masifa, kuma bana

son tsaki,ke ni gaba daya ma bana son rainin hankali da na wayo, idan kinga in daina zuwa gidanku ne kawai sai na dauke kafata ni ma lokaci na ya huta wucewa a wofi,in yaso sai manya su yi maganar auren kawai". Ya yi shiru yana kallonta. Ta dade cikin jan numfashi tana daure fuska,sannan cikin huci ta ce. "Shi ke nan zan kiyaye, ni ma bana son yawan magana,kuma idan ka zo ka dinga zama a muhallinka daban ina zama a nawa....ko daya bana son wannan zaman kunatar ba na son wata mu'amala ta kirki ta shiga tsakaninmu

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

18). Sannan kar ka dinga kiran wayata a cikin abin da bai zama dole ba". Ya fara tafiya,yana cewa cikin basarwa. "Zan kiyaye". Ta janyo jakarta don ta fanshe muntukus din da ya yi mata,cikin dakewa ta ce. "A'a tsaya ka karbi kudin zance mana". Ya tsaya cak ba tare da ya juyo ba, sai da ya hadiye dariyar da ta kama shi tsab,sannan ya juyo cikin,mazewa ya ce. "To na gode,na manta ma in gaya miki za'a yi bikin wani abokina sati mai zuwa ki ba ni kudin anko,shadda

ce 'yar dubu bakwai da kudin dinki dubu uku". Sai ta rasa abin da zata ce masa,kuma don kar ta bayar da kanta sai ta zaro dubu biyar ta mika masa tana cewa. "Aka ce kyauta tukwacin so ko? To tsakaninmu ba haka ba ne,na baka kudin zance ne da ya zama al'ada kuma don in nuna maka ni ce fa mai umarni da hani,kar ka je bikin...." Ya yi saurin tare ta da cewa. "To in haka ne kin gaza,tunda dubu goma ta fi karfinki,saboda haka kar wani lokacin ki ga rashin biyayya ta idan kika yi umarni na ki karba". Ya karbi dubu biyar din ya zira a aljihu ya juya zai fita,ba tare da ya bata damara magana ba. Dole ta mike ta biyo shi da sauri har tana hadawa da gudu ta cimmasa suka fito tare a salon tayi masa rakiya. Ya dinga sallama da yaran gidan yana raba musu kudi,ya ba su sama da dubu ashirin,sannan suka jera har wajen motarsa da fatima suna 'yar hirar ganin idon mutane,wanda yarfe kawai suke wa juna. Ta ce masa cikin gatsali. "Ka fa yi kokari,kamar ka yi abin a zo a gani". Shi ma cikin gatsali ya ansa mata "Kin san ai ba shi din na yi ba, saboda haka bai kamata aji a bakinki ba,ko kuwa kuna son kalato maganar da kika ce ba kya so? Ta ce,"Rashin so na da ita

ba zai hana in yi sharhi akan abin da na gani a baude ba....." Shi ma ya ansa. "Ba ki ba mara danki kunya ba, don dama na yi miki kallon rashin alkibla". Yana shirin tashin motarsa ke nan,ita kuma ya barta da tabo a zuciya. Dai dai lokacin da kawu ya shigo,sai ta buge da ce masa. "To mara mutunci,ga kawu nan sai ka tsaya ku gaisa". Ba ta jira cewarsa ba ta juya ta yi tafiyarta, amma ta labe tana hangensu da kawi,yadda Abdullahi ya zube kasa yana gaishe da kawu sai ka rantse dan limanin garin ne. Tana kallo kawu ya dago shi ya dan rungume kafadarsa yana cewa. "Abdullahi ko? A ladabce Abdullahi ya gyada kai cikin bayyana jin dadi,kawu ya ce. "Da kyau! Yanzu uwargidan ta yi min maganarka a waya.don kai na saki sabgogina na taho. Ka ba ni aron lokacin ka mana zuwa bayan magariba". Abdullahi ya kara kan kan da kai ya ce "Babu komai". Yana rike da kafadar abdullahi suka shiga gidan.

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

19) Bayana sallar isha'I kawu ya gana da Abdullahi, babu wani dogon bincike don ya yiwa

mahaifin Abdullahi farin sani,ba tare da wani shakku ba ya ce masa. "Na ba ka auren fatima tun daga yau, ka turo waliyanka da sadaki su shaida,ina fatan zaka rike amanarta,musammam saboda maraicinta..... Sannan ina yi maka nasiha kar ka bari soyayyar fatima ta runtse maka ido ka barta ta kangare maka kamar yadda suka yi da mijinta na farko..... Ya canja mata tarbiyya gaba daya kuma yanzu ya zo yana son jefa su masifar zaman haram. Tun daga nan zuciyar Abdullahi ta fara bugawa,ya kasa rufe baki yana kallon kawuhar ya dure maganarsa,sannan ya dora cikin bayyana murna. "Fatima ta zama matata kawu? Da me zan bayyana maka godiyata? A nutse kawu ya ce. "Ba godiyar na fi bukata ba, amanar na fi kaunar ka rike,kuma ina horonka da hakuri a cikin sha'aninta,tana da murdadden hali,amma tana da sauki kai idan an fahimce ta,saboda haka mu'amala da ita na bukatar hankali da azanci,kar ka ba ni kunya don Allah,saboda ko kadan ba na son damuwar fatima,yadda ka ji ina jaddada maka amanar nan tata,haka mahaifinta ya yi min satin da zai rasu,kamar dama yasan rasuwar zai yi, shi yasa kullum nake addu'ar Allah kar ya jarrabe ni a cikin lamarinta,kai ma ina horonka da

wannan addu'ar don ba zam rufeka ba. Nasa fatima kyakkywa ce matuka,wadda sai jarumin namiji zai iya tsallake shu'umancinta,ko ba ka san kyakkyawan mace na da hatsari ba?" A nutse Abdullahi ke gyada kai. "Na sani kawu,na sani. Duk na gane karatun da kake min,insha'allahu zan yi bita. Karfe goma da rabi na washe garin ranar da dare,yana gurfane a gaban mahaifinsa wanda ya nemi izinin gani tun safitar ranar,shi ne ya ba shi wannan lokacin saboda yawan jama'a. "Ina fatan babu matsala Abu Turab".(Alkunyarsa ke nan) Abdullahi ya kara rusunawa ya ce. "Allah gafarta malam babu matsala". Sai kuma ya yi shiru ya shiga sosa kai. Uban ya gama nazarinsa tsab,sai kawai ya zuba masa ido, suka dauki wani lokacin a haka,sannan malama ya nuna masa agogo ya ce. "Ba ka lura da dare ne? Ga lokaci na tafiya a matsayinka na mai iyali,ba dai dai ba ne ka je kana buga musu kofa". Abdullahi ya kara lankwashe kafa,kansa a sunkuye ya fara magana. "Allah gafarta malam.wata kyauta aka yi min,shi ne na zo in sanar da kai". Kallonsa kawai malam yake ba tare da ya tanka ba,har ya dora. "Wani bawan Allah ne ya kirani,ya ce ya aure min 'yarsa". Sai malam ya kara dubansa cikin tattare

ido ya ce. "Saboda ya tsammaci ba ka da mata?" Abdullahi ya girgiza kai a sunkuye. Mala ya ci gaba da cewa. "Uhum bude baki ka bani labari,kai ka fara nuna sha'awarka akan yarinyar ko kuma sai da ya baka ita sannan ka ji a ranka dama kana da bukatar kara aure a irin wannan lokacin?" Abdullahi ya girgiza kai, amma ya kasa amsawa da fatar bakinsa,har malam ya gaji ya dora. "Wane ne wannan mutumin,kuma me ye dangantakarka da shi?" Numfashin Abdullahi ya kai gwauro da mari,sannan ya kokarta ya amsa. "Prof ne a nan jami'ar bayero,yana karantar da tattali sunansa,prof,alkasim Najib,kuma ba ni da wata dangantaka da shi kawai na je gidan ne shi ne ya yi kirana ya ce ya bani auren'yarsa" Malam ya ci gaba da kura masa ido fuska a bace,ya ce. "Me ya kai ka gidan?" Abdullahi ya muskuta,amma ya kasa magana. Can malam ya kara gyara zama ya dube shi da kyau,ya ce. "Abu turab saurare ni da kyau,ina da bukatar amsar dukkan tambayar da na yi maka saboda kar in yanke maka hukunci bisa rashin adalci,ka gane ko? Kai ka kai kanka gidan prof bisa nuna kana son 'yarsa?" Kan abdullahi a sunkuye ya gyada kai, ba tare da fuskar malam ta canja ba ya ce.

"Yanzu Abu Turab kana matsayin almajiri zaka kai kanka gidan 'yan boko neman aure? Tafiyar ku zata zo daya Abu Turab? Anya? Tarangahumarka fa ta fara isa ta,duk shekarunka nawa da zaka hadawa kanka wannan zafin? Mata uku a lokacin guda,biyu ma ya ya ka iya da su? Abdullahi ya kara kan kan da kai ya fara bayar da hakuri, malam ya tare shi a fusace. "Wai don me zaka ba ni hakuri? Bude baki zaka yi mu tattauna,ina son sanin alkiblarka akab wannan aure auren.Aure uku cikin shekara hudu idan na ga kana da hujja m [truncated by WhatsApp]

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

.20) Me kake tunani game da mata da kake son cusa kanka cikin lamarinsu?" Kai tsaye kuma a nutse Abdullahi ya amsa. "Neman ilimi nake a cikin lamarinsa,don ina so dacewa da alkhairinsu,kuma ina neman tsarin ubangiji daga dukkan sharrinsu. Ban taba mafarkin zalunci a gar su ba,don haka nake neman toshe duk wata kofa da zan iya zaluntar da su ko da bisa kuskure,idan ka tuna,aurena na farko zabin kai na ne,amma ban yi dace tana da tarbiyya ba. Na biyu kuma ku kuka zaba min malam,amma Allah

ya sani bana kawar auren mace irinta,don haka har yau a cikin rudu nake. Don haka na nemi wannan auren saboda ta dace da irin matar da nake wa kaina fata,sannan 'yar mutanen kirki ce.ina hasashen zata dinke duk wata baraka a cikin sakokin zuciyata". "Me ka tanadar wa adalci?" Tambayar da malam ya yi masa ke nan bayan ya dire,shi ma ya kuma amsawa a takaice. "Niyya da kyakkyawan fata". Malam ya jima cikin nazari cikin kada kai, sannan ya nisa ya ce. "Abu Turab ina maka fatan aikinka ya yi dai dai da hikimar zancenka,amma ka sani bayan wannan zan bibiyi matar da aka ba ka don sanin irin gidan da ta fito. Idan na ga zaka iya tafiya a turban daya zan bar maku aurenku,sharudana a nan su ne. Kar na kuma jin ka da neam aure nan kusa, sannan duk wani hukunci da zaka yanke a gidanka ya zamana da sanina kafin ka yanke shi,kar na kara jin ka tura 'yar wani gidansu. Ina fatan ka. Fahimce ni Abdullahi ya gyada kai yana mai godiya sannan mahaifinsa ya ce. "Allah ya yi maka albarka,Allah ya jagoranceka, ya ba ka ikon yin adalci a tsakanin matanka". Cike da farin ciki Abdullahi ya dinga amsawa"amin amin. Fiye da sati daya abdullahi bai kuma waiwayar gidan su

fatima ba,gaba daya a tsorace yake,kar binciken mahaifinsa ya cafko komarsa ya wargaza masa shiri,saboda haka nutsuwa ta kaurace masa har ya fara yardarwa kansa taranguhumar da mahaifinsa ke masa kirari ta dace da shi. Rashin zuwa nasa dan dami fatima,don ta fara zargin ko ya janye,har ta kasa daurewa sai da ta sanar da Alh a waya,shi kuma ya nemi Abdullahi ya nemi ba'asi inda ya amsa masa cewa "Babu komai sabgogi ne suka sha kaina amma zan yi kokarin samun lokaci na je ko da bazan same ta ba. Allah bashi jama'ar gidan sun gannin". Cikin muryar bayyana damuwa Alh ya ce "Yauwa ka kokarta don Allah,kar ka wargaza mana shiri,kasan kawun nata wani bahagon mutun ne, idan ba a yi da gaske ba sai ya shawo kanmu,kusan mutane hudu na tura kamar kai yana cafko su? Kai kanka na tabbatar dalilin mahaifinka ya karbe ka" A takaice Abdullahi ya ce " Na sani". Da haka suka yi sallama. Bayan kwana uku da wannan wayar mahaifinsa ya kira shi a waya ya karbi lambar prof a wajensa,wannan ma ya kara kada cikin abdullahi kwarai,kwanaki biyun da suka biyo baya ya yi su ne cikin damuwa da dar dar. Zahirin maganar shi ne, malam ya nemi izinin ne na

zuwa neman wa abdullahi auren fatima, prof ya yi murna kwarai don shi ma ya shiga fargabar dauke kafar Abdullahi,jiya haka ya dinga surfa fatima da fadan cewar ita ta kore shi. Cikin farin ciki ya yiwa 'yan uwa da abokan da suka kamata taya shi karbar wadannan manyan baki waya, ranar kuwa duk suka hallara. A takaice a wannan zuwan nasu suka kawo sadakinsu dubu hamsin,ba a tashi wannan zaman ba sai da aka kulla auren fatima da abdullahi da shaidun da ba su haura sha biyu ba,aka yi musu fatan alkhairi da fatan samun zuria'a ta gari. Tirkashi! Fatima ba labari,Abdullahi ma haka, sun zama ma'aurata a wani irin yanayi mai shayar da mamaki,to balle kuma Alhaji. Su kawu suka raka su motocinsu cikin karrama juna da yiwa juna godiya.sannan aka rabu duk suna ganin mutumcin juna. Bayan sallar isha'I kawu ya shigo gida, momi ta shigo ta same shi,ko zama bai barta ta yi ba ya yi mata umarni da kiran fatima. Ba tare da ta nemi ba'asi ba ta fita sai ga ta tare da fatima.Ta durkusa ta gaishe shi.sannan ta koma gefe ta zauna. Ya dube su gaba daya cikin raha ya ce. "Sai na ba ku albishir din tare ko?" Bai jira cewarsu ba,ya dora da cewa. "Dattawan Abdullahi

sun zo,cikin ikon Allah har an daura auren,ungo sadakinta ba ta". Ya mikawa momi kudin. Momi ta rafka guda,amma fatima sai ta yi mutuwar zaune,d [truncated by WhatsApp]

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

.20) Me kake tunani game da mata da kake son cusa kanka cikin lamarinsu?" Kai tsaye kuma a nutse Abdullahi ya amsa. "Neman ilimi nake a cikin lamarinsa,don ina so dacewa da alkhairinsu,kuma ina neman tsarin ubangiji daga dukkan sharrinsu. Ban taba mafarkin zalunci a gar su ba,don haka nake neman toshe duk wata kofa da zan iya zaluntar da su ko da bisa kuskure,idan ka tuna,aurena na farko zabin kai na ne,amma ban yi dace tana da tarbiyya ba. Na biyu kuma ku kuka zaba min malam,amma Allah ya sani bana kawar auren mace irinta,don haka har yau a cikin rudu nake. Don haka na nemi wannan auren saboda ta dace da irin matar da nake wa kaina fata,sannan 'yar mutanen kirki ce.ina hasashen zata dinke duk wata baraka a cikin sakokin zuciyata". "Me ka tanadar wa adalci?" Tambayar da malam ya yi masa ke nan bayan ya dire,shi ma ya kuma amsawa a takaice.

"Niyya da kyakkyawan fata". Malam ya jima cikin nazari cikin kada kai, sannan ya nisa ya ce. "Abu Turab ina maka fatan aikinka ya yi dai dai da hikimar zancenka,amma ka sani bayan wannan zan bibiyi matar da aka ba ka don sanin irin gidan da ta fito. Idan na ga zaka iya tafiya a turban daya zan bar maku aurenku,sharudana a nan su ne. Kar na kuma jin ka da neam aure nan kusa, sannan duk wani hukunci da zaka yanke a gidanka ya zamana da sanina kafin ka yanke shi,kar na kara jin ka tura 'yar wani gidansu. Ina fatan ka. Fahimce ni Abdullahi ya gyada kai yana mai godiya sannan mahaifinsa ya ce. "Allah ya yi maka albarka,Allah ya jagoranceka, ya ba ka ikon yin adalci a tsakanin matanka". Cike da farin ciki Abdullahi ya dinga amsawa"amin amin. Fiye da sati daya abdullahi bai kuma waiwayar gidan su fatima ba,gaba daya a tsorace yake,kar binciken mahaifinsa ya cafko komarsa ya wargaza masa shiri,saboda haka nutsuwa ta kaurace masa har ya fara yardarwa kansa taranguhumar da mahaifinsa ke masa kirari ta dace da shi. Rashin zuwa nasa dan dami fatima,don ta fara zargin ko ya janye,har ta kasa daurewa sai da ta sanar da Alh a waya,shi kuma ya nemi Abdullahi ya nemi

ba'asi inda ya amsa masa cewa "Babu komai sabgogi ne suka sha kaina amma zan yi kokarin samun lokaci na je ko da bazan same ta ba. Allah bashi jama'ar gidan sun gannin". Cikin muryar bayyana damuwa Alh ya ce "Yauwa ka kokarta don Allah,kar ka wargaza mana shiri,kasan kawun nata wani bahagon mutun ne, idan ba a yi da gaske ba sai ya shawo kanmu,kusan mutane hudu na tura kamar kai yana cafko su? Kai kanka na tabbatar dalilin mahaifinka ya karbe ka" A takaice Abdullahi ya ce " Na sani". Da haka suka yi sallama. Bayan kwana uku da wannan wayar mahaifinsa ya kira shi a waya ya karbi lambar prof a wajensa,wannan ma ya kara kada cikin abdullahi kwarai,kwanaki biyun da suka biyo baya ya yi su ne cikin damuwa da dar dar. Zahirin maganar shi ne, malam ya nemi izinin ne na zuwa neman wa abdullahi auren fatima, prof ya yi murna kwarai don shi ma ya shiga fargabar dauke kafar Abdullahi,jiya haka ya dinga surfa fatima da fadan cewar ita ta kore shi. Cikin farin ciki ya yiwa 'yan uwa da abokan da suka kamata taya shi karbar wadannan manyan baki waya, ranar kuwa duk suka hallara. A takaice a wannan zuwan nasu suka kawo sadakinsu dubu

hamsin,ba a tashi wannan zaman ba sai da aka

kulla auren fatima da abdullahi da shaidun da ba

su haura sha biyu ba,aka yi musu fatan alkhairi

da fatan samun zuria'a ta gari. Tirkashi! Fatima

ba labari,Abdullahi ma haka, sun zama ma'aurata

a wani irin yanayi mai shayar da mamaki,to balle

kuma Alhaji. Su kawu suka raka su motocinsu

cikin karrama juna da yiwa juna godiya.sannan

aka rabu duk suna ganin mutumcin juna. Bayan

sallar isha'I kawu ya shigo gida, momi ta shigo

ta same shi,ko zama bai barta ta yi ba ya yi

mata umarni da kiran fatima. Ba tare da ta nemi

ba'asi ba ta fita sai ga ta tare da fatima.Ta

durkusa ta gaishe shi.sannan ta koma gefe ta

zauna. Ya dube su gaba daya cikin raha ya ce.

"Sai na ba ku albishir din tare ko?" Bai jira

cewarsu ba,ya dora da cewa. "Dattawan Abdullahi

sun zo,cikin ikon Allah har an daura auren,ungo

sadakinta ba ta". Ya mikawa momi kudin. Momi

ta rafka guda,amma fatima sai ta yi mutuwar

zaune,d [truncated by WhatsApp

Zuciya d kwanji

21) Fatima ba ta sami

kebe kanta ba saboda dan bikin da jama'ar

gidan

suke mata,sai ta yi kiran wayar Alh. Yana jinta cikin kuka sai hankalinsa ya tashi,ya hau tambayarta cikin rudewa, da rarraunar murya ta amsa masa. "Wai me ya karfafa maka gwiwar hada ni da aure da Abdullahi ne? Me ya saka tsammatar masa kyautata muradanmu?" A birkice ya hau amsa mata. "Kanin abokina ne, mutum ne mara wargi, sannan yana da tausayi,ya nuna kulawarsa game da mu da nuna damuwarsa akan matsalarmu,don haka na mika masa kokon bararmu tare da hikimar kawu ba zai yarda zaki yi auren kisa wuta da shi ba.... Wai me ya faru? Ta tsayar da kukanta tana goge hawaye, ta ce. "To Allah ya takaita". Ya ji kamar ta doki kolin kansa da tabarya, ya ce. "Ki fada min abin da ya yi miki". Ta fari numfashinsa da cewa. " Babu abun da ya yi min. An daura auren ne yau da magariba". Shi ma ya ji labarin a wani hagunce,bakinsa na rawa ya ce. "Ban gane ba? Sam bai sanar da ni ba,alhalin dazu ma mun yi

waya da shi". Fatima ta hadiye wani kututun

takaici ta ce, "To waya sani ko shi bai sani

ba,don ni ma ba ni da labarin sai bayan daurin

auren,shi yasa na fara tsoron lamarin. Alh ka yi

ganganci da ka dauko dan malamai ka hada ni

da

shi, ina shakkar idan Abdullahi bai zame min

matsala a numfashi na ba". Nan take shi ma

tsoron ya cika shi,ya ce. "Me yasa kika yi

hasashen haka?" Cikin karaji ta ce. "Haba!

Kana

ganin yadda aka yi min aure shigen na lokacin

sahabbai, ranar da kawu ya fara ganinsa. Fa,

washegari da safe. Ya yi kirana ya ce min. " Na

ga Abdullahi jiya, har na ma ba shi aurenki,

saboda. Haka sai ki kiyaye, a yanzu dai dai kike

da. Matar aure,sadaki kawai kike. Jira. Da

shaidu". Yau kuwa suka kawo sadaki aka kulla

auren su I su, sai dazun aka sanar da ni".

"Dakata! Ka daina maganar adalcin nan don

Allah,ka san duk adalci da zai maka bai kai

wanda zai yiwa kansa ba, da me ka shirya

kalubalantar adalcinsa idan ya ki sakina?"

"Kinga

zan kira shi a waya yanzu...." Ya tari

numfashinta ba cikin hayyacin sa ba,ita ma ta

tare shi cikin sheshekar kuka.

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.22) "Kar ka kira shi,kasan yana da iyali, zasu

iya. Sauraron abin da za ku tattauna..... Kawai

mu zubawa sarautar Allah idon,ni dai rayuwata

tana cikin wani hali......" Duk suka rude,ita

kuka

Alh kuka,soyayya ke nan ruwan zuma.

*************** ************** Abdullahi

ba shi da

labarin auren, sai washegari ranar da ya doka

sammakon amsa kiran mahaifinsa,wanda ya ce

masa ya biyo kafin ya wuce wajen aiki. Tunda ya

shiga gidan gabansa ke faduwa saboda yadda ya

ga jama'ar gidan na masa wani irin kallo,har

aka

yi masa iso ya isa falon mahaifinsa. Bayan 'yan

gaishe gaishe malam ya ba shi albishir.

Numfashin Alh ya kai gwauro ya kai mari,amma

sai ya hadiye ya ce. "Har yau ban gano inda aka

haifi matsalar da kike mana hasashe ba". Kai

tsaye ta amsa masa. "Ka rayawa ranka hujjar

da

Abdullahi zai gabatarwa mahaifinsa kafin ya

saki

aurena a cikin sati biyu? Labarin da na samu

wajen momi duk 'ya'yan gidan su Abdullahi na

yin abu ne bisa jagorancin mahaufinsu. Sannan

idan ma zai sake ni na tabbatar a matsayinsa

na

dan malamai zai yi min saki ne na sunnah,wato

saki daya wanda yana iya sakina a yau,gobe

mahaifinsa ya sa shi lallai ya mayar da ni, na

mayu fa Alh? Idan ma ba a yi haka ba,ni kuma

in

zo gida na riski tashin hankalin kawa,kila silar

da

zai haramta mana komawa aurenmu ke nan, dul

ba ka yi wannan tunanin ba Alh? Me yasa ba ka

hada ni da wanda ba shi da wata kyakkyawar

nasabar da za a duba ba?". Sai numfashin alh

ya

shiga sassarfa,ya ce. "Duk ban taba wannan

hasashen ba, na fi la'akari da adalcinsa...."

Yana

rufe baki ta amsa. "Dama na kiraka ne don na

sanar da kai jiya ni da iyayenka muka je gidan

prof cikin lamarinsu,ka sanar musu da taushin
harshe, ka yi kokari ka fita hakkinsu ka ji? Ni
kaina na yaba da gidan da ka nemo aurenka irin
su prof a wannan zamanin sun yi karanci".
Abdullahi ya yi shiru kawai,shi kadai yasan abin
da ransa ke zakka a wannan iyali. "Ka je ka
fara
shiri daha yanzu,ni ma bana son a dauki lokaci
ba
ta tare ba,don kar mu zama kananan mutane".
Abdullahi ya jima cikin shiru,sannan a kunyace
ya
ce. "Nan da sati daya ya yi malam?" Malama ya
dan murmusa,ya ce. "Allah ya nuna mana".
Abdullahi ya wuni ne cikin nazarin yadda
rayuwar
aurensa na sati biyu kasance,wai ya ya zai
tunkuri wannan rayuwar ne? Da me zai yi
tunkahon da zuciyarsa ke raya masa a auren
fadimatu? Da wacce hikimar zai tari kalubalen
da
zai dinga shigo masa dalilin auren a cikin gidan
da waje?.

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.23) Wannan lissafin ne ya hana shi sukuni a

wunin wannan ranar,har bayan sallar isha'I

inda

ya hallara a gidansa. Girki uwargida sadiya

ne,ita

ke ta dawainiya da shi a katafaren falon inda

ya

langwabe yana bayyana gajiya,yana kishingide

a

kujera idonsa lumshe,kana kallonsa zaka gane

ba

a fata gajiyarsa ta tsaya ba har ma da zuciya.

Sadiya ta dinga nazarinsa,sai ranta ya raya

mata

kawai miskilancin nasa ne ya motsa,domin tun

shigowarsa bai mata maganar da ida an jera

zata

cika layi hudu ba. Duk da haka ba ta yi zuciya ta

bar masa dakinsa ba,sai ta kame ta ci gaba da

kallon talabijin. Dai dai wannan lopkacin kiran

Alh

ya shigo wayarsa,ya daga wayar sannan ya

gyara

kishingida,a kasaice ya yi sallama. Kawai sai Alh

ya fara da tuhumarsa. "Sashe har an daura auren tun jiya,amma jiya da na kiraka ba ka sanar da ni ba?" Kai tsaye Abdullahi ya amsa masa "Haka ne, an daura tun jiya,sai dai ni ma ba ni da labarin sai yau da safe malam ya yi kirana ya ce da ni an daura min aure". Hantar sadiya ta yi masifar kadawa,ta dora masa ido babu ko kakkautawa tana kallonsa yana yamutsa fuska,yana sauraron kashedin da alh ke masa. "To sai ka yi kokarin cika alkwari,kuma in son ka ci gaba da dauke kafa a wajenta tunda an yi mai wuyar,kar ka sake ka taba min mata ka ji ko?" A takaice Abdullahi ya amsa,"To". Alh ya ce masa. "Yaushe ne tariyar?" Abdullahi ya mayar masa da amsa. "Na sanar da malam nan da sati daya nake son ta tare,ya kuma amince min, don haka zan yi kokarin

ganinta a gobe..... Ka dai tsumaye ni nan da

sati

uku". Jikin Alh a sanyaye ya yi masa sallama ya

ajiye wayar,shi ma ya fara shan jinin jikinsa

cikin

lamari,ya fara jiyo kashin gaskiya a cikin

hasshen

fatima,me yasa komai sai da malam za a yi?

Abdullahi na ajiye waya sai ya lumshe ido don

haka sadiya ta yi mugun kuluwa,a kuntace ta

ce.

"Abu Turab wa aka daurawa aure?" Ya yi

firgigit

ya tashi zaune kamar wanda ya ko daga bacci ya

ce. "Oh yi hakuri,dazu na yi ta kiran wayarki na

ji

ta a kashe,zan sanar da ke an ba ni aure har an

daura shi a jiya,yau malam ke sanar da ni".

Maganar da a zane ba ta fi sadara uku ba,

amma

girmanta ya zarce na gwaron dutse a

kwakwalwar

sadiya,sai ta rasa abin da zata ce, kallonsa

kawai

ta ke kirjinta na bugawa,dakin na zagayawa da

ita. Ba tare da ya direta ba ta tilastawa kanta

yin

magana bayan da numfashin ta ma ya karbi

nasa

aikin na tafiya cikin sassarfa. "Na yi nadamar

aurenka Abu Turab,babu wani alkhairi a ciki

aurenka wallahi...." Ya tashi zaune a

hanzarce,ya

kuma ware ido yana kallonta sosai. Ba ya

mamakin fitowa wadannan kalaman daga

bakinta,don ya yarda rashin arzikin sadiya ya

wuce nan, sai dai ya kasa sabawa,sam ya tsani

rainin hankali.sai dai a yaunasihar malam ta yi

masa birki,kawai sai ya sanya ido yana kallonta

har ta sami damar dorawa. "Ai ko na mamajo

ne

kai iyaka ke nan. Cikin shekaru hudu aure

uku,ba

za a hada biyar ba sai ka rufe kofa,haka kawai

da

kuruciyata ka tara min kishiyoyi? Ni ban haifa

na

kana auro 'ya'yan wasu suna neman jaza min

ciwon zuciya,ayi magana ka ce malam ya yi

maka aure kamar wani dan akuya,idan haka ne

gaba daya ma auren malantar ba shi da wani amfani". Har yanzu ya kasa tanka mata,idonsa dai na kallonta kai tsaye,fuskarsa kuma ta ki byar
da wani karatu da zai sa a fahimci matakin da zuciyarsa ta dauka,watakila hakan ne ya sanya sadiya mikewa ta ci gaba da zazzaga masifa. "Ni wallahi idan babu hali sai dai ka bani tikiti na daware.Ba zan yi ta zaman hakuri da kai babu tsatso ba, amma kai kullum idonka akan mata, ka
tara mu ridi ridi babu wani abun arziki ko kai har
yau ba ka yarda kai ne ba ka haihuwa ba, ka ke lilon tara mata?" A wannan karon sai ya tanka,kuma cikin murmushi wanda ke bayyana walwalar zuci. "Ya ya za a yi na ki yarda alhalin na riga na gada? Kin san 'ya'ya talatin din. Da ke
cikin gidanmu a ruwa iyayenmu mata suka sha?"
Sai ta kara butsarewa cikin tsabar fitsara,ta ce. "To idan ma ba ka gada ba Abu Turab,babu shakka an fitar da zakka,kuma babu ta inda ido ya mutu kwalli ya tono shi". Shi ma tana rufe

baki ya amsa cikin halin ko'in kula da son tura

haushi. "Haihuwar kawai na rasa,amma Allah

bai

hana ni komai ba bayan ta,ciki har da ba ni

damar na auro na kuma aurowa,ko zan dace da

mai tsarkin zuciyar da zata karbe ni

abakararena,ba tare da ta tsangwame ni ko ta

tsangwami kanta ba. Kinga sai kiji mu luf in

yaso

dangi sa haifar mana'ya 'yan da zasu ji

kanmu.

Maganar ta yi masifar bakantawa sadiya rai,

musamman da ta tuno lokacib da zai auro

hindatu irin wannan tabarar ta dinga bare

masa,

amma bai taba damuwa ba,sai ya dinga nuna

mata shi kansa ba da son ransa zai yi auren ba,

don da ba zai iya yiwa malam musu ba ne kawai.

To wannan ta kayatar da zuciyarsa ke nan da

yake neman cin fuskata akan aurenta? Amsar

wannan tambayar ta fara kada hantarta tun

ma

kafin ta santa,ya ya amsar zata samu? Abu

Turab ba shi da kirki idan bai ga dama

ba,soyayya ba ta hana shi rashin mutuncinsa

idan ya motso. To da wanne KWANJIN zata

kubuta daga fifita amaryarsa da zai iya yi idan

ya

fi kaunar amaryar a kanta?24) Gaba daya tashin hankali da rashin hakuri

suka bayyana a fuskarta,sai huci take kamar in

ta

bude baki za aga hayaki,idonta a kansa,wannan

yasa ya yi saurin yin fuska bayan ya dube ta

sakarce,idonsa cikin nata,ya ce. "Kuma ya ishe

ki

haka! Kishi ba hauka ba ne,kar ki nemi ki zage

ni"

Bai ba ta damar magana ba,ya daga wayarsa ya

kira Hindatu,yana ajiye wa sadiya ta sauke

fushinta cikin debe kauna. "Wai Abu Turab idan

na zage ka me zaka yi? Ya hadiye dariyar da ta

cika masa ciki. "Kin fi ni sani. Billahillazi idan

amaryar ta zo sai in nuna miki iyakarki,in dinga

hada mata kwananta da naki in ga abin da zaki

yi, za ki ce in fita in bar miki gidanki ne tunda

ke

kike aure na? Ba ta sami bakin magana ba,sai

ga

Hindatu ta yi sallama ta shigo. Ta same su a

hargitse, sadiya a tsaye tana cika da batsewa,

Abu Turab a kwance ya hada girar sama da ta kasa. Tana neman gurin zama ya tare ta. "A'a kar ki zauna! Mike ke ma idan kina da wandon taki rashin kunyar ki juye min.Aure aka daura min jiya,ma'ana kishiya na yi muku". Duk da maganar ta caki zuciyar Hindatu matuka,amma sai ta hadiye kasancewarta mai dabarar boye fushi da bacin rai,muryarta a sake ta ce. "Da gaske?" Ya saci kallon sadiya,ya kara murde fuska ya ce. "Akan me zan muku karya? Wallahi da gaske ne, kuma cikin satin nan zata tare". Hindatu jima tana dubansa,tana kuma satar kallon sadiya,ko zata ji zafin aurensa tana sa ran sanyinsa saboda sadiya,domin mace ce mara kaunar zaman lafiya,Allah kuma ya ara mata dama tauraron sadiyar ya fi nata haske a idon Abu Turab,duk da munanan halayenta,ke nan Hindatu zata yi farin ciki da auren Abu Turab musamman idan amaryar

zata danne tasirin sadiya. Da murmushin da ya ratsa har zuci,hindatu ta dube shi ta ce. "To don me zan juye maka kwandom rashin kunya,alhalin dama nasan kana da sauran kofofin? Ka auro biyu ma ni yanzu na shirya,abin da ba a kaina a su zauna ba?" Haba! Sai sadiya ta kara tunzura ta ga yarfe kawai Hindatu ta yi mata. Ta yo kanm Hindatu da bala'I. "Abin da ya fi haka ma kina da lokacin ki fada tunda a dure kika ganshi,dama kin san da wata a ciki kika shigo saboda haka dole wasu su biyo bayanki. Ni ce nasan darajarsa a sabonsa ko mijin mace dubu ne ba hudu ba,auren soyayya ai ba karya ba ne".

Sai da ta jima da sauke numfashi sannan Hindatu ta mike tana amsa mata.. "Allah ya yi mana tsari da soyayyar fatar baki,salon soyayyar ke nan kike juye masa kwandon rashin kunya? Ni da ba na sonsa yake tsammanin mun shula irinta a

gidanmu? To Abu Turab ba mu da gonarta, aure kuma Allah ya sanya alheri,Allah ya sa badi war haka ka cike gurbi" Babu alamun wasa da shakka a fuskarsa da muryarsa,ya amsa. Ba amin ba,ai wannan matsayin mace biyu zata shigo,ina fatan daga kanta in kulle kofa,babu shiga babu shiga babu fita Babu alamun wasa da shakka a fuskarsa da muryarsa,ya amsa. Ba amin ba,ai wannan matsayin mace biyu zata shigo,ina fatan daga kanta in kulle kofa,babu shiga babu fita. Hindatu kanta ta ji ciwon maganarsa,amma nan da nan ta watsa ta kan sadiya. "A'a wannan sai dai ka fadawa mai auren saoyayya,ni me amsa sunan abin da ahnnunka na dama ya rika me zan dorar? Duk da ka watsa mata kasa a ido ba ka ce ita ke amsa matsayin mace biyu ba". Ba ta jira cewarsa ba bare ta saurari hayaniyar sadiya ta fice daga falon,shi ma ya mike ya kule a bedroom har da murza key yana sauraron gorin da sadiya ke lika masa iri iri har da na sharri

sannan ta koma kan hindatu.

Hafsat

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

25) Washe garin

ranar sai a office ya karya,don sadiya ta dauki

zafi sosai da shi,har ya bar gidan bai ga keyarta

ba,bayan ya gaji da bugun kofarta ki budewa.

Sai

wajen sha daya ya daure ya kira wayar

fatima,sau biyu tana katsewa yana sake

kira,sai

ana ukun ta daga bayan ta kusa yankewa. Ba ta

ce masa kala ba,shi ma sai ya shiga numfashin

jin isa,sannan murya a bace ya ce. "Zan shigo

anjim,ko kina ganin na zamana kawai?" Ta sha

kamshi da kyau,kafin a kasaice ta ce. "Don me

zaka yi zaman naka?" Tana rufe baki ya amsa

mata. "Don kar na zo mu aikatawa juna ba dai

dai ba,kina satar hararata,ni ma haka. Idan ta

kure ki yi min tsaki....mts! Idan zuwan nawa ba

shi da. Wani muhimmanci na share kawai...."

Ranta ya yi masifar baci,ita kanta kuma ta rasa

abin da ya bata maya ran.tsakin da ya yi mata,

ko ma'anar korafinsa,ko kuma rashin ba ta girmanda kima? Ya kamata duk ukun,su bata mata rai, amma ta fi jin ciwon rashin ba ta kimar,tasan ko makiynta na sonm kallon kyakkyawar fuskarta ko da tana kunshe da abin da ya fi harara,amma me yasa kyawunta ba ya dada Abdullahi a kasa? Dole ta tare wadannan kalubale ga zuciya ta hadiye,murya a bace kamar

dole ta ce. "Na fika kin zuwan naka, don akwai ciwo cikin kaskantar da kai na saurare ka.... Sai dai kama iya zuwa domin zuwan naka yana daga

cikin biyan hakkin da muka dauke ka akai". Ya dan yi jim, tunkunna ya amsata. "To idan haka ne

zan dauki hutu akan zuwan,zan komo bakin aiki ranar da akika tare...." Ta yi saurin tare shi a tunzure kamar tana a gabansa. "Za ka samar da

gibi ke nan... A halin yanzi jama'ar gidan nan sun

damu da rashin zuwanka.... Za ka zo ne domin su ba don ni ba, don ni babu abin da zai amfane ni a zuwanka.... Kashedi na karshe,idan ka zo

bama son takura,kar ka yi min irin zaman kunatar da ka yi min zuwanka na farko...." Shi ma ya tare ta kamar sike. "Shi yasa ai na ce na yi zamana kar na zo,ki ga bakar fuskata". Daga nan ne ta gane zafinta ba zai ba ta ladabinsa ba, sai ta dan sassauta murya ta ce. "Idan ba zaka yi min zaman kunatar ba ke nan?" Ya dan ja fasali lafin ya tanka ba tare da shakka ba. "Kwarai da agske,ai ban ga dalilin da zai sa ki dinga daga min hankali ba.ban taba yi miki kallon wata mace da don va rabe ta zan ji abin da kike kokarin yi min katanga da shi ba,watakila da na yi miki kallon cikkakiyar mace ba zan karbi wannan kwangilar ba, don na na munafunci...." Tun da fatima ta ke ba a taba fada mata magana mai munin wannan ba, abdullahi ya ci fuskarta matuka! Ya kuma kara sanyawa zuciyarta kullaci game da shi.To me ta rasa? Tambayar da yakanmata ta yi masa ke nan, amma shakkar

amsar da zai iya ba ta ta yi mata birki. Ta hadiye yawun takaici, a kausashe ta ce, "Ido kayan wari ko? Inji makaho, Na tabbatar idan na rantse ba zan yi kaffara ba,ba ka ajiye kyakkyawar mace kamar ni a gidanka ba...." ya tari numfashin ta a dake. "Ai ba a nan ta keba, wai an danne bodari a ka". Ta yi dif wasu kwalla masu zafi suka fara cika mata ido,ta rasa ma tunanin da zata yi akan wannan mutum wanda wulakanci ya zagayewa numfashin Dukkan KWANJINTA ba shi da tsiri a muhallansa.kyauta, kudinta da iya jan zaren mulkinta ya wasa kefa allamar su duka sai ya hada da ta mutuncinta da fuskarta. Kuka ya dan fara fixgarta,ta kashe wayar bayan ta ce masa. "Abdul ba ka da mutunci wallahi. Na gode". Ya jima yana kallon wayarsa,kalamanta na yawo a kwanyarsa. Ya dan kafa ido alamun son raba hankali fiye da gida biyu,har lokacin da jarumtarsa ta motsa ta danne komai ta ba shi

damar tabe baki ya ci gana da harkokinsaa

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.26) Fatima ta wuni da wannan takaicin da zarar babu idon mutane sai dai ta yi ta faman hawaye. Ta rasa inda zata tsoma ranta ta ji sanyi bare hanyar da zata bi ta fanshe wannan cin mutumcin da Abdullahi ya yi mata. Wannan bai hanata da $omi zuwansa ba, aka yi ta hidimarsa kamar wancan lokacin ko m$a fiye tunda yanzu ya zma a halin gida. Ita ce dai ba ta

wani shiri game da zuwan nasa,har sai da jama'ar gidan suka kwabeta bisa rashin wanka da canja tsari, sai ita da kanta ta ga beken kanta.To mutumin da ka yi kwalliya ma ya. Ce ba ka da kyau ina ga ba kayi ba? Kawai sai ta biyewa su safiya,ta yi gayu na garari ta saka kaya wadanda suka lafe a jikinta suka kuma dace

da fatarta,ta yi fes kamar mai shirin gasar sauraniyar kyau.A yau babu ma rigakafin wato laffaya,sai yalolon mayafi ta yafa irin rufin 'yammatan zamani. Karfe biya dai dai ya

rangada

mata waya tana ganin sunansa sai da gabanta

ya

fadi, haka kawai abdullahi ya fara tsoratata,ga

kuma su safiya a wajen bare ta dizga shi. Ta

daga wayan da walwala a fuskarta,amma ta

kasa

tanka shi, shi ma a takaice ya ce. "Na karaso".

Ta dinga zabga murmushin dole,a$$a ta kasa

tankawa, sai mata sauke wayar tana ajiyar

zuciya. Safiya da shukura suka tafa,shukura ta

ce, "Tabdijam, wanna gayen ya tafi da

imaninki."

Duk suka fice suka barta tana binsu da kallo

wasu kwalla suka cika mata ido,in banda dole

mai Sanyawa a kwana a ido,ai babu dalilin da

zai

kai ta inda wancan dan rainin hankalinm zai ga

inuwarta. Har wasu mintuna tana zaune sai da

ya

turo mata khalid da kira sannan ta dauro amsa

kira. Tan shiga falon suka doramata ido su

duka,musammam Abdullahi wanda yake mata

kallo daga sama har kas,idanuwansa na fitar da

wasu sakwani wanda zai sa ka tsammaci

tsantsar soyayyar amaryarsa a cikinsu bai tsaya

ga tura sakon kawai ba sai ga shi tsaye nuna

alamun girmamawa da marhabin. Su salma sun

baz amata ido sai ta rasa irin acting sin da zata

karbe shi,don haka ta ji kafarta na

hardewa,shi

kuma Abdullahi ya sami distination da nasa

acting din, domin har ya isa gabanta bai kuma

bata lokaci ba ya ware hanununta ya rungume

ta.

Dakin ya fara wantsalata,kirjinta yana

harbawa ta

fara kokarin kwacewa lokacin da ta fara jin

shewar su safina yahanata da jarumtarsa ta

namijim da ya lakanci soyayya.ya dago kanta

ya

sumbaci goshinta.sannun a hankali ya bi

kunnenta yana rada mata wasu manyan

kalamomi masu huda zuciyar masoyi,don haka

kwakwalwarta ta kasa fassara mata su. Face

wasu 'yab kwayoyi da zuciyarta ke fada mata

kamar sun shafeta

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

27) Wadannan sakanin da za su iya samar da

mintoci sun yi min kama sa mafarki,sun dan

kwatanta min ana samun aljanna a duniya....

Fadima numfashinki na da sanyi da kamshin

shaka kamar yadda jikinki ke tashin kamshi.....

Dole ki yi tasiri mai karfi a rayuwar masoyi ko da

bai shirya hakan ba...." Ta zame tamkar

mutum-

mutumi,tare da shi ya ja ta zuwa kujera ya

zaunar da ita,sannan zauna ya zauna a

hannun

kujerar,ya dafa kafadarta ya kokarin su hada

ido,ya ce. "Ki share su safina,don sun ga kina

jin

kunya suke miki wannan dan bikin". Ya juya

flga

su safina yana dariya. "Ku je abinku na gode

da

karramawa". Ba su bar yi musu shegantaka ba

suka fice, A sakanni goma dakin ya bayar da

dif!

Kafin kowa ya yunkura. Abdullahi ya mike

zumbur

ya bayar da baya cikin kankanin lokaci ya canja

fuska,kamar fuskarsa ta ranar haduwa, wadda

ta

dace da munanan kalamansa a waya. Hakan ne

yab hadar wa fatima takaici da kaicon

mu'amalar

da ya yi mata a yanzu,a matsayinsa na baranta

da matsayinta a gurinsa na wadda ba ta isa

hada

kafada da sauran mata ba, kawai sai ta sami

kanta da kuka kashirban. Ta dinga kuka kamar

ranta zai fita yana tsaye rungume da

hanaye,ya

juya mata baya kamar kukan nata ba ya

damunsa,har dai ya juyo gare ta fuskarsa da

alamu tausayawa irin na tsananin namiji mai

imani da mace mai rauni. Ya durkusa a gabanta

tare da dago fudkarta muryarsa a raunane ya

ce.

"Abin da na yi ya fice yadda yakamata plan

dinmu ya ajiye ko? Ki yi hakuri ban yi don na

bata ranki ba. Ba kuma wani sabon abu ba ne a

cikin dabi'una,dama haka nake don haka ban

ga

wata hanyar da ba ta kai wannan ba wadda zata

nuna farin cikina da kasancewarki amaryata ko

da ta a gaibu ne. Ina jin kin ji ciwon haka ne

domin kiyayyata da ke cikin zuciyarki.... Ama kuma...." Ta kwace kanta tana share hawayenta,kuma ta tsayar da kukan sai dai zuciyarta ta kara rinewa da takaici. A kufulce ta
ce masa. "Takaici na ya samu ne ta hanyar ba ni matsayin macen da zata iya shiga gonar soyayyarka ne, ko da kuwa a plan dinmu ne.... Ko ka manta ne? Yakamata ka bi wata hanya wadda zata ba ka damar ci gaba da jadadda abin
da ka fada idan dai ba rikidewa na yi daga halittar dutse na koma mace a idonka ba......" Muryarsa a tausashe ya tare ta da cewa."Kin kuntata fahimtarki ga magana ta fadima, idan babu soyayyar da zata samar da sha'awa a tsakaninmu me yasa ba zamu samar da wadda zata samar da zaman lafiya a tsakani mu ba? Dube ni a wani dan uwanki,idan ma ba zaki iya hakan ba, yi min kallon baranki amma ki samar da kauna ta tsakanin yaro da uwargijiyarsa". Ta
fara sassarfar numfashi bayan kishiyoyin abubuwa biyu sun hadar mata lokaci guda takaicin da maganarsa ta samar mata da tsoron

janyewar biyayyar Abdullahi da ta fara samu

idan

" Na ji,matsa ka ba ni waje". Ya mike yana

dariya,ya ce. "Shi ke nan zo ki ba ni abinci kar

su

ce ban ci ba". Ta dago ta zabga masa harara,ta

ce, "Share guri ka zauna ba zan kara zuba maka

ba,ko kudin ka sanya ka siyo ni?" Ya amsa cikin

dakewa. A'a,ni kika sa kudi kika siyo,kuma

kanki

za ki tsinka,don zasu yi tsammanin mun shagala

da wasu al'amura ne shi yasa ba mu tuna abinci

ba". Da ta dan nutsu sai ta ga kamshin gaskiya

a

maganarsa

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

I no see 28.... bear wit me....

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Sumaiya Ibrahim Al-hussain

wldn

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Zainab Abdulkadir Sani

Thnx

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

29) Tun daga wannan rana Abdullahi

bai kara komawa wajen fatima ba,bai kuma kara

yi mata waya ba, abin mamaki sai hakan ya

dinga yi mata ciwo. Ba don takaicin rashin

ganinsa ko kuma fassarar da jama'ar gidan

zasu

yi mata na rashin kulawarsa a gare ta ba, sai

don

hakan da ya yi shaida ce na bai dauke ta a

bakin

komai ba. Kusan Alh ne ya canje shi,domin da

shi

ta ke raba dare suna hira a waya tunda babu

hali

da rana,sannan ya bude mata bakin aljihunsa

da

kyau, wato ya tura mata makudan kudade

asusunta wanda zata yi hidiman bikin da su.ya

so ma ya tura mata kudin Abdullahi na sallama

ta ki yarda da uzurin cewa, idan kawu ya

ankara

kudaden asusunta sun fice kima zai bincike ta,

tunda bai barta sakaka ba. A ranar asabar

ma'aikata suka je suka kawata mata

dakunanta a

gidan Abdullahi, makeken falo mai dakunan

bacci

biyu kowanne da bandaki,a falon ma akwai.ga

kicin hade da sito da kuma baranda. Abdullahi

mutum ne mai kaunar kawata muhalli don haka

girman gidan sa da kawar da gidan ya kunsa bai

yi kama da nasa ba, musamman idan aka dubi

tilon motar da yake hawa alhalin harabar gidan

zata ci motoci hudu.haka cikin gidan ma yana

da

yalwa bayan a fitar da sashe hudu irin na

fatima

sak! Sadiya,Hindatu,shi kuma yake zaune a

cikin

daya.akwai wasu empty dakunan saboda baki ko

wasu bukata na daban,kai har da karamin wurin

shan iska mai kama da lambu.akwai rumfa gefe

da fararen kujeru, can kuma ga bishiyu har da

fulawoyi. Wannan ta dan kara daga darajar

Abdullahi a idon dangin fatima,duk da cewa sai

a

saka gidan Abdullahi bakwai a cikin na alhaji

wanda fatima ta baro,amma ba za'a ce fatima

ta

kastanta ba.ko kuma tsammanin mamallakin

gidan zaiyi sana uren kisan wuta. To haka ake

kashe dala wajen kawata mata nata dakunan

tamkar ta zo da niyyar zama. Ranar lahadi aka

wuni ana shagalin biki da yammaci aka kai

amarya gidanta bayan an kaita gidan iyayen

Abdullahi har gaban malam ya yi ta sheka mata

albarka,kafin ya koma kwarzanta mata angonta

nata da irin kyawawan halayensa. Bayan sallar

magariba kadan kowa ya watse,aka bar fatima

da

halinta, niyyarta da kuma sake saken wadda

zata

fissheta. Gidan dif! Kamar babu wani mai rai sai

ita sai gaba daya kadaici ya mamaye ta don ta

saba gidansu gidan mutane ya mamaye ta, don

ta saba gidansu gidan mutane ba ma ka jin

kunne. Haka gidan Alh ma babu laifi,amma

wannan kamar kufai! Ba ta jima tana kirga

mintunan da suka samar da awa daya da 'yan

kai

ba ta ji dirin motar Abdullahi wato bayan sallar

isha kadan,kawai sai gabanta ya yi wani

mumunan faduwa. Gaba daya ta rikice,sai barin

jiki ta ke ta tashi ta koma falo,ta kara lullube

jikinta da laffayar da ta ke nade,ta fara

duban

kofa tana tunanin darenta na farko a gidan

alh

wanda idan dai irinsa ake wa kowanne irin

ango,to abdullahi ba shi kadai zai shigo gidansa

ba a yau. Ta dan fara jiyomaganganu sama

sama

wanda ta tsinci muryar Abdullahi sai kuma wasu

muryoyi biyu wanda ba su yi kama da na abokan

Abdullahi ba, domin kamarsu na karbar umarni

daga gare shi ne. Ama abin mamaki abdullahi

bai

nemi dakinta ba har sha dayan dare ta

motsa,wannan ya sa ta dan saki ranta,sai dai

ta

kasa ko motsin,wannan ya sa ta dan saki

ranta,sai dai ta kasa ko motsin kirki, iyakacinta

dai falon kamar wadda ta zo ci rani. Sha daya

da

rabi sai ga alh ya kirata a waya ta daga jikinta

na

bari ko sallamarta alh bai amsa ba.ya ce. Fatima

ya nemi shigowa wajenki?" Da sauri ta girgiza

kai

kamar yana ganinta, tukunna ta ce, "Ko

duriyarsa

ma ban ji ba". Alh ya sauke wata katuwar ajiyar

zuciya

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

30) , ya ce. "Haba na shiga rudani,tun karfe

takwas nake kiran mutumin nan yana wata

kiran

nawa a kwandon shara,ina shakkar idan bai yi

adding din lambobina to reject list ba, tabbas!"

Cikin fatima ya dauki wani kugi,ta ce. "Ko Alh?

Ni

kuma sai nake shakkar zai hak*,kasan rabon da

shi tun washegarin daurin auren? Kuma bai taba

kiran wayata ba". A matukar gajiya Alh ya ce.

"Toh,Allah ya saya dore,ki sa wa dakinki key

kinji? Kar ki yarda ki dinga barin kofarki

bude".

Ta ce da shi cikin bin umarni. "To bari na je na

rude". Ta kama key zata murza ke nan

Abdullahi

ya murda handle ya turo kofar. Da gabanta ya

yanke ya fadi kawai sai ta yi mutuwar tsaye wajen. Bai ko dube ta ba ya wuce ta zuwa tsakiyar falon yana kare masa kallo kamar wanda

ya zo daga kauye. Ta silalo a mugun kasalce ta zube kan kujera bakinta fal addu'ar neman tsari.

Ya juyo ya dube a fuskarsa babu walwala ya ce. "Ina ta tunanin ki zo da kaza da kayan sayen baki sai na ji shiru,shi ne na biyo baya"m Ta tilastawa kanta karfin hali lokacin da ta ke kallonsa a sakrce,ta ce. "Dama akwai wannan cikin sharudanmu?" Ya soke hannu a aljihu ya fara cije lebe, Sannan ya zaro hannu daya yana

juyawa ya ce. "Ina tsammanin tana daga cikin sharuda ne masu aiki irin na magani a jikin cuta,kin san ba ko yaushe aikinsu ke tasowa ba,ko kin manta? Ba a zube sharadin zan zo tadi

ki ba ni kudin zance ba kike ba ni. Na rike raina hakan yana da alfanu kamar dai yau,idan kika sai

bakina sannan ki ka kawo min kaza kamar ko wanne mai KWANJI idan ya yi aure". Ta rasa

abin

da zata ce masa saboda fargaba da takaici,sai

kallonsa kawai ta ke. Tana kifta idanuwa,har

sai

da ta sami basirar da zata iya a fada da tasa

basirar. "Idan shi ke nan abin da ya kawo ka sai

ka fice na daina ganin inuwarka,ko kai zaka

biya

ba ni ba. Ba ni da bukatar bakin naka bare ni na

yi asarar kudina... Kaza kuma ka manta illarta

a

tare. Da kai ne da kake nemanta?.... Mts! Mai

tsaurin ido kawai,ka fice ka ba ni guri idan ba

rainin da ka saba ka kawo min ba". Kafin ya

amsa kiran Alh ya shigo wayarta cikin gadara ta

amsa wayar. "Ina fatan kin rufe kofar?" Inji

Alh.

Ta dubi abdullahi wanda ya zuba mata ido a

tsorace,sannan ta dubi kofar bakinta na rawa

ta

ce "Eh, na rufe" "Ya ce mata murya a kwance.

"To sai da safe". Tana sauke wayar Abdullahi ya

dube ta cikin ido ya ce. "Me yasa kika yi masa

karya?" Ta kawar da kai ta ce. "Ai wani lokacin

halal ce...." Ya yi saurin tarar numfashinta, ya

ce.

"Kin ga ni kuwa ban. Karbar halaaccin karya sai ta yi matukar kure min,ko hakan nema sai na kan

yi ta a bai bai" Ta kara bata rai,ta ce. "Ka yi abin

gwaninta,idan ka yi abin da ya kawo ka sai ka fice zan kwanta". Ya dan ja fasali sannan ya dora

cikin nata batun. Akwai saura da yawa". Ya yi fuska sosai ya dubi tsakiyar idonta ya ce.

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

31) "Kar ki kara yi min tsaki balle ki fadi wata kalma mai kama da zagi a kunnena,ko ba ki da tarbiyya ne? Ban girme ki ba? Ya kamata ki ce min na yi miki tsaurin ido? Ko kuma ki fada min idan kimar kudi ta zarce ta zarce ta girma da mutumci....." Ya dan dakata ya shaki iska kadan

sannan ya dora cikin ci da zuci. " Ba na sarayar da girmana da mutumcina akan kudi,idan kina tunanin shi ne tazarar da ke tsaninmu har kika fi

ni tsawo. To ki ajiye wannan tunanin zai fi miki

kyau". Ya ba ta damar magana,amma ta kasa

ta

rasa ma abin da ya cukwaikwiyo

zuciyarta,mamaki? Takaici? Ko kuma

sallamawa?

Sai fitar da numfashi da kyar take yi. " Sai mu

yi

bakwana". Ya katse lissfina,sai ta saka masa

ido

kawai. Ya yi taku kamar uku da hannu. "Duk

ranar girkinki zan shigo kamar wannan lokacin

in

miki bakwana,ranar da sauran ke da girki zan

shigo miki da maraice,sannan duk safiya zan

shigo mu gaisa,sai maganat abinci kowacce na

girkinta daban ne,idan ina dakinta ta hada da

ni,

ke me kika gani a ranar naki girkin?" Ta

tattare

duk masifat da ke makogoronta akan kalmar da

zata fitar. "Ba na bukatar in dora wata

tukunya a

gidan nan, idan na ci 'yan kwalam ma sun ishe

ni

maneji zuwa sati biyun". Fuskarsa ba ta sauya ba, ya tambaye ta. " Kin zo da na sati biyun da zaki yi?" "Ina ruwanka?" Ya kada kai, ya ce. " Babu,sai dai akwai sharadi...." Ta yi sauri dakatar da shi da hannu,sannan ita ma ta mike ya ga tsawonta. "Ba ka da wani sharadi da zaka kafa min shi a yanzu,wanda ba ka kullo shi tun ranar da muka shirya ajandarmu ba, saboda haka
sharadinka ko wanne iri ne ba shi da muhalli a sha'anina". Ya dinga kare mata kallo sama da kasa, sannan ya kada kai,karon farko tun shigowarsa murmushi ya bayyana a kuncinsa,ya janyo cofee table ya zauan. Ya zamana ita ce a tsayen,bai dauke ido daga kanta ba ya amsa mata. " Bayan waccan ajandar ce aka kulla min damar jagoranci a cikin sha'aninki da son ranki ko babu.... To wai me kike wa tsoro? Ki jira ki ji sharadin nawa mana don me za ki hau yi min wannan masifar?" Tsaki taso ta yi,amma ga mamakinta sai ta ji zuciyarta na shakkar ta yi masa tsaki,dole ta buge da kada harshe,sannan ta dubi wani wajen daban. Ya kara fadada murmushinsa yana kara nazarinta,ya ce. " Sharadin nawa ba fa wani mai tsauri ba ne,

dama

fada miki zan yi. Nan gidan babu matar da ta ki

fita sai da izinina,ma'ana idan kina fita a

gidan

Alh ba tare da neman izini ba a nan gidan lallai

ne sai da yardata,don haka kar ki sake in ga

karfarki a waje ba tare da yardata ba" Bai bata

damar magana ba ya kuma dora wani batun

bayan ya mike ya nufi kofa. "A karshe in

shawartarki da karanta waya da Alh, sannan ki

san irin maganganun da zaki yi da shi, saboda

gudun bacin rana wani cikin gidan nan yasan

halin da muke ciki,sannan idan akwai hali ki

dan

boyewa duniya rashin kaunar da kike min,kin

gane ko? Taso ki rufe kofar". Ba tare da ya jira

cewarta v ba ya fice daga falon,tana binsa

galala

da kallo cikin tsabar rudu. Ta rasa makamar da

zata rika don fara nazari akan wannan ba

izgilen

mutumin wanda ko shakka babu ya riga ya gama

damarta,ita ma kuma da alama ta fara sallama

masa tunda ta ke jin shakkarsa,koda yake

dama

can ita ba masifaffiya ba ce, Allah ne kawai

yake

dorata akan mutane suke shakkarat. To da

alama

bai dorata akan Abdullahi ba, wanda yake nufin

wasu abubuwa masu tsauri a kanta,irin wanda

numfashinta zai jure da ma wanda ba zai jure

ba.

"Kar ki sake in ga kafarki a waje..." Maganarsa

ke

nan da ta bude mata kofar hasashen me

Abdullahi yake nufi a kanta? Yana son nuna

mata

iyakartaZuciya d kwanji

.32) Yana son nuna mata iyakarta ne ta hanye

mulkarta don tana cikingidansa ko kuma kawai

yana nufin kuntata mata ne don ya sami

wannan

damar? To idan ba ta fita ba me zata ci? Kuma

idan ta fita ba da izinin nasa ba me ya tanadar

mata? Ba ta iya amsa dukkan tambayoyin da ta

yiwa kanta ba, kuma hakan ne ya taimaka

wajen

raunana zuciyarta ta barke da kuka. Ta je ta

rufe

kofar sannan ta dawo ta zauna ta ci gaba da
kukanta tana tuno tasirin Alh a
rayuwarta,wanda
ba ya iya ja da duk wani zabinta ko da kuwa bai
wa ransa dadi ba, a hakan kuma kullum yake
kirarin sauran mata rakota duniya kawai suka
yi,
amma yau ga ta a gidan da ake aikata mata ita
ta rako matan duniya,har da bita da kullin
takura
da wulakanci. Kusan a nan zaune ta kwana a
nan
falo,sai da aka fara kiraye kirayen sallar asuba
sannan wani malalacin bacci ya fara fizgarta.ta
daure ta jira sallar asuba ta gabatar da ita
sannan ta kum kwanciyar anan falo bacci mai
nauyi ya dauke ta A hannu daya sadiya ta fita
daga nata kuncin tun shigowar Abdullahi a
daren
jiya wanda ko kallon kofar dakin amarya bai yi
ba,ya share guri ya zauna kallon wasan kwallon
Kafa,har wannan daren ya yi musu asuba ta
gari
sannan ya waiwaye amaryar shi ma kamar akan
kaya,sadiya na duban agogo mintuna ashirin da

takwas ya yi ya fito ya shige nasa dakin har
wayewar garin nan. Sadiya ta gama yardar wa
ranta wannan amaryar har ta fi Hindatu
kaskanci
a idon Abu Turab,lallai babu wata mace da zata
sami rabin matsayin da ta ke da shi a zuciyarsa,
wannan ya sa kashi 70% na kishin amaryar ya
fice daga zuciyarta,hanka linta kwance ta shari
bacci har da saleba. Wajen karfe goma Abdullahi
ya kwankwasa kofar sadiya cikin shirin fita,ba
shi
da yakinin zata saurare shi,domin jiya.da safe
kaca kaca suka rabu. Amma ga mamakinsa ko
minti daya bai hada ba ta zo ta bude kofar,ba
tare da ta dube shi ba ta wuce kai tsaye , ya bi
bayanta ya zauna hannun kujera yana mai
fuskantarta,fuskarsa kunshe da walwala,ya ce.
"Kin tashi lafiya?" Ta kawar da kai tana shan
kamshi,ta ce. "Kalau". Ya dan zuba mata ido
ya
ce. "Ina fatan kin ci abinci kafin ki kwanta
wannan baccin naki,bana son zamanki da
yunwa". Ta muskuta ta kara gyarawa,wanda
hakan na bayyana hasken da zuciyarta ke yi,sai
dai ba ta son bayar da kai bori ya hau. Ga

jarabar dokin da ya ishi zuciyarta na son ganin

wannan amarya wadda ta buzuz ta fi ta kima. A

yangance ta dubi kwayar idonsa ta ce. "Wai fita

zaka yi ne?" Yana yi mata wani tsadadden kallo

ya ce. "Eh,uwargida ran gid,ko in zauna akwai

abin da za ki ba ni?" Ta yi saurin girgiza kai. "

A'a sauka lafiya,wai ba zaka gabatar da mu ga

juna ba ne a wajen amayar taka?" Ba tare da

ya

ba wa maganarta muhimmanci ba, ya ce. "Har

sai na gabatar da ku ga juna sadiya,sai ka ce

wasu yara? Ku gabatar da kanku ga juna

mana,ta zo wajenku ko ku uje inda ta ke". Ta

dube shi da gefn ido,ta ce. " Kawai kuma a

matsayina na babba sai na zubar da girmanan

na

shiga wajenta ko? Ya tuntsure da dariya ya ce.

"Sadiya ke nan uwar son girma. To wallahi ta

girme ki, ko wannan kika duba kya ba ta girma".

Fuskarta ta cika da walwala ta ce. "Oh tsohuwa

ka kwaso mana ke nan?

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.33) Ya gyada kai ya kuma girgiza, ya ce. "

Idan kin ganta idonki ya kwashe miki". Ya mikamata hannu alamar ta zo gare shi,yana cewa. "Wai ba zamu gaisa ba ne?" Ma'ana ya basar da wancan zancen. Ta kawar da kai ranta na kara haske,tana kada idanuwa ta ce. "Ai na sallamawa amarya,idan kwana ukunta sun cika ka kara mata wata daya a nawa". Ya iso gare ta yana girgiza kai. "Ba zan iya maraicin rashinki ba". Ya jima suna faranta ran juna,sannan ya yi

mata sallama ya nufi dakin hindatu. Yana shiga kicin dinta ya wuce ya barta a falo ya kinkimo fulas da kofi ya zo ya zauna tana faman binsa da

kallo,ya ce. "To tashi da sauri mana ki kawo min mahadi,kina ganin zan makara". Murmushi kawai

ta yi,ta mike zuwa kicin ta zubo masa wainar shinkafar da ta yi da kyakkyawar miyar albasa,sannan ta kawo masa kayan shayi, sai da ta hada masa komai sannan ta koma gefe tana cewa. "Abu Turab ai ban yi tsammanin zaka fita aiki yau ba. Haba zaka ragewa amaryarka daraja,

a kawo ta jiya kuma yau ka barta ka fita aiki".

Ya

fara taimakon cikinsa yana cewa. "Aljihuna ne

babu ko karfanfana dole sai na fita,ko

akwai'yan

kudi a wajenki ki sam min aro?" Ta yi saurin

girgiza kai,ta ce. "Ba ka dai kyauta ba. Ai ya

kamata ka yi tanadi tun jiya". Bai dube ta

ba,ya

amsa. "Za a kori gaba". Takawar da kanta daga

gare shi,ta ce. "Me ye sunanta?" Takawar da

kanta daga gare shi,ta ce. "Me ye sunanta?" Ya

dan zuba mata ido,sannan ya amsa "Sunanta

fadimatu,don Allah anjima ki yi kokarin lekawa

dakinta ku gaisa,kar ki duba komai,ki duba ni

da

na ce ki je din kin ji". Ita ma ta dan kafa masa

ido sannan ta kawar gami da ajiyar zuciya,ta

ce.

"Anya ba ka dora min babban aiki ba kuwa Abu

Turab? Me yasa ita ba ka yi mata izinin ta biyo

mu dakunanmu mu gaisa ba?" Ya girgiza kai, ya

ce. "Na fa ce kar ki duba komai". Sai kawai ta

tsaya tana kallonsa yana ta faman cin

abincinsa,dama shi mutum ne mara wasa da

cikinsa. Can ta nisa ta ce masa. "Wai amaryar

ba

ta yi girki ba ne,to ita me zata ci?" Ba tare da

ya

dube ta ba, ya ce. "Yanzu zan fita na nemo

mata". Sai ta ji maganar na yi mata yawo a rai.

A gidan Abdullahi za a ki dora tukunya,kuma a

fita waje a siyo,kuma wai shi ne ma da

kansa,anya? Ta dai share har ya gama ya yi

mata sallama ya fice,can ta ji tashib motarsa

bai

fi mintuna ashirin ba ya dawo. Da sauri suka hau

lekensa daga ita har sadiya wadda ta ke son

sanin abin da ya dawo da shi,yayin da Hindatu

ke

dokin ta ga kalar abincin da za a tarbi amarya

da

shi. Mai masa share sharen harabar gida ya biyo

shi da manyan kwalayen sunfi a kirga sun fi

kala

goma dangin kayan sha,tsotse tsotse da tande

tande,shi kuma abdullahi na rike da ledoji biyu

na

take away mai tambarin wani shahararren

restaurant. Sai da Ayuba ya gama shigowa da

kayan kofar dakin amarya ya fita,sa nan

Abdullahi ya fara kwankwasa mata kofa. Wani

tokareren bakin abu ya tokarewa safiya a kahon

zuci,kamar ta hadiyi zuciya ta mutu,Hindatu

da

sauri ta saki labile zuciyarta na wani irin

bugawa.tunda ta ke ba ta taba jin zafin kishin

Abu Turab irin na ranar yau ba,duk da kuwa Abu

turab tuni ya bayyanar mata sadiya ce mai

kyallin goshi. Cikin magagin bacci fatima ta ji

bugun kofarsa,da sauri ta bude idonta ta dubi

agogo,sai ta tarar sha daya har ta gota, nan

take

kalamansa suka fado mata. "........ Da safe

kuma

ko ba ranar girkin ba ne zan dinga shigowa mu

gaisa......" Ta ture bargo ta dau hijabinta ta

zira

kirjinta sai harbawa ya ke, saboda fargabae irin

cin kashin da ya kunso mata mata a wannan

shigowar, tunda shi dai ya zama annoba, duk

haduwa sa ya gadar mata bakin ciki

3 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

34) Sai da ta yi ta gwada irin yadda zata

daure fuska da kuma kalaman da zata iya

fansar

kanta idan ya nemi raina mata hankali,sannan

ta

bude masa kofar,ta koma makwancinta ta

zauna

tana cin magani bayan ta lullube kafarta da

bargo. Sai da ya gama shiga da kayan nan a

kicin dinta tsab, sannan ya kitsa da ledar take

away din, ya ajiye bisa coffe table fuskarsa a

daure ya fara nazarin falom da shiwadda ko

kayanta na jiya ba ta cire ba ga kuma shaidar a

falon ta kwana. Sai daya gama nazarinta tsab

cikin sassaucin murya ya ce. "Kin tashi lafiya?"

Ta kada kwadar ido da kawar da kalba tare da

ta

tanka ba. Ya ci gaba da kallonta wasu irin

abubuwa na huda zuciyarsa juriyarsa na shanye

su. Ya bata murya ya ce. "Ga kayan kwalam din

da kika ce min sun ishe ki sati biyun da kike

zatarwa kanki a gidan nan,idan akwai wani abu

da kike muradi sai ki sanar da ni,wannan kuma

karin kumallo ne na yanzu (yana nuna mata

take

away din) bai kamata na je gidanku na ci abinci

mai kyau ke a nawa ya gagara ba". Ta daga a wulakance ta dube shi ta ce, "Nawa ka kashe na biya ka? Ai ba mu shiryo ta zaka yi wata wahala da ni ba". Tana rufe baki ya amsa mata. "Ni ne kawai na shiryowa kaina a wani gefen kuma don na nuna miki kudin kawai kika fi ni,amma na ki da

shugabanci daga indallah". Takre ya bayana a fuskarta. "Wa kake shugabanta.....?" Ya tare ta

da gadara. "Ke!!!!" Ta kada kai tana cije lebe,ta

ce. "Ai na fi karfinka abdul ya ya zaka yi da ni?"

Nan ma bai yi kasa a gwiwa ba ya amsa. "Yadda namiji yake da ko wacce mace musamman jarumi

irina me jarumtar kashi da ta zuciya..... Ni sam ban taba yarda wata mace ta fi karfin namiji ba duk irin kasaitarta...." Ta motsa baki kamar zata

yi tsaki,sai ta hadiye shi,Nan take kanta ya fara

ciwo saboda tsabar takaici,ta dafe goshi kawai. Zai kuma dorawa ta dago ta kalle shi rai a

bace,ta ce. "Abdul wannan hayagagar taka ta

ishe ni, idan ka gama abin da ya kawoka ka fice

min,kuma daga yau bana bukatar gaisuwarka da

bankwananka.Na yarda ba zan fita ba sai da

izininka, sai dai ba zan taba neman izinin naka

ba

ma'ana ba zan fitan ba har wa'adin mu ya cika

mu rabu kowa ya huta,isa kuma na yarda ka isa

ai ga alama nan tsurut da kai ka ajiye mata

biyu

kana shirin ta uku ko wannan aka suba sai a

sara

maka....." Kuncinsa kunshe da murmushi ya

tare

ta. "Kin zare kanki daga ciki ne?" "Kin zare

kanki

daga cikih ne?" Ta yi fuska,ta ce. "Ai dama ba

a

ciki nake ba". Ya yi mata wani kallon mai tarin

fassarori wanda ita kanta duk hikimarta ta kasa

ba shi ma'ana.ya jima yana jan fasali sannan

ya

kada kai,ya ce. "Akwai amanarki a tare da

ni,wanda shugabancinki a yanzu ya jaza

min,saboda haka dole na shigo na miki

bankwana

kuma na ga yadda kika kwana...." Sai ta yi masa

shiru ranta na kara daci,ya jima tsaye yana

kallonta ta rasa yadda zata yi da shi,ta san

neman abin da zai bakanta mata kawai ya

ke,kuma ba zai samu ba don ba zata dinga biye

masa yana sa mata ciwon kai ba. Hai kuwa

bayan ya gama kare mata kallon sai ya bita da

kulli. "Wai a nan kika kwana ne? Duk me ya yi

zafi?" Ko motsi ba ta yi ba bare alamar zata

tanka,sai ya kada kai ya juya. "Sai ki tashi

haka,ki yi wanka ki dan gyara gurin kara a yi

baki

su yi miki kallon kazama ki daga bakin kura".

Haba wasu hawaye masu radadi suka tunludo

mata,ba ta iya hadiyewa sai da ta ce. "Abdul

aniyarka ta bi ka". Ko a jikinsa don yana

dariya

ya fice,ta dafe kai a wajen tana maimaita.

"Innalillahi wa inna illahi raji'un" Ta yi

kukanta ya

ishe ta, sannan ta bai wa kanta hakuri ta tashi

ta

gyara falon,sannan ta fada wanka a gurguje

don

ta dan fara jin hayaniya a cikin gidan. Ta
shirya
da shigar turawa,ruwan kasar wando wanda ya
fito da kirarta da farar vest saboda zafin da ke
gari duk da na'urar sanyaya daki ta wadata a
gidan,amma ji ta ke komai ya yi mata nauyi da
zafi,kamar yadda zuciyarta ta ke.. Ta saki
ranta
ta kwashi abinci don ta tabbatar babu ruwan
abdullahi da abin da yunwa gauraye da bacin rai
za su haifar mata,ita kadai wannan asarar
data
shafa. Cikin kayan da ya zube mata a kicin ta
tarar da abin da ta fiye so,wato yellow peach. Ta
balle gwangwani biyu a faranti ta koma falo
zamanta ke da wuya aka kwankwasa mata kofar
falo,haba gabanta ya yi mummunan faduwa
don
ta yi tsammanin dan hayaniyarta ne, tunda
tasan'yan gidansu babu mai zuwa mata a
wannan ranar. Sai da ta leke ta tagar kicin ta
ga
wasu bakin mata biyu sannan hankalinta ya dan
kwanta,sai da ta koma mazauninta ta zauna ta
dauki farantin peach dinta ta tsiro da cokali ta

kai baki sannan ta yi izinin a shigo. Sadiya da Hibdatu ne, an kullo tsegumi an taho,amma daga tsomo kafarsu numfashinsu ya so ya dauke saboda haduwar falon,sai wani kamshi da sanyi mai rahama ke dukan mutum. A kasaice kamar yadda ya zame mata dabi'a ta ce. "Ku shigo". Sadiya dai don da kunya ne ace ta koma amma tana dora ido akan fatima sai ta ji gaba daya falon ya fara zagaywa da ita.amarya Abu Turab ke nan? Sadiya da gama tsinkewa don tasan mijinta dama can ba sauki,bare ya sami wannan 'yar mai kama da gwal. Ko hindatu ta ji babu dadi game da amaryar Abu turab ba zai wuce na kasaita da rashin kulawarta ba, sai kuma ledojin abincin da ke gabanta wanda a arharsa da matsayin resturant din da aka siyo shi ya haura duba uku.kudin cefane su na kwana biyu a karin kumallon mace daya! Turkashi! Da gaske matsayin mace biyu ta ke amsawa... Ko ma ta haura. Su suka yiwa kansu wajen zama suna mai fuskartarta,sannan ta sami damar matsawa a yangance ta ce. "Ina kwananku?" Hindatu ce ta yi

kokarin amsawa da murya a bude,amma sadiya

kusan a ciki ta amsa ta kuma kasa sake daga ido

ta dubi fatima. Sai da fatima ta ci peach yanka

biyu sannan ta dire faranti ta mike cikin yauki

tana cewa "Bari na kawo muku ruwa". Da sauri

hindatu ta ce. "A'a mu fa yan gida ne ba sai

kin

ba mu komai ba". Ba tare da fatima ta dakata

ba,

ta ce

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

35) "To'yan gida ba za a karrama ku ba, ina

zuwa". Ta zuba lemon mangwaro biyu a dogon

farnti,yellow peach biyu da sosa ruwa faro da

tambulan biyu da kuma choculate cake guda

biyu. Ta kawo musu ta ja wa kowace coffee table

a ganata,ta bude musu lemo,sannan ta zazzage

musu peach ta yi musu bismillah,sannan ta koma

nata muhallin. Ko kallon kayan sadiya ba ta yi

ba, sai Hindatu ce ta dauki lemon ta kurba

sannan ta dube ta ta ce. "Abu Turab ne ya

zubar

da ladansa bai gabatar da mu ga juna ba, shi ne

muka yi karambanin zuwa inda kike tunda ke ba
ki nemo mu ba. Ga yaya babba ( ta nuna sadiya)
ita uwargidanki,sai ni Hindatu na bi bayanta. A
kasaice fatima ta juyo ta dube su, da dokin ta
ga
matan da suka fita.ta yi tsaki a zuci kawai ta
kawar da kai,haushinsu kuma ya kara turnuke
mata zuciya,daman tunda ya ce matansa sun fi
ta taji gaba daya ta tasne su, ashe ma burgar
banza ce ko kama kafarta ba su yi ba, duk da shi
ya ce ba a nan ta ke ba. To amma abu a duhu
wa zai dorar? Da kyar ta hadiye tsanar da ta yi
musu ta amsa batun da suka zo mata da shi a
hagunce. "Wane ne kuma kuma abu turab
Kamar
a kufule sadiya ta ce. "Angonki!" Fatima ta
kawar
da kai tana kara hadiye takaicinta, kamar dole
ta
ce. "Au,ban sanshi da wannan sunan ba".
"Amma
ba ku dade tare ba?" Tamabayar da sadiya ta yi
mata ke nan,ita kuma sai ta juyo kawai tana
kallonta tana ta faman kuma sai ta juyo
kokawa

da zuciyarta wadda ke karanta,don ta buge da
kai
peach a baki ta taune ta hadiye,sannan ta dubi
talabijin ta ce. "Ba ki da labari ke nan?" A dan
zafafe sadiya ta ce. "Kusan haka ne, don an yi
abin ne cikin gaggawa kinga zan iya tsammanin
akwai wani 'yar burum burum". Duk da fatima
ba
ta iya bakar magana ba,sai ta ji yau kamar an
kimsa mata,don sadiya na rufe baki ta amsa.
"To
ko ma dai odiyo diyo ne ya fice wai tunda ya
zama dahir,ko a mafarki dai muka hadu
haduwar
ta yi amfani tunda mun auri juna,auren da na
tabbar a yanzu ya fice gaibu. Sadiya ta fara
murmushin da ya fitar da sauti,ta ce. "Dama ga
abu turab da aure aure,shi har kwallon kafa
aura
yake jiya raba dare ya yi yana kallon kwallo,na
yi
mamakin yadda kika saki wannan damar".
Maganar ta daki zuciyar fatima,amana nan da
nan sai ta fanshe. "Babu wani abin mamaki
akan

aurensa don in dai namiji bai yi sa'ar auren

farko

ba to ya gama garari,ba kwallon kafa ba har

kwallon ciki ma wataran sai ki ga ya aura,abin

da

kuma zai fi saukin yi min ciwo ke nan,wato akan

gazarwa da zan janyo a cika min gida da

kishiyoyi". Sadiya ta yi masifar kuluwa tamkar

ba

ita ta fara zunguro fitinar ba,bacin ranta ya

kasa

boyuwa tana numfarshi ta ce. "Wata kishiyar ai

suna ta tara,kishiyar da zata yi asarar daren

farko ai maraba da ita. Wallahi ni a kawo min

dozen ma" Numfashin fatima ya yi kamar ya

dauke saboda takaici,ta rasa amsar da zata ba

wa sadiya ta fashe,sai gaba daya ta tsani kanta

ta kara tsanar Abdullahi,wannan babu tantama

shi ya janyo mata wannan koma bayan da ya ce

sai ta tare a gidansa

2 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

36) Ta dinga gyada kai tsawon

lokaci,sannan ta ajiye numfashi ta dubi

Hindatu,ta ce. "Ita ta gabatar min da kanta,ke kin

yi shiru ko rakiya kika yi mata?" Hindatu ta bude

ido ta ce. "A kan me? Igiyarta daban tawa daban,

don duk abin da ta fada ita kadai ta sanshi,don ni

ban san shi ba.... Ni umarni na bi,don maigidan

ya ce na zo mu gaisa,na kuma sauke nauyi......"

Fatima ta cije lebe cikin girgiza kai ta tare ta.

"Kwarai kin sauke nauyi,ina kuma godiya ba tare

da na hakkake taki gabatarwar ba tunda tare na

ganku.... Ni ban shigo gidan nan don wata ta

dinga zuwa tana min haushi ba saboda duk fadin

dangima babu karnuka......" "To mun gode". Abin

da hindatu ta ce ke nan, kuma salin'anlin ta shi

da lemonta a hannu ta fice,sai sadiya ma ta ke

mata baya bayan ta saki katon tsaki tana habaice

habaice. Fatima ta bi su da kallo kanta na wani

irin ciwo saboda bacin rai,yau fa ake yinta,rana

zafi inuwa kuna,auren sati biyu mijin babu dadi

matansa babu dadi,ita zara'u ina ta tsoma

ranta?

*********** *********** ********* Karfe

biyar

abdullahi ya dawo gidansa ya zauna a falonsa

da

gajiya yana kallon wasan kwallo cikin rabe

hankali,fiye ma da uku. Amarya fatima ta debi

kason mutum biyu,kwallaon kafa daya,ga kuma

iyayen gida wadanda mintuna talatin ke nan

da

shigowarsa babu wadda ta shigo masa ko sannu

bare ta taushe shi game da radadin gajiyar

zuciya

da ta jikin da ya kwaso. Ya gaji ya fara kiran

wayar sadiya amma har sau uku tana kin

dagawa,sai ya haura ya kira hindau,ita kuma

tana

dagawa don rainin hankali sai cewa ta yi. "

Lafiya?" Takaici ya rufe shi,a zafafe ya ce.

"Wacce banzar tambaya ce wannan hindatu?

Kuna jina na dawo amma don raini a rasa me

bullowa ta gaishe ni?" Kawai sai ta kashe wayar tana tsaki. Ashe ya ji ta, ya sauke wayar cike da mamakin mata, mata fa shaidanu ne, kalau fa ya

bar su,amma yanzu ya je ya dawo duk sun wani birkice masa,wai ma har hindatu da yake da garantin ba ta salwantar da mutuncinsa da kimarsa. Sai ya ji gaba daya ransa ya kara mugun baci,kawai sai ya tashi ya sa wa kofarsa makulli don ma kar wata ta yi gigin kwaso kafa ta zo masa ya sauke mata nasa rashin mutumcin,don gaba daya haushinsu yake ji. Ya tara lemuka masu sanyi a gabansa,idan ya dure wannan gwangwani ya dauki wannan yana kallon

wasan kwallo wai duk don zuciyarsa ta sami sanyi,amma kamar turi don ba abin da ta ke muradi ke nan ba. Fatima ta ke son gani,amma babu wani dalili na ganinta a yanzu,idan ba yana

son karyawa kansa tsari wanda Zai iya rushe masa wata katanga a cikin ginin da ya yi nisa a cikinsa ba. Haka ya dinga daurewa har daba da magriba ya yi wanka ya shirya cikin kananan kaya wadanda suka fito da kuruciyarsa

fili,tana

kuma matukar yi masda kyau,ya fes turaren

five

eleven sannan ya kullo kofa ya fice masallaci.

Sai

da ya sallaci isha'I sannan ya nemi gida dauke

da take away din amarya,zuxiyarsa cike da

sakar

yadda za su bullowa juna yau. Yana shiga ya yi

karo da sadiya a tsakar gidan wanda babu

dalilin

ganinta a tsakar gidan a wannan lokaci,yasan

kwannan zancen,ta fito ne kawai don ta sanya

masa ido kawai ta sami abin yi masa korafi su

hau rigima. Ya share kamar bai san Allah ya

tsire

ba,idanunta kan ledar hannunsa ya shiga

kwankwasa kofar fatima. Ya shafe fiye da

mintina

goma yana bugun kofar ba tare da jin a ransa

zai

gajiya ba idan ya shafe sama da awa daya yana

yi. Can sai gata ta zo ta bude tana sanye da

after

dress,fuskarta na bayyana shirin ko ta

kwana,ta

koma baya zuwa tsakiyar dakin tana sauraron

karasowarsa. Ta gama zuwa wuya ba zata yarda

Abdullahi ya jona mata ciwon zuciya babu dalili

ba. Ya karaso ya ajiye ledar kan table sannan

ya

zuba mata ido,tun ma kafin ya yi magana ta

riga

shi. "Ka ga malam! Matukar rashin arziki ka

kwaso ka shigo min ka juya da takunka,don ni

ma na shaki kamarsa ina ji kum a raina ba zata

yi mana kyau ba....." Ya dan yi galala yana

kallonta cikin murmushi,sannan ya taussa

harshe

ya ce. "A'a,arzikin na kwaso,ba ni hanya na

wuce,amma ke ma ki shaki irinsa". Ta yarfe

hannu ta wuce kujera ta zauna tana tsaki,ya

kara

rage nisan da ke tsakaninsu idanunsa a

kanta,sai

huci ta ke kamar wadda ya kashewa dan fari. Ya

dora kafa kan table yana ci gaba da kare mata

kallo,sannan cikin muryar zolaya ya ce. " Sannu

2 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.37) Ta kada ido ta kawar da kai, ya kuma zungurota da sassaukar murya. "Ki daina fushi fatima,sam ba ya yi miki kyau wallahi..... Ina ganin kamar ba ki saba ba......" Nan da nan ta kara cika,ta ce. "Ai na ga wadanda fushin ke yiwa

kyau wadanda babu tantama ka dace da su sun dace da kai.idan kana na ka muzguna min,idan ba ka nan ka turo min wakilai,sai dai na yi mamaki da ba ka hada wannan kwangilar da su ba,ko kuwa kyashin ba su ba nasu kason kake? Na ga suna yi min gorin asarar daren farko alhalin dama can na gaibu ne...... Ya ji kamar ta

dabawa zuciyarsa adda,wato rashin mutumci su sadiya suka zo suka yi mata? Ya ji ciwon abin fiye da duk wani bacin rai da ya riske shi a 'yan watannin da suka shude,sai dai juriyarsa ta hanawa fuskarsa bayyanawa,amma muryarsa a sanyaye ya amsa. "Ni ban turo kowa ba,duk kuma abin da wani ya yi ra'ayin kansa ne ba nawa ba......in kuma kishi ne ya sa ki fadar hakan,to ki tuna.babu wani dalili da zai sa ki yi kishin matana". Sanyin muryarsa ya sa ta dan

dube shi a tsanake,sannan ta kawar da kai ba

tare da ta tsira da wani abu a cikin kallon nasa

ba. "Ba na bukatar ka yarda da ni,don haka ba

zan yi kokari goge duk wani fenti da zuciyarka

ta

kagi goga min ba. Amma kishin matanka Allah ya

tsare ni,sai dai abin da nake musu ya fi kishi,

domin kuwa ba na kaunarsu,na kuma raina

musu

wayo fiye da yadda kuka raina nawa kai da su.

Ya kara tausasa murya ya ce. "Yanzu don Allah

me ya kawo wannan maganar? Ko don kawai na

yi raddi ki ce na miki rashin arziki?" A kufule

ta

amsa. "Idan ma zaka yi rashin arzikin ai na

shirya masa.... Kai ban ki ba fa a ce a yau na

bar

gidan nan ba, domin DUHUNSA ya fara munan a

idona". Ba tare da wata shakka ba, ya ce. "Ga

shi

kuma kin yi masa shiga sojan badakkare". Ta

yunkuro a birkice ta ce. "Me kake nufi?" Da

karfin

gwiwa ya share tambayar tata, cikin kara

kyautata murya ya ce. "Ya ya kadaici? Na damu

da yawa da kadaicin da nake hasashen kin wuni
cikinsa,sai komai ya gundure ni a office na
matsu
na zama abokin dauke kewa gare ki ko da hakan
na nufin ba zan miki abin burgewa ba". Ta yi
sukuti kirjinta na bugawa tun kafin ta shirya,ta
kalubalance shi. "Wannan dogon zancen naka
yana bukatar tambihi a nawa lissafin,in hali
fito
fili ka wanye min domin in dorar da na fahimce
ka". Ya girgiza kai cikin dariya. "Duk abin da
zan
furta a matsayin tambihi ba zai canza da wanda
kika bukaci na fassara miki ba don ni ne din dai
ba canja ni aka yi ba". Da ta rasa abin ce masa
kawai sai ta nuna masa kofa,ta ce. "Idan ka
gama abin da ya kawo ka, ka fita Allah ya tsahe
mu kalau". Ya dan jima yana nazari,sannan ya
murza yatsu ya juya ya fice yana cewa. "Ga
abincinki nan. ******************
***************
Dare da wuni suka dinga dauki dai dai har suka
samar da lissafin da za a kira kwanaki bakwai
na
kwanan fatima a gidan Abdullahi. Sai dai yadda

al'amura ke faruwa a gidan sun zarce akiyasta

su,musamman a ma'auni irin na

ZUCIYA,zuciyar

ma irin ta fatima da Abdullahi wadanda

dukkansu

abubuwa masu girma ke yiwa kudirinsu.baraz

ana.

Fatima dai tana yiwa nata kallon sauki, domin

gab ta ke da cimma buri idan mai duka ya

rayata

sati daya a gaba,kawu dai ba zai dafata ba

kuma

ba zai la'ance ta ba idan mai afkuwa ta riga ta

afku.,matsalar ta daya shi ne, banjin da aka

samu

tare da Abdullahi,daga wani kungurmin makiyi

zuwa wani mai sadaukar da komai a kanta ko da

kuwa bakin tsanyarsa bai mutu ba. Abdullahi ba

ya yiwa nasa kudirin kallon matsala wadda zata

dada jarumi da kasa,amma a zahirance

jarumtar

tasa ce kawai ta kaga hakan domin shi kadai ne

tilonsa ba shi da mai goyon baya,kuma yana

yunkurin ne a inda ba a san yana yi ba,

hasalima

ba a damu da yunkurin nasa ba, sannan a gefe
ga
ma sa ido da sana'ar korafi da hakkinsu ko
babu.
Cikin sati dayan nan da za a kira abdaullahi
gwauro to zai iya amsawa,domin ko wacce ta
zare wukarta akansa. Don me? Kwanakin fatima
uku wanda shari'a ta ba ta a matsayinrta na
bazawara ba su sauya da kwana dayan da ya
karantu ba. Ba ta cas ba ta as,sai dai Abdullahi
ya shigo mata da abinci daga waje ba na kudi
kadan ba, banda kyayyakin kwadayi iri iri hatta
ruwan sha ba ya ma dosarta da pure water sai
dai na roba, kuma ko baki tayi abin da zasu ci ke
nan. Ranar da sadiya ta karbi girki,washegari
da
safe ta jangwalo masa fitina yana shirin fita
aiki,
ya fita siyowa fatima karin kumallo bayan ya
hantse ke nan da girki sadiya,ya dawo da
abincin
ya kai wa fatima dakinta suka yi dan fadan
nasu
da ya zame masu jiki ya nufi dakinsa ya kara
kintsawa sai jin hayaniyar sadiya ya yi kuma a

bangaren fatima. Haba da sauri ya fito sai yaga

fatima tsaye a barandar kofar dakinta sanye

da

hijab ga kuma sadiya rike da zandameniyar

tsintsiya tana hayaniya. Ya tsaya daga tasa

barandar yana rike da jakar lap top dinsa

fuskarsa

babu yabo babu fallasa ya ce. "Me ya faru?"

Zuciya a kule sadiya ta hau koro masa jawabi.

"Wai ita wannan ba aure ta zo gidan nan ba ne

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.38) Ni ban ga wani abu daya da ta ke ko ake

mata wanda zai sanya a kirata matar aure ba".

Bai ko motsa ba ya tari numfashin ta a dake " Oh

wannan tambayar kika kira ta ki yi mata ke

nana?" Cikin nufin tura haushi sadiya ta ce. Allah

ya tsare,kai ma da kake kwanan kallon kwallon

kafa a honey days dinta ba ka ga asarar bata

bakinka ka yi mata wannan tambayar ba bare

ni.... Maganar sharar tsakar gidan na nake

mata,kasan nura ya je auye,kwana dai dai muke

ni da hindatu..... Ita kuma na ga kamar cin abinci

kawai ta zo yi,to mu ba bayin ta ba ne, sai ta

shigo a yi da ita. Ya dinga nazarin sadiya,idanunsa da fuskarsa na bayyan tarin bacin rai da suka riska,ya yi gyaran murya ya ce. "Yau ne za ta fara sharar?" Cikin gadara ta gyada kai,shi kuma ya ajiye jakarsa ya nufo ta yana mika hannu. "Ba ni tsintsinyar duk ranar tata sharar a dinga tuna min ina sharewa. Ta kankame tsintsiyar tana kallonsa da yanayin takaici,ta ce, "Abin da ya kamata ka ce mi ke nan?" Ya tsuke ido ya ce mata. "Dama mun yi ajandar fadin kamata tsakanina da ke?" Ta yi saroro kunnya ma rufe ta saboda ta san halin Abdullahi,babu ruwansa sai ya tsinkata gaban fatima da ta rungume hannu ta zuba musu ido Sadiya ta yi dira dira ta ce. "Ka ga ni bana son bakar magana". Nan ma ya tsare ta da ido,ya ce. "Amma kika nema?" Kamar zata saki kuka,ta ce, "To bayanta zaka bi ke nan?" Ya kada kafada alamar ko in kula,ya ce. "Ke ce za ki fada,tunda watakila kin yi zaton naki bayan zan bi, sai kuma aka sami akasin haka..... Ba ni tsintsiyar na ce". Ta mika masa tana shirin barin wajen,ta ce. "Lallai aikin shara ya dawo hannunla don kuwa ni ma bazan kara saka tsintsiya a tsakar gidan nan ba, kullum sai ka dinga sharewa. Tana direwa ya

amsa. "Ashe? Ga shi kuma ke ba cin abinci kawai kika zo yi gidan ba,wanne za ki zaba ke nan? Idan kin zaba sai ki fada min Allah basshi yau na yi kwannan kallon kwallo da safe na share miki gida". Takaici ya lullube sadiya ta ma rasa da kalamar da zata amsa,kawai sai ta wuce ta barshi tana jinsa ya saukaka murya ya cewa fatima. "Yi hakuri don Allah,shiga ciki. Ya nade riga ya share gidan tas inda ya tsallake barandar sadiya da Hindatu,ya share ta fatima sannan ya wanke hannu ya fice abinsa. Kwana biyu da suka biyo baya bai share gida ba,amma yana ware barandar fatima ya share, ba tare da ya damu da manya da kanana kalubalen da yake fuskanta daga sadiya ba kai har ma da Hindatu da a yanzu ta fara ganin kamar makancewarsa ta yi yawa duk kuwa da iyakarsa ke nan da dare raba makwanci suke. Kai sai abin ma ya bar tsakar gida, kwananta biyar ya lura komai ya yi kura a falon fatima,sam bai zarge ta da kazanta ba don yasan ba ta saba ba.Abin da ta sani kawai ta wanke goma ta tsoma biyar,don haka ranar lahadi da safe da ya je gaishe ta sai da ya tabbatar ya goge komai tsab sannan ya yi mata kyakkyawar shara tana zaune tana

kallonsa,sannan ya fice. Wannan dabi'ar tasa ta son bauta mata ba tare da neman raddi ba, wani lokacin ma yana yi suna fada,ta taimaka kwarai wajen zaba tare fiye da rabin tsatsarsa a zuciyar fatima. Ta fara bude ido ta kalli kalarsa,kyakkya wan matashi mai akida,wanda ba ya taba sakaci ko sarayar da hakki ko damar sa ko a wajen da yake da kason kaskantar da kai. Sai fadan da suke yawan yi ya fara birgeta. Ta kuma fara nazartarsa a matsayin na sabo kawai ba wanda ake yi a doron kiyayyar da ta ratsa zuciya ba, shi yasa hankalinta ya kwanta kamar tsumma a randa,ko yaushe suka yi waya da Alh ta kan tabbatar masa ai Abdullahi na aiki mai kyau,ya dauke ta kamar 'yar uwarsa. Matsalarta daya su sadiya,wanda motsi kadan sai ta kwashi damin habaici da dalili ko babu,wannan ya kara mata tsanar su musamman sadiya,wadda ta lura kamar numfashinta ma neman masifa da gori ne. Dadinta daya idan Abdullahi na kusa wanda kan ari rigimar ya yafa ko da kuwa gorin zai fada kansa. Ranar lahadi girki ya zagayo kanta,a ranar ne kuma sam ba ta ji duriyar Abdullahi ba tunda ya yi mata gyaran falo ya fice bai shigo mata bankwana ba dare duk da ta ji shigowarsa gidan

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.39) Ga mamakin sai ta ji ciwon hakan ko saboda gorin sadiya.to mai gorin rashin kwanansu a dakin juna ina kuma ya dauke mata kafa kwata kwata? Da safe da ya shigo kawo mata karin kumallo bai gabatar mata uzuri ba, ita ma ba ta nema ba,duk da ba ta so hakan ba saboda neman tsira da mutumci a idon sadiya a ragowar kwanakinta a gidan. Daga wannan rana kuma sai hakan ya zame masa dabi'a,illa da yamma idan ya dawo ya kan shigo ya kawo mata abinci kusan kamar akan kaya sai ya fita,ko fadan ma ba ya saurararta su yi. Kwana sha biyu girki ya kuma waiwayarta,tana ta dokin. Dawowar Abdullahi saboda wunin da ta yi da yunwa saboda ta yi bakin kawayenta. A ranar kuma ba ta da sha'awar wani abu da ya danganci gwangwani. Karfe biyar ta ji shigowar abdullahi gidan,ammahar shidda bai waiwayeta ba, cikin kuncin kanta da jona ruwa a kettle don ta sha tea. Tana tsaye tana jirab tafasar ruwan ne Abdullahi ya cimmata a kicin din cikin kannana kaya da kamshin turare. Tana ganinsa ta baka

fuska,ko sallamarsa a kicin ta amsa bai damu ba ya dora. Me kike yi?" Ta share shi, cikin zolaya ya ce. "Yauwa abinci za ki mana?" Kawai sai ta kashe butar ta zare cable ta nemi ficewa daga kicin din,shi kuma ya babbake kofar yana kokarin su hada ido. "To me ye na fushin don Allah? Ni ban ga laifin da na yi ba". Ya fada da murya mai karancin sauti,wadda kuma ana yinta ne masoyin da aka kadaice. "Wata alfarma na zo nema". Ya kuma fada yana kara kaskantar da murya. Ta yi baya rungume da hannu tana kallonsa duk ta takura,kasancewar ba ta sanye da hijabi, don tun shigowarta gidan bai taba katarin ganinta haka ba, hasalima kanta ko kallabi babu sai kwantaccen bakin gashinta da ta makale da ribon. Shirunta ya ba shi damar karanto alfarmar. "Don girman Allah ki zo mu je gadon kaya ki gaida su hajiya,ba ki ji fadan da malam ya yi min ba yau akan hakan,har yana ganin ko don babu rana mahaifiyata ne sa na ki kai ki ki ga yan'uwa". Har yau ta kasa dauke ido a kansa,fuskarta ba ta bayyana rashin kunya ba, illa ta bayyana damuwa kamar a raunane ta ce. "Wacce irin rigima ce wannan abdul,bisa wacce fuskar zaka kwaso min fita da kai?" Ya kawar da

kai,ya marariraice mata. "Ki yi hakuri,kin san sha'anin iyaye,sai ka kansace mai taka tsan tsan a cikin lamarinsu don ka samu ku rabu kalau.... Kuma ya kamata mu yiwa malam uzuri tunda bai san me ye akwai a tsakaninmu ba... To banda abinki ma waye zazai yarda mun fita taren? Idan Alh ne sai kar ki sanar da shi a waya alal akalla dai ai ba ki taimaka na ma mahaifina ba don ban taba yi miki irin abin da ya yi min wannan sakayyar ba" Ta dan yi rau rau da ido,amma sai ta hada ta motsa,ta ce. " Ban hanya na wuce". Ya ba ta hanyar na wuce". Ya ba ta hanyar, sai da ta jima a falo sanyaye ya bita jiki a sanyaye.ya same ta sanye da hijabi ta rafka tagumi. Ya kara kan kan da murya,ya ce. "Ki daure muje fadimatu". Ta janye tagumin,ta ce. "Zan je,amma kai ma ka yi kokari salin'alin jibi ka sallme ni na bar gidannan nan". A takaice ya ce. "Toh". Sannan ya dubi agogo ya dube ta. "Tea za ki sha? Bari na hada miki ki sha sai in yi wanka ki shirya da kyau,don Allah ki binne matsalarmu a zuci kar ki bari ko kadan a san babu jituwa a tsakaninmu kin ji? In kin yi hakan ma kin gama biyana". Cikin mintuna kadan ya hada mata tea din tun a kicin ya hada komai.ya

zo mata falon da shi a kofi da choculate guda

biyu,ya ajiye a coffe table ya janyo mata har

gabanta ya yi mata kyautar murmushi,sannan ya

juya yana cewa. "Idan na dawo sallar isha sai mu

tafi". Kai tsaye masallaci ya wuce,har bayan isha.

Yana dawowa ya fece ado kamar mai zuwa zance

ya baza turare,sannan ya rufo kofarsa ko su

sadiya bai yiwa sallama ba ya nufi dakin fatima.

Ta gaji da nata kyan cikin riga da style din zanin

atamfa super milk kala mai ratsin purple da

ruwan zuma.ta gama hadawa idon Abdullahi sai

dai iyakarsa ke nan ganin da zatawa kai haduwar

tata,ko yabo ba shi da ikon ya yi balle abin da ya

fi shi. Tana ganinsa ta yi saurin shigewa daki ta

dauko mayafin da takalmi da jaka purse,ya yi

saurin shanye kallon da yake mata lokacin da ta

karso kusa da shi,muryarsa a dask [truncated by WhatsApp]

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.40) Ko gezau ba ta yi ba, sai dai ta saci kallon

kofar dakin,sannan ta mayar da hankali ga

nazartar gidan. Ya kayatu kwarai,ya sha adon

furanni ko'ina,ga shi makeken gaske saboda

yanayi shirunsa kamar babu kowa a cikinsa,sai

karar A.C ko'ina. Sai da suka bi wani korida

sannan suka fita harabar gidan,tana binsa a

baya

har wajen motarsa ya bude mata kofa ta

shiga,sannan ya zagaya ya shiga ya tashi motar

suka fice waje, sannan ya tsaya ya fito ya rufe

garkamemiyar kofar gidan da key. A sannu

yake

tafiya da motar bayan gilasai da ya rufe

kirif,ya

kunna A.C, ga kamshin airfreshner da ke motar

ya gauraye da kamshin turarukan jikinsu ya

hadu

ya ya zama samfurin wani kamshin daban.

Motar

ta yi dif! Kowa zuciyarsa na na zarin,hakurin

Abdullahi dai ya fara zarce awon da ya mallaka,

kusancinsa da fatima ya dinga buga masa zuciya

yana kuma kore masa duk wani tashin hankali

da

zai iya samun kansa a ciki. Ya dinga satar

kallonta yana kallon titi.A karshe sai ya mika

hannu ya latsa sautin D.bany a wakarsa ta Fall

in

love. Fatima ta kara yin dif! Ko motsin kirki ba

ta

son yi.zuciyarsa ta kasa nutsuwa don ta

tabbatar

Abdullahi na nufin wasu abubuwa masu tsauri a

kanta,abin da yake ba za ataba kiransa plan

ba,na gaske ne kuma ba yau ya soma ba tunda

ya tsiro da aure.to amma da wanne KWANJIN

zata kalubalance shi,mutun mai fuska biyu

irinsa?

Sai kawai ta zabi yin bakam ta manne jikin

kofar

motar,tare da alkawarin anyi na farko anyi na

karshe. Har suka je salon wakokin da yake sa wa

ke nan,daga fall in love ya fada,no one like u,

ya

zarce I'm in love, duk ta shanye ta yi banza da

shi. Da ya tsayar da motar kofar gidan ma sai

ya

ki bude mata kofar ta ja mabudin ta saki ta

dube

shi,lokacin da ya kife kai a sitiyarin,a kufule ta

ce. "To ka bude ni mana!" "Ya dago a gajiye ya

dube ta,ya ce. "Oh ba zaki barni na nutsu ba ke

nan?" Sai ta kasa magana,tsawon fiye da

mintuna goma sannan ya gaji ya dago ya dube

ta. "Ki yi kokari don Allah ki toshe duk wata

barakar da zata nuna ba kya sona fatima,ina so

su ganki a mace mai ilmi da tasan abin da ta ke,

ki daure ki ba ni wannan alfarmar domin

ubangijin

da ya halicceki". Kai tsaye ta amsa mas. "Na

ji,amma sauti,idan ba haka ba wallahi babu

wata

alfarmar da zaka kuma neman a wajena na yi

maka,ko da kuwa zata shafe ni" Ya hadiye

dariyarsa ya ce. "Don dai in tsargu ne,amma ni

ba

ke na sa wa ba, bari na bude miki kofar". Ya

balle kofar sannan ya fito ya bude mata, ta

fito

ya rufe kofar sannan ya yafuceta suka zagaya

ta

wata hanyar daban saboda cikar da kofar gidan

nasu ya yi da masu daukar karatu

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

41) Iyakar karamcin yau fatima ta je gidansa

babba da yaro kowa na farin ciki da zuwanta.

Waje waje Abdullahi ya dinga kai ta yana

gabatar

mata da masu wajen,matan malam

uku,haj.zainab,haj Anisa da haj umma,ko

wacce

ta karrama su kwarai,turamen atamfa da

turaruka. Haka ya kai ta wajen matan

yayyensa

wadanda ke nasa bangare su ma suka dinga

karram ta. A nan ne ya shiga kiran kannensa

yana gabatar mata su ita kuma tana yabawa da

matukar karamci babu ta inda ta bude kofar sai

suka dinga yi mata kallon mace mai kirk matuka

da son mutane. Kai har dakin da ya yi

samartakarsa sai da ya nuna mata,sannan ya

nuna mata dakin mahaifiyarsa wanda yanzu

kannensa mata suka gaje ya ce. "Kin ga dakin.

Innata,shekararta biyu da rasuwa". Har cikin

zuciyarta ta tausaya masa yayin da kalamanta

suka cika da alhini. "Allah sarki,Allah ya ji

kanta,ya sada ta da annabin rahma". Idonsa

kwal

kwal ya amsa mata,"Amin har karfe goma suna

gidan,sam Abdullahi ya tsani a tafi saboda ya

sami damar mu'amala da fatima da kare mata

kallo,bai kum ataba sanin tana da fara'a

kamar

haka ba. Muryarta sassanya mai dadin

sauraro,kalamanta a takaice masu azanci da

sanyaya rai,ga ta da karrama mutum ta hanyar

ambaton sunansa a duk maganar da zata fada

masa,shi kansa ba ta sanya shi akwandon shara

ba, idan magana ta biyo ta kansa ta kan ce,

"Abdull kaza. Karfe goma da kwata suna dakin

kannensa. Mata ana hira ta dube shi ta ce.

"Abdul mu tafi dare ya yi". Ba shi da wani zabi

duk da ransa bai so hakan ba, suka yi sallama da

kowa wani jikan gidan Adamu ya rako su da

kayan fatima har mota. Sun fara tafiya kun

kun

kun kamar dazu sai dai yanzu babu D.banj

tunda

ta yi hani da wannan. Da kanta ta kawar da

shirun da ke tsakaninsu ta hanyar wani raddi

da

ta ke fatan ranar samuwarsa. "Abdul kulliyar

jama'ar gidanku suna da kirki da son

farantawa

dan Adam ba kamar kai ba". Ya dauke wuta

kamar bai ji ba,sai can ya muskuta ba tare da

ya

dubeta ba,ya ce. "Yarinyar ni na rufe shafin

rigima da ke" Kamar ba zata tanka ba,sai kuma

ta tanka din. "Haka ne,gara mu yi rabuwar

arziki,mu sami kafar zumunci ko?" Tana

kallonsa

kai tsaye shi kuma nasa kallon a titi,bai tanka

ba

amma kuncinsa cike da murmushi. Ya dinga

tukin

cikin matukar kasala kamar masu tafiya a

keken

da babu birki,can ya kira sunanta a kasalce.ta yi

dif, takaici na isarta. "Fadima wallahi ba ni da

lafiya". Ya fito fili ya fada mata.ta kuma

share

shi, sai ya kuma shagwabewa. "Da gaske nake

fadimatu,kirjina bugawa yake, taba ki ji".

Cikin

tsuke ido ta fuskance shi.42) Abdul ka mayar da ahankalinka,babu irin

wannan a tsakaninmu sai ka bari mu isa gida

akwai wadanda zasu iya daukar alhakinsa. Bai

sami damar bata amsa ba wayarta ta shiga ruri

sai ya bata damar ta amsa alhalin dukkan

hankalinsa na kanta don yana tsammanin kiran

alhaji ne. Ilai kuwa ita ma ta amsa ba tare da

wata shakka ba,sukayi gaisuwa irinta

masoya,sannan yace mata ina kika shigane ina

ta

faman kiran wayarki baki daga ba,ta danja

fasali

sannan ta amsa ina falo ne wayar na cikin daki

yace mata.wlh har nashiga damuwa fati,nayi

tsammanin ko kun hada kai da abdul. Kinsan

kuwa dazu gani ga abdullahi agidan mai

yashareni?sai yayi kamar bai ganni ba alhalin

mun hada ido.fatima ko kin bashi dama ne ya

shigo dakinki har yasan wacece ke?Da sauri ta

dubi abdul, wanda take da yakinin zai iy jin

abin

da alhajin ke fada,ta daura maballin rage sauti

sannan ta canja wayar zuwa kunneta na dama

murya na rawa tace..kai haba kila dai bai ganka

bane kawai amma har yau bai saba dangantakar

da ke tsakannmu ba,nakanyi kwana biyu ma ban

sa shi a ido ba.alhajin ya saki ajiyar zuciya yace

to allah yasa ya dore nidai na karaya ko jiya

doctor ya tabbatar min B.P dina ya kai 160,cikin

tausayawa matuka tace Ayya alhaji ka kwantar

da

hankalinka, inshaa allah nan da kwana biyu

mun

fara lissafin rayuwa tare,ya kyalkyale da

dariya

yace inshaa allah,bari ba barki ki huta sai da

safe, Ta sauke waya anutse kuma tayi

fuska,harsukaje gida babu wanda ya tanka

wani,fuskar abdul.ta murde kamr wanda aka

aikowa sakon mutuwa ,sai huci kawai

yake,hakan

bai hanashi rakata dakinta da kyaututtukan da

ta

samo ba,sai dai baice mata kala ba yafice inda

tabi shi da kallo tana mamakin wannan

sauyawar

tasa. Dasafe ma karfe takwas haka ya shigo

mata babu walwala da ledarsa mai hawaye zaki

ahannu,ta bude masa kofa bai ko dubi inda

take

ba ya wuce ya jona ruwa akettle ya fasa kwai

guda uku yasoya ya rufe afaranti.yajuye ruwan

zafi afulas ya jero mata adogon faranti cup da

sauran kayantea,ya dora bread sannan ya ajye

kan center table.muryarsa a cushe

yace,breakfast

is ready, baijira cewarta ba ya kada kai ya

fice,tabi shi da kallo cikin tunanuwa iri iri,gaba

daya zuciyarta ta jagule,me yayi zafi haka?

Haka

ta wuni zuciyar babu dadi gashi ranar ko kare

bai

shigo mata ba bare ya dauke mata kewa,wannan

damuwar ta sabbaba mata dokin ganin jibi

domin

ta sami barin wannan gidan da maabotansa suke

ajuye,daga masiffafu sarakan gori sai

shugabansu

tufkar hagu .

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

zuciya d kwanji

43) Sai dai duk da haka aranta bata so suyi

rabuwar tsiya da abdul ba.ta fara sabo da

shi,kuma ta yarda da batun mahaifinsa yana

da

kirki da tausayi ga diya mace da son ya

kyuatata

mata.To ita ma zata dorar da wannan duk da

rashin matsayinta agurinsa bai kware mata baya

ba.tana mamakin yadda damuwar yau ta ke

saurin sanyata kuka,Dazarar ta zurfafa

atunani

kawai sai taji hawaye. Da laasar sakaliya tana

kwance dakin baccinta tana kanana hawaye,ta

jiyo abin da aka saba,wato hindatu da

bakuwarta

suna gulmarta.tunda tazo gidan hindatu bata

taba

tararta gaba da gaba da wata magana mai daci

ba amma sau uku kenan tana zuwa mata jikin

windo da baki suna gulmarta,yau ma ga

gulmar.bakuwar tace kwatakwata wannan

amaryar taki ba a ganinta ne?hindatu ta mele

baki tace.ina zaki ganta?bata fitowa sai ta rako

baki jiya dai ya kwasheta sunje gadon kaya,ina

jin iyayenta suka kai ma malam kara,akayi

kiransu akayi musu fada,ko kaca kaca malam

yayi masa oho!Don yau a wani hagunce ya tashi

daga magana ya hau surfa min balai wai na

barshi yaji da abin dake gabansa,cike da son jin

tsegumin bakuwar tace.Oh me yayi zafi haka?

hindatu na daria ta amsa.hum in kika ji labarin

sai mamaki ya dameki,kinga matar ne?

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

44) "Hum in kika ji labarin sai mamaki ya dame k-n kinga matar ne? Wanke hannu ka taba
wallahi kyakkywar mace iyakar saninki. Amma Abu Turab shakulatin bangaro yake da ita,kallo ba ta ishe shi ba, ko girki fa ba ta yi kullum safiya ranar girkin ta.wajena yake cin abinci,da
dare kuma shi yasan inda yake ci. Ita kuma ya fita waje ya siyo mata saboda tsabar daurewa karya gindi...." Bakuwar ta ce. "Allah mai iko,yaya ran sadiya?" 'E kinga yadda ta yakune?
Nasan kuma lamarin matar nan ke ramar da ita.ga kudin ga kyau,ga kuma tsabar mulki. Ga sadiya da bakin kishi,yau da safe ai a kanta ya sauke fushin bayan ni na kama kaina. Tana fa ganinsa a birkicen nan wai ta hau tuhumarsa,wai
jiya ya fita da amarayarsa bai fada mana ba. Kin
san Abu Turab da bakar magana,kawai sai ya nemi guri ya zauna rai a bace ya yanko mai zafi ya ce. "To kinga sadiya tun da ke kika auro ni kike kuma daukar nauyina zo ki kafa min

padlock

kar na dinga fita da ita,sai na nemi izininki,ai

duk

ke kike ciyar da mu...." Kin santa ita ma da

dacin

rai,sai kawai ta ara ta yafa ta ce. 'Kamar

gaske,idan kana sonta me yasa ka mayar da ita

'yar gadin dakinka tana fada kuka wuni da

kwana....' Babu shiri fatima ta fice daga dakin

baccinta zuwa falo don ta gaji da wadannan

bakaken maganganun kar ta ji abin da zai balla

mata zucita,ashe kallon da suke mata

wulakancinsa har ya kai haka? Cikin wannan

radadin zuciyar ta yi wanka ta kasance cikin

pink

din kananan kaya,siket din iyakar gwiwa da riga

matsattsiya ko cibiya ba ta rufe mata ba. Ta

kishingida a kujeru tana kallo duk da

hankalinta

ba ya tare da abin da ta ke kallo. Biyar da kwata

ta ji dirin motar Abdullahi,ta dubi agogo

gabanta

na faduwa saboda tunanin yadda suka kwashe

yau da safe. Sam ba ta yi tsammanin shigowarsa

a wannan lokacin ba, don haka ba ta damu da

kayan da ke jikinta ba, amma kwatsam sai ga

shi

kuma ya sami majigin kallo duk da fuskarsa

babu

walwala. Ta kawar da kai tana faman jan siket

sannan ta ja riga,a karshe ta dube shi a

turbune

ta ce. "Haba malam,mene ne haka babu daukar

dama?" Ya dage gira ya ce. "A'a,kaddara ma

barance na zo". Sai ya share wannan batun,ya

nemi guri ya zauna karo na farko ke nan da ya

zauna a dakin tunda ta zo gidan,komai ya kawo

shi iyakarsa tsaiwa. Muryar a saukake ya ce. "Ba

ni da kudi sosai ne zan shiga kicin,me kike so na

girki miki?" Har zata gwale shi,sai ta tuno dan

bikin da Hindatu ta gama yi mata dazu,kawai

sai

ta kawar dakai,ta ce. "Ni 'yar cirani ko me ka ba

ni ai godiya zan yi in karba,yau da gobe ne

kawai,

jibi ya zama tarihi". Ya hadiye duk takaicin da

maganarta ta sabbaba masa,ya ce. "To za ki ci

dan wake? Sai ki hada da fruit salad". Duk da

ba

ta san ya ya dan waken yake ba sai ta kada kai

ta ce. "Zan ci" Ya ce,"to bari na dan huta". Ya kara share guri ya zauan,idonsa akan talabijin amma a saukake ita yake more kallo.ta gama sakwarkwata zuciyarsa da yi masa fami a soyayyarsa wadda yake ji a ransa ba ta shafi kyau ko iya wankanta ba. Cikin dabara ta silale daki,sai ga ta ta fito sanye da after dress suka dubi idanunwan juna kai tsaye ya tura mata wani

sako,ta karba amma sai ta zubar har da tare gira,sai ya fito kai tsaye ya fada mata. "Da dazun

da yanzu ba ki canja a idona ba". Ta kara bata rai,ta ce. "Wasa ka ke,amma ni dai nasan na canja tunda ga shi har bakinka ya bude...." Tana

rufe baki,ya magantu. "Zan yi tambaya. Ganin da

na yi miki babu wannan after dress da matsala ko

babu? Wai idan muka kalli hakan ta fuskar addini

da kuma al'adar bahaushe". Ta jima tana jan fasali sannan ta ce. "Ni ba diyar malamai ba ce,kuma ban karanta Hausa da al'adu ba" Ya

kada kai,ya ce. "Ni na ji a raina a duk

bangarorin

biyu,wato addinin da al'adarta babu matsala.

Abin da kuma azancina ya kasa fassarawa shi

ne,ban ji kin canja idona da zuciyata ba, a

ganin

da na yi miki dazu da na yanzu da ma duk

wanda

na sha yi miki a baya tun kafin aurenmu,ko ke

za

ki iya fassarawa?" Kai tsaye ta amsa masa

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji .45) "Manta matsayin da ka ba

ni kawai ka yi,

wanda shi ne dalilin da ya sa ba na canjawa a

idonka,ko ka manta ne?" Ya yi saurin taren

numfashinta. "Ban manta ba... Amma ina

cigiyar

wanda ya taba ba wa wani ko wata irin matsayin

da na ba ki don ya wayar min da kai akan abin

da irin wannan matsayin ke nufi" Ta yi

sugudi,sannan ta ce. "Yanzu ka koma

zaurance,idan zaka iya fassara min sai lurarmu

ta dore,idan ba zaka iya ba mu diga aya ka

shiga

kicin dinka". Ya yi murmushi har kumatunsa

suka

lotsa,ya ce. "Na fada miki duk abin da kika ki a

bakina da fassararsu suka fito,amma wannan

bari

in gwada ko zan iya fahimtar da ke. Da ace

maganar soyayya zata iya giftawa tsakaninmu,

ina karrama matsayinki da karramawar da ta

zarce wadda masoya kan ba wa juna. Ga shi

kuma ban tava wani amini ba bare na hasaso

matsayin da na ba shi.... Kinga duk wannan

'yan

kace nace da muke? Ina jin kololuwan

muhimmancinki a zuciyata. Sai ta yi masa dif!

Har ya gaji da kiran cewarta ya ce. "Kin kulle

tattaunawar tamu ke nan? Cikin rashin kula ta

ce. "Kwarai,saboda ba ta da wani amfani da

zata

yi mana". Ya kada kai ya mike yana cewa. "Ke

ce

kike ganin haka, amma ni da kwakwalkwata ta fi

ta ki kaifi nasan ribar da tattaunawar ke ba

ni".

Bai jita cewarta ba ya fice,ya wuce kai tsaye

kicin

din Hindatu, duk abin da zai bukata game da

danwake a can ya debo,Hindati na kallonsa

kamar

zata yi magana ganin irin fuskar da ya yi sai ta

watsar da shi. Ya kai kayan kicin din

fatima.sannan ya koma dakinsa ya sanyo

singileti da wando three quater ya koma kicin

din.

Karaf sai idonsa akan wayoyin fatima biyu akan

fridge.Haba cikin zafin nama ya kwashe su ya

kashe si daya bayan daya.sannan ya tura su a

aljihu,yana mai hamdala ga Ubangiji,sannan a

fili

aljihu,yana mai hamdala ga Ubangiji,sannan a

fili

ya ce. " Ke da su har abada". Cikin zafin

naman

nishadi ya dinga aikinsa yana rera wakarsa ta

fall

in love duk ya cika mata kunne da zuciya. Yana

daba da kammalawa ya yi bako Hindatu da

kanta

ta shiga dakin fatima domin sanar da shi, ta

sami

fatima kishingide,ga Abu Turab na rero wakar no one like u daga kicin. Hindatu ta kulle a yangance

ta nuno mata kicin,ta ce. "Yana ciki,don Allah karasa ki sanar da shi". Hindatu ta same shi kace

kace cikin aiki yana zuba dan wake a warmer yana koda waka da rawa,a gefe ga kayan marmarinsa ya wanke. Yana ganin Hindatu ya dake ya maze kamar ba shi ba,ya hade rai ya ce. "Lafiya?" Ta hadiye wani kududun takaici,ta ce.

"Muftahu ne ya zo wai yana ta kiran wayarka ba

ka dauka ba". Ya kasa hada ido da ita,ya ce. "Eh,

na bar wayoyin a daki,mu je". Ya ajiye cokali suka fito kicin din tare, ya dan daga murya ya ce.

"Don Allah zahra'u taso ki karasa". Ta dan juyo a

kaikaice,babu kunya babu tsaoron Allah ta ce. "Kasan Allah? Sai dai ka dawo ka sami girkinka yadda ka bar shi,babu abin da zan yi". Shi ma kuma ya shanye ko kadan ya ki ganin laifinta.

Da

saurin murya ya ce. "Kin ga Hindatu fadawa

muftau ya ba ni mintuna goma ina zuwa". Bai

jira

cewarta ba ya koma kicin din,/urguje ya hada

kan

kan aikinsa,ba tare da ya hada fruit salad din

ba

ya tura kayan marmain a fridge ya gyara kicin

din

ya fito yana ce wa fatima. "Ki yi min hakuri

zuwa

bayan sallar isha na zo na karasa. Babu damuwa

ko?" Ta tabe baki ta kada kai,shi kuma ya fice.

A

falonsa ya tara da muftahu da su

Hindatu,muftahu na ganinsa ya hau yi masa

shakiyanci. "A'a ka ga zakaran kukun shekarar

2012". Dariya kawai Abdullahi ya yi ya shige

dakinsa ya watsa wayoyin fatima a durowa ya

kulle,sannan ya zira jallabiya ya fita wajen

muftahu

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

.Zuciya d kwanji

46) Sadiya ta dinga yi masa wani kallo,kamar mai shirin tashi ta shake shi,Hindatu kanta a yau

irin kallon da ta ke masa ke nan, tana ma shakkar anya shi din ne? Ko ya gansu fuskarsa ba ta nuna damuwa ba. Ya mikawa muftahu hannu suka gaida,sai muftahu ya ki sakin hannu

nasa yana cewa. "A'ah!" Abdullahi ya fizge hannunsa ya zauna ya ce. "Kai dallah malam manta wannan maganar". A tunzure sadiya ta ce

"Babu maganar ladatarwa,ni ma ga nawa girkin can yana jiranka". Muftahu na dariya ya ce. "Shekarar 2012" "Na karba". Abin da abdullahi ya

ce ke nan, ya kuma canza wata hirar inda ya hau

tambayar muftahu game da saurensa da za a yi kwanan nan. Muftahu ya ce. "Kai aure da wuya Abu Turab,wallahi kamar na daga auren nan,ku ne auren ba ya muku wahala kake samun 'ya'yan

dattijai,kasan na yi mamaki wannan auren naka?

Ban taba zaton a gidan 'yan boko ana karbar sadaki kawai a bashi aure ba. Sadiya da ta ke a wuya ta tare numfashinsa. " To ba gara wanda za a cajeka sosai a barka da KWANJINKA ba, yanzu don Allah ina amfanin abin da Abu Turab yake? Shi ke nan kullum a hanyar gidan abinci idan ba haka ba ya daura zani ya shiga kicin.... Kasan Allah Abu turab da wasa na kamaka kana mata girki ranar girkina sai mun yi tashin hankali

da kai?" Budar bakinsa sai cewa ya yi. "To sai dai kar a kuma". Muftahu na murmushi ya ce.

"Ba a yin haka Abu turab,ai duk matsayinsu daya

a gurinka..." Abdullahi ya tari numfashinsa,ya ce.

"Babu ruwanka muftahu,ban tauyewa kowaccensu

hakkinta ba, saboda haka babu ruwansu da dangantaka da wata ko naman jikina ta ke yanka.wai kowa ba da halinsa zaka zauna da shi ba, yanzu ke ba hakuri nake da halin kaifin harshen ki ba, ke kuma kullum kafarki a waje". Wannan karon Hindatu ce ta shiga maganar.

"A'a

Abu turab, maganar ka barni unguwa fa

daban,maganar ka zama bawan wataina ganin

daban". A fadace ya ce da ita. "To duk ba sai

ku

yi abin da zaku yi ba" Da muftahi ya ga lamarin

zai kwabe sai ya shiga tsakani suka shiga wata

hirar daban.sai da ya fara shirin fita sannan

muftahun ya ce. "To ba zaka kirata mu gaisa

ba?" Abdullahi ya ce. "Ka kyle wannan yarinyar

muftahu,'yar rigima ce". Cikin tsura masa ido

muftahu ya ce. "Don Allah wai ba ta son auren

ne? Ya girgiza kai ya ce. "Ko daya, akwai wata

a

kasa ne?" Cikin zulumi muftahu ya ce. "Kana

ganin manya ba zasu shigo maganar nan ba Abu

turab? Wannan rayuwar fa ba zata dore ba,

mace

ba zata shiga kicin ta girka abin da zata ci ba

ma

bare kai ta baka,sannan kai ba wani amfana

kake

da ita ba...." Abdullahi ya yi fuska,ya ce. "Ya

ya

zaka ajiye min wadannan kunnuwan kana yi

min

irin wadannan maganganun? Baka san mata ba ne rantse,sam ba a iyar musu.in ce fatima ba ta soma su yi mitar na tsaya tana wulakanta ni, in ce in kadai nake sonta su ce abin da nake. Fice hankali ko na hada da nasu hakkin... Don Allah mu share wannan maganar zaka yi mamaki wata rana." "Allah ya kai mu" Muftahu ya yanke zancen,Abdullahi ya ce. "Jira na yi wanka sai mu
fita masallaci tare". Ya shige toilet ya bar muftahu da su sadiya suna yi masa gutsiri tsoma. Sai bayan sallar isha'I ya komawa fatima,ya karasa abin da ya rage ya shirya mata
kan darduma a falo inda ta ke kwance tana kallo.

Ya zauna a kujera yana dubanta. "Fatima kin taba
cin danwake kuwa?" Ba tare da ta dube shi ba ta
girgiza kai, ta ce. "Ina dai jin sunansa". Ya ce,"to
bari na zubo miki,Allah ya sa ki iya ci". Bai jira cewarta ba, ita ma ba ta tanka ba ya zubo mata wanda ya tabbatar ya fi katfin cikinta ko da ta

iya cin dan waken. Ya kawo gabanta ya ajiye, ya

janyo tum tum ya zauna a gaban nata. Ta dan

harare shi,sannan ta harari abincin ta ce. "Ni

ba

yanzu zan ci ba". A tausashe ya ce. "Don Allah

daure ki ci fati,kinga idan ba ki iya ci ba sai na

nemar miki wani abincin". Tsawon mintuna biyu

sannan ta yunkura ta tashi ta janyo tasar

abincin,ta tsirawa danwaken ido,sannan ta

daga

kai ta dube shi ta ce. "Haka yake shi kuma?" Ya

kada mata kai. "Eh,ci ki ji". Ta dauki fork ta

kai

daya bakinta tana juya shi a hankali.ba zata

iya

cewa da dadi ko babu ba saboda rashin sabo.ta

kuma mayar da cokali yasar Abdullahi na

kallonta

har ta kai loma biyar,ya ce,Abdullahi na

kallonta

har ta kai loma biyyr,ya ce. "Za ki iya? Ba tare

da ta dube shi ba ta kada kai. Cikin dakewa ta

dube shi ba ta kada kai.

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

.Zuciya d kwanji

47) Cikin dakewa ta dube shi ba ta kada kai.

Cikin dakewa ya dauki cokali ya saka a kwanon

nata, A tausashe ya ce. "To bari na tayaki ci".

Ta

bata rai ta bata fuska sosai,sai dai ba ta tanka

ba, kuma ba ta fasa cin abincin ba. Falon ya yi

tsit,a nutse suke cin abincin,shi yake

dawainiyar

zuba mata lemo da ruwa har suka cinye dan

waken.ya zyra mata ido ya ce. "Ya isa?" Ta

kada

kai tana janye jikinta gefe,ya zuba mata fruit

salad din ya mika mata,sannan ya kwashe

kwanukan zuwa kicin.ya dawo ya dafa kujera ya

dan sunkuya,ya ce. "Ina tafi?" Ta rufe ido ta

bude

ta dube shi,ta ce. "Ya yi mata wani dunkulallen

kallo gami da murmushi sannan a sanyaye ya ce.

"To sai da safe". Ta kokarta ta amsa. "Allah ya

tashe mu lafiya". Ya dan tsura mata

ido,sannan

ya juya ya fice. Ta sauke kai daga kallonsa,sai

ta

ji kewarsa ta darsu a ranta.ta fara ji a jikinta

Abdullahi ya samar da shakuwa a tsakaninta da shi,wanda sam ba ta so hakan ba, kuma tabbas yanayin bautar da Abu daya ke kuntata mata game da shi,shi ne yadda ta ke jin shakkarsa a duk wani abu da ya hado da shi,ko motsinsa ta ji

sai gabanta ya fadi,shi yasa lokuta da dama ba ta iya ja 'in ja da shi,sau tari karfin hali kawai take yi ta ke taya shi su yi fada,amma tsoron kaifin bakinsa ta ke, wanda yanzu ta fahimci dabi'arsa ke nan. Yau da safe da yake cikar nan

yana batsewa ba karamin buguwa zuciyarta ta yi ba, shin kuwa akwai mutumin da ya taba samun irin wannan matsain a rayuwarta? Ta nemi wayoyinta babu,ba ta zargi komai a ranta ba, da zummar duk lokacin da aka kirata zata gansu,amma har lokacin bacci babu labari, duk da haka sai ta share ta yi kwanciyarta.

Abdullahi

kuwa raba dare ya yi yana bude asiran wayarta, musamman inbox da sent msg,in da ya gano tsantsar so da kaunar da Alh ke mata,da kuma haukan kyautar da yake mata. Nata raddin ba ya

wuce godiya da nuna tana kewarsa. A logs dinta

ma, kiran Alh ya mamaye wayoyin,wanda suke

bata mintuna har da awa akai. Duk sai ran

Abdullahi ya jagule,wani garwashin kishi ya

dinga

babbaka masa kirji tare da yiwa Alh kallon wani

dan ta'adda a soyayya,tare da cewa bai fi shi

son

fatima ba, illa kawai ya fi shi sakaci da samun

dama a cikin soyayyarta. Ranar da kyr ya

runtsa

don kunan zuciya, bayan ya yi flashing

layukanta,ya yiwa wayoyin boyo na musamman.

Washegari da duku duku bayan ya dawo

masallaci ya kwankwasa mata kofa,ta zo ta bude

cikin yanayin me barci.ya dube ta a nutse ya ce.

"Kin yi sallah?" Ta gyada masa kai,bai ja

magana

a tsaninsu ba, ya ce. "Zan miki karin kumallo ne

saboda in son fit da wuri". Ta ba shi hanya ya

wuce kicin,ita kuma ta sake fecewa dakin bacci

har da murza key sai farkawa ta yi ta tarar da

abinci a falo.

1 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.48)Sannan falon a gyare tsab,kicin ma

haka,wanke wanke ne kawai Abdullahi ba ya yi.

Sai da ta yi wanka ta shirya,ta karya kumallo

sannan ta saka dambar neman wayoyinta.

Wasa!

Har sha biyu tana fama ita da kanta ta fara

zargin an dauki wayoyin,to wa zai dauka? Daga

jiya zuwa yau ba ta yi baki ba, kuma babu mai

shigowa dakinta sai Abdullahi,shi ma iyakarsa

falo wanda shi din ma jiya kawai zata dorar ya

sauya mazauni ya zauna. Sai gabanta ya fadi

da

ta tuno da wayoyin jiya ta barsu a kicin... Babu

tantama shi zai dauki wayaoyin.to bisa wanne

dalilin? Sai hoton bacin ran da ya shiga ranar

da

ta amsa wayar Alh saboda tsabar karfin hali. Ta

wuni da tanadin bala'I iri iri na taron

Abdul,aka yi

rashin sa'a ta shiga alwarlar sallar magariba ya

shigo kawo mata abinci,bai kuma yi jiran

fitowarta ba ya fice saboda sadiya mai girkin ta

kafa ta tsare. Har karfe tara babu labarinsa,ta

gama tanadin bala'inta har ya nemi fin

karfinta,abincinsa kuwa ko kallonsa ba ta yi ba.

Karfe goma ta gota,ta kuma gama zuwa wuya kawai sai ta zira hijabi da silifas ta tunkari dakinsa. Lokacin yana tare da sadiya da Hindatu wadanda suka balle littafin korafi,shi kuma yana biye musu har suna kirarin bar masa gida. Cikin su uku babu wanda cikinsa bai kada ba lokacin da fatima ta kwankwasa kofar falon,shi ya yi zargin fati ce,to da me ta zo? Sadiya ta razana sosai,amma da Hindatu ta ce. "Ko waccan matar ce?" Sai sadiyar ta wartsake,kufule ta ce. "Shigo". Fatima na huci ta tura kofar ta shiga,sai ga Abdullahi zaune wanda da ya kishingida hankali kwance Fatima ba da mu da kallon da kowa a falon ya zubo mata ido ba, musamman abdullahi wanda gaba daya ya tsargu,wato tun ma kafin ya ji abin da ta zo da shi. Ta dan tsaya daga nesa tana kare masa kallo,ta ce. "Abdul ina wayoyina?" Muryarsa na rawa ya ce. "Wayoyinki fadima? Ba ki gansu ba ne?" Ta dakatar da shi

da shakkiyar muryar da ta koshi da bacin rai.

"Abdul kar ka raina min wayo don Allah, kawai ka

ba ni wayoyina". Kamar su kadai a falon,gaba daya Abdullahi ya ras nutsuwarsa.A rikice ya karaso gabanta da muryar tausasawa,ya ce.

"Fatima maida hankalinki mana,me ye yake damunki haka?" Tana bude baki zata yi magana ya yi saurin rufe bakinta da hannusa,sannan ya ja

hannunta da sauri suka nufi kofa,da ta fara turjewa ma kawai sai ya dauketa cak! Ya nufi dakinta har da murza keu sannan ya ajiye ta akan kujera ya durkusa gabanta yana rike da hannayenta cikin tarin gabanta yana rike da hannayenta cikin tarin damuwa,ya ce. "Me ye haka fatima? Ya ya zaki nemi tona mana asiri a wajen da za a yi mana dariya alhalin Muna zamanmu lafiya ba tare da wani yasan tsakaninmu ba? Da nata hucin bacin ran ta ce.

"To wannan kusancin da ka yi min na me ye? Don me zaka durkushe a gabana haka? Sakar min

hannu". Ya girgiza mata kai yana kokarin

shigar

da idonsa cikin nata. "Abin da kika rasa ke

nan,

shi yasa kike son fitinata da zafin kai. Ga shi na

ji

na gani bana son damuwarki.haba fatima me ya

yi zafi?" Ta nemi kwace hannunta ta kas,nema

yake ma ya fice haka,sai kawai ta sallama tare

da zafafa murya,ta ce. "Ban gane abin da na

rasa

ke nan ba..." Ya kuma tare ta da tasa muryar

mai

kama da rada. ". Haka na ce,ba ki san rashin

kunsaci da masoyi yana mayar da mutum

masifaffen karfi da yaji ba tare da an ankara

ba?

Kadaici ya yi miki yawa fatima,ina son nuna

jarumta wajen abotakar gangar jikinki. Ba

ruhinki

kawai ba nake faman dawainiya da shi ba.....

Ina

ganin hakan zai sanyaya zafin kanki". Ranta

ya yi

mugun baci,ga shi ba ta da matakin dauka

domin

ya kanainayeta!habarsa akan gwiwarta ya kuma

matse tafular hannunsu da juna.... Ita da ta kwashi masifa da neman 'yanci ga abin da ya fi'yanci ta zungurowa kanta. Hawaye ya fara biyo kuncinta,ya bude baki yana mata kallon mamaki kamar bai san me ke akwai ba,ya ce. "To wannan hawayen na me ye?" Ta ce,"na wannan rungumar da kake min ne. Bisa wacce alakar zaka dinga hada jikink da nawa?" Kai tsaye ya magantu. "Kin duk duniya babu wanda ya isa ya hada jikinsa da naki bai zama abin tir ba,duk kuwa da fuskar da kika dubi aurenmu". "Ni maganar wayoyina nake maka ba maganar wani aure ba,kai ma ai kasan auren da yadda aka kullo shi babu kuma wanda ya isawarware wannan kullin..." Ta fada a gajiye,shi kuma ya dora cikin karsashi. "An hado da kudirorin zuciya a wancan kullin? In an hado ki fada min zan yarda abin da nake ji a raina

game da ke yau zuciyata ta haife shi..... Ta taru

numfashisa cikin sartun hawaye

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

.49) "Abdul....! Kai ka dauki wayoyina?" Ya yi

zuru kawai yana kallonta,sai can ya girgiza kai

yana murza tafin hannunta cikin nasa. Ta ga

rikici

da yawa a idanunsa,amma sai ta dauke su

kanana akan wanda ke cin wuta a cikin

zuciyarta.

Ta ladiye wani kududun bakin ciki sannan ta

dubi

tsakiyar idonsa ta ce. "Na ji ba ka dauka ba,

wayoyina ba,idan a yanzu ka yi min abin da ka

aure ni a kansa wato saki. Kwana sha hudu da

sha uku ai duk daya ne. Saboda haka sallame

ni... Sai zuciyata ta nutsu ba kai ka dauka ba".

Ba ta damu da sai ta ji amsarsa ba, kawai sai ta

kwantar da kai a majinginin kujera. Ya saki

hannunta a hankali, sannan ya koma hannun

kujerar da ta ke zaune ya sunkuya ya fara

lasar

labbanta har ya kai ga tsotsar,ko motsi ba ta yi

ba bare alamar zata hana shi,in ta gudu ina zata? In ta nuna masa karfi a matsayinta na wacce jarumar? Don kansa ya zabi saurara mata,sannan ya mike yana dan kai komo a tsakiyar falon.can ya dube ta yana rike da dunkullalen hannunsa,ya ce. "Ni na dauki wayoyin". Ta dage cikin sartun hawaye ta ce. "Abdul ina shawartarka da ka lura da zuciyarka don ba ka sa ta aiki ba, to ita zata saka ka je ina

tsumayinka gobe". Ya yi mata duba na 'yan sakanni sannan ya kada kai ya fice yana ce mata. "Godiya nake". Ta bishi da kallo har ya bace lokacin da gaba daya duniyar ta yi mata kunci da zafi. A falonsa wayam! Babu sadiya bare

Hindatu,sai ransa ya yi masa zaki matuka,don bai

ba wa kwakwalwarsa damar tanadin KWANJIN da zai karbi kalubalen sadiya ba, wadda ke takama da girki gari banza ma ina kuma ga an taba mata

shi a irin wannan lokacin? Da sauri ya garkame kofarsa don kar ta dawo.ya shige daki a gajiye ya

fada gado. Yau ya zungurowa kansa fitina,ya san
kuma ba zata jijiga shi da wasa ba ga sadiya ga Hindatu,ga kuma wadda ta ninke su a tashin hankali ta shanye,wato fatima. Da yake dama tuni ya shiryawa wannan yakin na fatima,sai jarumtarsa ta ba shi damar bacci a wannan daren, har ma ya sallaci karshensa tare da mikawa Ubangiji kokensa kamar yadda ya saba.ya kuma roki Allah ya ba shi sa'ar cinye jarrabawar da ya yi masa na jarrabarsa da matsanancin son fatima duk da hatsarin da ke tattare da nuna mata so. Da ya dawo masallaci ma sai ya kara mayar da kofar dakinsa ya rufe,har karfe tara bai motsa ba. Sadiya ma da ta
gaji tra kwaso masifarta ta biyo shi. Yana jinta ya yi lif ta karaci bugunta ta kuma shakar wai kullacin ta koma. Cikin sanda ya murgina a gado ya ce. "Duk abin da zaki yi na dadi ne'yar nan".
Har sha biyu bai motsa ba,kasancewar lahadi ce,tare da cewar ko su sadiyar bai sallama da maganar gida ba,bare ita uwar gayyar da sai ya girka ya kusa bata a baki. Kwasam sai ga kiran

wayar kawun fatima. Ya daga cikin zakuwa,suka gaisa ya ce masa. "Allah ya sa kana gida,yau na dauko momi zamu kawo muku ziyara, za mu biya wani guri nan da awa daya zamu karaso". Haba wani matsanancin farin ciki ya kulle shi, ya dinga

zubawa Allah godiya. Babu shiri ya fada wanka,cikin sanda ya fice daga gidan ya siyo musu abin motsa baki,don neman adalci sai ya hado da su sadiya,fatima kuwa dama ba ya maganarta yasan ta koshi da rikincin da ta tanadar masa. Ya dinga kwankwasa kofar sadiya

tana sharewa,sai kawai ya rabu da ita ya koma kan Hindatu don kamar akan kaya yake,tsoro yake kar fatima ta fito ta tsinka shi a tsakar gida.

Kofar hindatu a bude ta ke,yana shiga suka yi kicibus,kawai sa ya mika mata ba tare da ya tanka ba, fuskarsa kuma ababu walwala ta karba tana mamakin wannan irin mazewa. Yana fita ya

ga sadiya a kofar dakinta tana cika tana batsewa,sai ya yi kamar bai san tana yi ba,ya yi fuska ya nufeta yana cewa. "Me ya faru da

tsakar

ranar nan kika garkame kofa,kum don neman

fitina kina jina ina bugu kika share ni? Sai ta

rasa

ma abin da zata ce masa ta tsaya tana kallon

wannan karfin hali. Bai barta haka ba sai ya

mika

mata nata kason yana cewa. "Ki zo ki dan gyara

min falon can,baki zan yi. Ta karba a fusace ta

shige daki tana cewa. "Sai ka yi kiran wadda ka

kawai kwanan nawa ta zo ta gyara maka,ai ba

'yar aiki ka ajiye ba

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

50) Ya ji wani sanyi ya ratsa zuciyarsa,

wani lokacin da tagagi dadi ne da shi,yanzu

dalallabata ya yi ya yarda ya yi laifi dai ta

birkice

masa. Awa daya ba ta cika ba su kawu suka

karaso,ya sauke su a falonsa da karramawa,ya

yi

ta dawainiya da su har su momi ta kai ga

zolayarsa. " Ina zahra'un kake wannan

dawainiya

da kanka?" A ladabce ya amsa mata. "Dan baccin azahar ta kwanta,bari na tsota". Ya fice gabansa na faduwa zuwadakin fatima bakinsa cike da addu'a kamar akan kaya ta ke, sau biyu ya rankwashi kofar sai gata ta bude tana sanye da hijabi don rainin hankali har da kit. Ya dubeta samada kasa, fuskar nan tata dif! Babu alamar ta taba dariya.ta miko masa hannu,sai ya ji ma dariya.ya miko masa hannu, sai ya ji ma dariya na neman subuce masa. Kawai sai ya yi fuska ya tureta ya wuce ciki. Ya juyo ya fuskanceta yana magana kamar ba ya so. "Kinga ban shigo ba tun safe ko? Ban ji dadin jikina ba ne" Ta kyabe baki gami da gyara rikon kit din a hannunta,ta ce. "Allah ya sauwake,ina jinka". Ya share abin da ta ke nufi cikin nuna kulawa ya ce. "Kin ci wani abin?" Ta kara daure fuska,ta ce. "Idan na karasa gida na ci". Ya yi murmushi yana dan ja da baya

yana kallonta a kaikaice. "Fatima rigima ko? To anyi rashin sa'a yau gidan sun rigaki zuwan kuwa
da momi sun kawo mana ziyara suna falona".
Alamun tsoro suka bayyana a fusklarta karara,ta
jefar da kit ta dafe kirji,ta ce. "Na shiga uku,yanzu
Abdulla tona mana asirin zaka yi?" Ya yi saurin girgiza kai. "A'a fadima,Allah ne dai ya kawo su,tun wancan satin yake min maganar zasu zo. Ta sulale akan kujera a gajiye kamar wadda ta yi
gudun famfalaki.ta rafka uban tagumi tana dubansa, sai kawai hawaye ya fara shatata a idonta,ya matsa kusa da ita yana girgiza mata kai. Ya ce. "To kukan fa?" Ta fara goge hawaye wani na bullowa,ta juya hannu ta ce. "Abdul su kawu ba su iya zuwa ba, da wacce dabara zaka sallame ni na bar gidan nan a yau ba tare da sun
game me ya faru ba? Ya dinga. Yi mata kallon tsabar son kanta da bata lokacinta wajen fadin maganar da ba zata yi mata amfani ba, koda yake akan sharafinta ta ke ba ta san me ye so

ba, tunda ba ta taba dandanar zakinsa da dacinsa ba,shi yasa ta ke wasarere da irin wannan alakar da ke samar da shi.kuma kila ta yi
amanna da cewa sai ka ga dama kake so, idan ka ga hagu sai ka ki. Amma da yake an ce yaki dan zamba ne, kuma ya yi digiri a kansa sai ya bayyanar da fuskar alhini sosai yadda dul wayonta sai ta gaskata shi ya ce. "Ni ma abin da ya dame ni yanzu ke nan. Ina ganin sai dai ki kara min lokaci.... Ko kwana biyu ne...... Ki karbi girki ke nan,akwai batutuwa da nake so mu tattauna kafin ki tafi, ba zan rufe ki ba fatima ina
shakkar dalilin da yasa kike son komawa Alh ya isa ki salwantar da darajarki dominsa,ban yarda
gigin so ne ke dibarki ba,kuma bana yi miki mummunan zaton domin kudinsa kike so ki koma din.... To a amtsayina na musulmi dan uwanki ina son shawartarki kafin kafin tafi din,kin fahimce
ni?" Da sauri ta girgiza kai. "Ba na so na fahimce.
Ka,don ba na tsammanin shawarar taka zata yi

min wani amfani,koma wanne nazari ka yi akan dalilin komawata gidansa ai dalili ne.da na kudin da na soyayyar dama na wani abun daban idan ya gamsar da ni, ai shi ke nan babu abin da ya shafe ka" Ya amsa mata. "Shi ke nan,yanzu ina muka tsaya da maganar karin kwana biyun? Nan ma ta girgiza kai ta ce. "Ko kwana. Daya ba zan kara ba,idan kuwa na kara to sai ka dawo min da wayoyina". Kawai sai ya hade rai ya nufi kofa,ya kuma watsa zancen da suke a kwandon shara,ya ce. "Kin zo ku gaisa da su kawu,sanuri suke". Da sauri ta sha gabansa ta rike shi,sai dai ta kasa magana bakinta sa motsi yake. Ya dubi fuskarta ya dubi hannun da ta rike shi sannan ya kuma dubanta da shakakkiyar murya ya ce. "Ba zan jure shakar numfashinki ba,cika ni ki ban hanya na wuce". ce. "Ba zan jure shakar numfashinki ba,cika ni ki ban hanya na wuce". Ta hadiye wani tukukin takaici ko zata sami damar

maganar,amma ya gagara. Ya yi tunanin ya yi maganinta sai ya tuna su kawu da ke jiransu,kawai sai ya tureta ya wuce yana cewa. "Ya rage naki ki san da fuskar da zaki karbe su,ni
dai na yi alkwarin kina kofa ni kuma zan yaga".
Ya fice ya barta,duk da cikin rudu ta ke ba ta dauki lokacin nazarai mafita ba,da gudu ta bi bayansa tana goge hawaye,sai ya tsaya ta a hanya ya dinga goge mata hawaye da rigarsa bai damu da cewa fara ce rigar tasa ba. A karshe ya rungumeta a kirjinsa yana fada mata kalaman rarrahi. "Calm down...ki saukakawa kanki damuwa fadima,duk wannan kuncin ina zatar masa sauki, hakuri da rashinsa kadan ne fadi"....
Ya dago kanta idanuwanta a bushe. Babu alamar
hawaye... Ya kara murje fuskarta... Da hannayensa masu taushi, sannan ya ja ... Hannunta suka tafi. Da nutsuwarta ta isa ga kawu fuskarta da walwala sosai,suka gaisa sannan ta koma ga momi ta harde mata da shagwabar nuna kewa. Ta ce. "Amma dai ba wajena kuka zo ba momi, tunda kuka sauka

dakin

Abdul". Ciki jin dadi kawu ya ce. " Ni dama ba

wajenki na zo ba wallahi godiya na zo yiwa

abdullahi. Tana satar harara abdullahi ta ce.

"Da

ya yi me kawu? Bayan ya kulle ni ya hana ni

zuwa wajenku... Don Allah kawu gobe a kawo min

motata".

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

50) Ya ji wani sanyi ya ratsa zuciyarsa,

wani lokacin da tagagi dadi ne da shi,yanzu

dalallabata ya yi ya yarda ya yi laifi dai ta

birkice

masa. Awa daya ba ta cika ba su kawu suka

karaso,ya sauke su a falonsa da karramawa,ya

yi

ta dawainiya da su har su momi ta kai ga

zolayarsa. " Ina zahra'un kake wannan

dawainiya

da kanka?" A ladabce ya amsa mata. "Dan

baccin

azahar ta kwanta,bari na tsota". Ya fice

gabansa

na faduwa zuwadakin fatima bakinsa cike da addu'a kamar akan kaya ta ke, sau biyu ya rankwashi kofar sai gata ta bude tana sanye da hijabi don rainin hankali har da kit. Ya dubeta samada kasa, fuskar nan tata dif! Babu alamar ta

taba dariya.ta miko masa hannu,sai ya ji ma dariya.ya miko masa hannu, sai ya ji ma dariya na neman subuce masa. Kawai sai ya yi fuska ya tureta ya wuce ciki. Ya juyo ya fuskanceta yana magana kamar ba ya so. "Kinga ban shigo ba tun safe ko? Ban ji dadin jikina ba ne" Ta kyabe baki

gami da gyara rikon kit din a hannunta,ta ce. "Allah ya sauwake,ina jinka". Ya share abin da ta

ke nufi cikin nuna kulawa ya ce. "Kin ci wani abin?" Ta kara daure fuska,ta ce. "Idan na karasa

gida na ci". Ya yi murmushi yana dan ja da baya

yana kallonta a kaikaice. "Fatima rigima ko? To anyi rashin sa'a yau gidan sun rigaki zuwan kuwa

da momi sun kawo mana ziyara suna falona".

Alamun tsoro suka bayyana a fusklarta

karara,ta

jefar da kit ta dafe kirji,ta ce. "Na shiga

uku,yanzu

Abdulla tona mana asirin zaka yi?" Ya yi saurin

girgiza kai. "A'a fadima,Allah ne dai ya kawo

su,tun wancan satin yake min maganar zasu zo.

Ta sulale akan kujera a gajiye kamar wadda ta

yi

gudun famfalaki.ta rafka uban tagumi tana

dubansa, sai kawai hawaye ya fara shatata a

idonta,ya matsa kusa da ita yana girgiza mata

kai. Ya ce. "To kukan fa?" Ta fara goge hawaye

wani na bullowa,ta juya hannu ta ce. "Abdul su

kawu ba su iya zuwa ba, da wacce dabara zaka

sallame ni na bar gidan nan a yau ba tare da

sun

game me ya faru ba? Ya dinga. Yi mata kallon

tsabar son kanta da bata lokacinta wajen fadin

maganar da ba zata yi mata amfani ba, koda

yake akan sharafinta ta ke ba ta san me ye so

ba, tunda ba ta taba dandanar zakinsa da

dacinsa ba,shi yasa ta ke wasarere da irin

wannan alakar da ke samar da shi.kuma kila ta

yi

amanna da cewa sai ka ga dama kake so, idan
ka ga hagu sai ka ki. Amma da yake an ce yaki
dan zamba ne, kuma ya yi digiri a kansa sai ya
bayyanar da fuskar alhini sosai yadda dul
wayonta sai ta gaskata shi ya ce. "Ni ma abin da
ya dame ni yanzu ke nan. Ina ganin sai dai ki
kara min lokaci.... Ko kwana biyu ne...... Ki karbi
girki ke nan,akwai batutuwa da nake so mu
tattauna kafin ki tafi, ba zan rufe ki ba fatima
ina
shakkar dalilin da yasa kike son komawa Alh ya
isa ki salwantar da darajarki dominsa,ban
yarda
gigin so ne ke dibarki ba,kuma bana yi miki
mummunan zaton domin kudinsa kike so ki koma
din.... To a amtsayina na musulmi dan uwanki
ina son shawartarki kafin kafin tafi din,kin
fahimce
ni?" Da sauri ta girgiza kai. "Ba na so na
fahimce.
Ka,don ba na tsammanin shawarar taka zata yi
min wani amfani,koma wanne nazari ka yi akan
dalilin komawata gidansa ai dalili ne.da na
kudin
da na soyayyar dama na wani abun daban idan

ya gamsar da ni, ai shi ke nan babu abin da ya shafe ka" Ya amsa mata. "Shi ke nan,yanzu ina
muka tsaya da maganar karin kwana biyun? Nan ma ta girgiza kai ta ce. "Ko kwana. Daya ba zan kara ba,idan kuwa na kara to sai ka dawo min da
wayoyina". Kawai sai ya hade rai ya nufi kofa,ya
kuma watsa zancen da suke a kwandon shara,ya ce. "Kin zo ku gaisa da su kawu,sanuri suke". Da sauri ta sha gabansa ta rike shi,sai dai ta kasa magana bakinta sa motsi yake. Ya dubi fuskarta ya dubi hannun da ta rike shi sannan ya kuma dubanta da shakakkiyar murya ya ce. "Ba zan jure shakar numfashinki ba,cika ni ki ban hanya
na wuce". ce. "Ba zan jure shakar numfashinki ba,cika ni ki ban hanya na wuce". Ta hadiye wani
tukukin takaici ko zata sami damar maganar,amma ya gagara. Ya yi tunanin ya yi maganinta sai ya tuna su kawu da ke jiransu,kawai sai ya tureta ya wuce yana cewa. "Ya rage naki ki san da fuskar da zaki karbe

su,ni

dai na yi alkwarin kina kofa ni kuma zan yaga".

Ya fice ya barta,duk da cikin rudu ta ke ba ta

dauki lokacin nazarai mafita ba,da gudu ta bi

bayansa tana goge hawaye,sai ya tsaya ta a

hanya ya dinga goge mata hawaye da rigarsa bai

damu da cewa fara ce rigar tasa ba. A karshe ya

rungumeta a kirjinsa yana fada mata kalaman

rarrahi. "Calm down...ki saukakawa kanki

damuwa fadima,duk wannan kuncin ina zatar

masa sauki, hakuri da rashinsa kadan ne

fadi"....

Ya dago kanta idanuwanta a bushe. Babu

alamar

hawaye... Ya kara murje fuskarta... Da

hannayensa masu taushi, sannan ya ja ...

Hannunta suka tafi. Da nutsuwarta ta isa ga

kawu fuskarta da walwala sosai,suka gaisa

sannan ta koma ga momi ta harde mata da

shagwabar nuna kewa. Ta ce. "Amma dai ba

wajena kuka zo ba momi, tunda kuka sauka

dakin

Abdul". Ciki jin dadi kawu ya ce. " Ni dama ba

wajenki na zo ba wallahi godiya na zo yiwa

abdullahi. Tana satar harara abdullahi ta ce.

"Da

ya yi me kawu? Bayan ya kulle ni ya hana ni

zuwa wajenku... Don Allah kawu gobe a kawo min

motata".Zuciya d kwanji

.51) Don Allah kawu gobe a kawo min motata.

Nan take dama ta samu ga Abdullahi,ya

yunkura

cikin ladabi ya ce. "Don Allah kar a kawo mata

kawu, ni bana son yawo ita kuma na fahimci ba

ta son zaman gida.... Nidan so samu ne ma ta yi

irin wata shiddan nan ba ta fita ba" Fatima na

zabga masa harara kawu na karfafa masa gwiwa.

"To don me za a kasa samun abin da ake da

iko?

Me zata fita ta tsinta? Idan don ta mu ne na

dauki nauyin zan dinga dauko momi duk

karshen

wata muna zuwa ganinta,'yan uwanta maza su

dinga zuwa". Momi ma ta ce. "Haka ne, ni ma

ban goyi bayan ka barta fita barkatai ba!idan

na

ta kama ka hakura da wata sabgar taka ka kaita

ku dawo tare, sannan ka sanya ido sosai a kan

masu zuwa gidanka,duk matar da tarbiyyarta

ba

ta yi maka ba kar ka ji shakkar komai ka hanata zuwar maka gida". Turkashi! An kwance min zani

a kasuwa". Fatima ta fada tana kallon Abdullahi,wanda kamar ya kifa saboda gajiya. Babu yadda ta iya dole ta hadiye maitarta ita ma

ta bullo ta wata kofar ta rokon wayar hannun . Mommi tare da togaciyar nata sun fata ruwan zafi

sun tsaya.nan ma Abdullahi ya sako baki. "Kar ki

bata wayarki momi, jiya fa aka yi abin,kuma yau

din nan zan kawo mata wasu. Nan ma ta kuma shanyewa,ta ce. "Momi zo mu je can". Prof ya dubi agogo ya ce. "A'a ta zo mu tafi,ya ya abokan zaman naki,kuna zaune lafiya ko?" Nan ma karaf Abdullahi ya ce. "Lafiya kalau kawu,fatima kirsu su gaisa". Wani katon abu ya daki zuciyar fatima,sai ta yi sararo tana duban Abdullahi,amma tana lura da yadda iyayenta suka

sa mata ido, sai kawai ta tashi ta fita ba tare da

ta san abin yi ba, a takaice ma ko kofar dakin
kowaccensu ba ta sani ba. Kawai sai ta tsaya
jikin karfen tanki tana kananan jawaye,dama
ga
ta da arhar kuka. Shi yasan ya yi kulli babu
jimawa sai ga shi ba tare da ya girmama laifin
da
ya yi mata ba,ya hau share mata hawaye ya ce.
"Yi hakuri zo mu kirasu tare.". Bai jira amsarta
ba,ya ja hannunta suka nufi adin sadiya. Da
sauri
sadiya ta bar jikin taga ita ma da tata kwallar
don tuni ta ke lekensu tun daga rarrashin dazu
da
ya yi mata tana ganinsu,komai ya yi mata daci,
don ta hango tsabar kauna da sadaukarwa a
idanunwan Abdullahi a fatima, fiye da zaton ko
shaukin da ke rikita shi,ba ta taba samun shi a
salube kamar yadda ta ganshi da fatima a yau
ba,
wanda komai na sa na nuna kauna a gare ta,
idanunwansa,harshensa da sautinsa,wanda duk
suna samun umarni ne daga kwakwalkwasa
bayan zuciya ta sanar da ita sun hadiye tarin
kaunar fatima . Tana jinsa ya dinga bugu,sai da

ta yi yaki da zuciyarta sannan ta zo ta bude kofar,hakurinta kuma ya gaza don suna shigowa ta hau hayagaga. "Me ye ya faru zaka kwaso min wannan matar ku shigo min daki kana isa ta da ihu? Da sauri fatima ta kalle shi, amma da yake a kule ta ke, sai ta gaza barshi ya dauki mataki,ta yi tarangahumar tsoma baki. "Toh! Au kare ne shi da yake miki iju? Kin ga kuwa ko ni da nake da kason abinci kawain.uke kafada da kwallon kafa.... Ba zan ce ....." Da sauri Abdullahi yasa hannu ya rufe bakinta,sannan ya dora yatsansa akan labbansa ya amabata "hush!" Nan take ta karbi umarnin sa cike da shakkarsa har ya fahinci hakan,don haka ya dora don ta rage mata tsoron cikin zuciyarta. "Kar ki kuma yarda wannan maganar ta hada ki da wani a cikin gidan nan,ki barsu kawai su shafta iyakar fahimtarsu su fassara.... Ba na son ki kara musawa kowa kinji? Da abinci kawai kika tsira ranar girkinki duk da haka muna zaune lafiya babu wanda yasan

cikinmu,kin gane?" Ta kada kai,kawai,sannan

ya

juya ga sadiya,ya ce. "Kina da lokacin da zan ci

gaba da yi miki ihun ko na yi gaba. A tunzure ta

ce masa. "Ba bi da shi" Kai tsaye ya yafici

fatima

suka fice, sadiya kuma na yi musu Allaj ya isan

kebewar da suke a kwananta. Suna fita fatima

ta

turje ta rungume hannu, ta ce, "Abdul,idan

waccan ma kansa ba ka isa da ita ba kar ka fara

kai ni wajenta wulakanta ni,don wannan

masifar

tasu tana daya daga cikin abin da yasa na kagu

na bar gidan nan

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

53) Dama hindatu mace ce mai kara da boye

bacin rai, don haka da ladabinta sosai ta gaishe

da su kawu,yayin da abdullahi ya bayar da

uzurin

sadiya na wanka. Kawu ya hadu ya dinga yi

musu nasiha. "Don Allah ku rike amanar

junanku,babu wata rayuwa me dorewa bare

wayonka ya fissheka,an san dai zama ko da da
iyye ne ana sabawa,amma fahimtar juna ke
hana
kullaci. To ku janye kullaci a cikin zamanku na
tabbatar zaku ci ribar hakan a gaba ko bayan
kasa ta rufe idanunwanku,sab oda kun bar
iyalanku masu mutunci da zumunci". Hakika
hindatu ta ji dadi maganganun prof wanda ta
tabbatar abin da fatima ta ke kawai albasa ce ba
ta yi halin ruwa ba,kuma gatan da sadiya ta
rasa
ke nan,don kulliyar danginta tayata kishi
suke,sau
nawauwarta ke zuwa hindatu na gaishe ta tana
sharewa? Da hindatu ta ke sallama da su,sai
prof
ya mika mata dubu biyar ya ce ta raba da
yar'uwarta. Ta yi godiya sosai,da suka tashi
tafiya sai ga ta da turaren wutanta katuwar
kwalba ta kawowa momi dama sana'arta ke nan.
Fatima da Abdullahi suka yi musu rakiya har
wajen mota kafin su shiga motar ne Abdullahi
ya
dinga nuna son su kebe da kawu,kawu na
fahimtar hakan ya cewa momi. "Wai kuwa kin

leka dakin nata? Kar ta ce mun yi mata "yan goranci,ku je momi suka tafi. Cikin tsananin ladabi Abdullahi ya ce. "Kawu don Allah kar a ba wa fatima waya, babu abin da ya sami wayoyinta ni na kwashe su, ko cikin dabara ne a sanar da 'yan uwanta kar su zo ta sanya su su siyo mata waya,ko ta karbi tasu ta yi amafani da ita. A taimaka min da wannan kawu". Prof ya yi kasake

cikin bugun zuciya,ya ce. "Wani abin ta yi ko?" Da sauri Abdullahi ya girgiza kai, amma bai ce komai ba. Kawu ya kara shiru sannan ya kada kai. "Nasan ba za a rasa dalili ba, sai dai ba zan matsa maka inji ba, hasalima zan yaba maka a matsayinka na namiji mai boye sirrin iyali,kuma ina tabbatar maka zan ba ka goyon baya don in zaton alkhairi tare da kai. Ban taba ganin mutumin da fatima ta ke shakka bayan ni kamar

kai ba, saboda haka zaka iya tarbiyyarta don ba ta lankwasuwa ga mutumin da ta rainawa wayo.zan karantawa 'yan uwanta zuwa gidan nan,kai ma ka sanya ido ga kawayenta ka bi shawarar momi,duk wadda tarbiyyarta ba ta yi maka ba runtse ido ka hanata zuwar maka

gida,ka fahimci ni? Cike da farin ciki Abdullahi ya
dinga yiwa kawu godiya har momi ta fito suka
kara sallama da su suka tafi. Fatima ta yi saurin
shigewa cikin gida ba tare da ta jira shi sun jeru
kamar yadda suka fito ba. Shi ma hakan sai ya yi
masa dadi don yana fargabar kebewar su ta hau
yi masa maganar tafiya. Yana shiga ya zira
takalminsa ya fice, bai kara waiwayar gidan ba
sai da sha biyun dare ta gota kowa ya kai
bacci,kai daya idan ka dauke fatima da duniyar ta
yi mata kunci,tana jinsa ya shige dakinsa ya
garkame kofa. Sai bayan sallar asuba ya nemi
dakin hindatu domin ya wanke mata zuciya tunda
ita ke da girki. Hindatu ta yi hakuri ne kawai don
ta gane lallai akwai tarin abubuwa da ke damun
zuciyarsa a cikin lamarin fatima,sannan ta
tabbatar borenta ba zai amfane ta da komai
ba,kamar yadda bai amfanin sadiya ba, wadda
yake ganin KWALLIN goshinta a da,eh a da mana

don a yanzu yankewa abdullahi hukuncin inda
zuciyarsa ta karkata abu ne mai wahala.idan an
zuciyarsa ta karkata abu ne mai wahala.idan an
hutar da tunani ne ma za a ce akan fatima
karka
ta fada,wadda a yanzu karkarin dai ace ba ya
kwana a dakinta,ko kuma ita ba ta kwanan nasa
dakin,amma duk wata dawainiya da shakka
wadda ke tasowa karkashin soyayyarsa ita ta
mallake su. Sai ta nuna masa ba ta damu ba,
suka yi harkokin arzikinsu tare har ya shirya
fita,kafin ya sanya kayansa ya dubeta a
nuste,ya
ce. "Don Allah hindau ki yi min afuwa na je na
nemarwa yarinyar can abinci". Ta jima tana
dubansa,

Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

"54)Abu Turab don Allah wannan wanne irin
zama ne? Shin kasaitarta ce tasa ba zata shiga
kicin ta yi girki ba,ko kuma don ba ta iya ba,
saboda ta fito gidan hutu ko kuma tsabar
soyayyarta ce ta saya ba ka so ta wahala?" Kai
tsaye ya amsa mata. "Duk cikin abin da kika

fada

babu dalilin Hindatu,ki yarda dai a ranki akwai

dalilin sai dai kar ki kwadaitar da zuciyarki

sani,domin sirrinmu ne ni da ita,fahimtar

junan da

ke tsakanina da ke ya sa na nemi ki goyi

bayana.bana son kananan magangnun da suke

tasowa a tsakaninmu dalilin zuwan fatima,kin

sani hindatu ba a sanyawa namij karfi wajen

mallakar soyayyarsa,amma ana iya mallaka ta

hanyar kyautatawa da biyayya,shaidar da na yi

miki ke nan, don Allah Hindatu kar ki canja,ki

tayani neman abin da nake so sai ki ga Allah ya

dora ki a kaina na yi miki adalci ko raina bai so

ba. Ki daina bin yamma kina shan kida tunda ba

ki san abin da ke fake ba, wai har ku dinga fitar

da sirrina hindatu.ina amfanin kawayenki su zo

ki

fada musu zaman da nake da matata, wace

ribar

kika samu a hakan? Babu ma wanda ya fi

bakanta min irin sanar da muftahu da kuka yi,

raina ya yi mugun baci wallahi don dai kawai na

shanye ne. Ke kanki kuma kin san wannan ba

dabi'ar mace ta gari ba ce, ni ina saka ku kuna

warwara,idan kuka korar min ita da wanne idon
za ku dube ni? Ba zan munafubce ki ba
Hindatu,fatima tana da muhimmanci a
rayuwata".

Hindatu ta ji ciwon maganarsa ta karshe,sai dai laifinta da ya fara gabatarwa ya danne shi,don haka fuskarta ta nuna nadama.A sanyaye ta ce.

"Ka yi hakuri da yarda Allah ba za a kuma ba".

Suka yi shiru na wani lokaci,sannan ta kuma dagowa ta dube shi. "To ka je mana,sai ka yi gaggawa kar ka makara,ga shi yau monday". Ya yi firgigit ya tashi yana cewa. "Haka ne,na gode da fahimtar da kika yi min". Ya fice.ta bishi da kallo tana maimaita wasu kalamansa a fili.

.......Ki tayini neman abin da nake so.... Idan
kika
korar min ita da wanne ido zaku dube ni.........?
Fatima na da mahimmanci a rayuwata'.

Wadannan kalaman sun isa awon iyakar zurfin
da
abu turab ya yi a kaunar fatima,don duk
kaunarsa
ga sadiya bai taba fitowa a gabanta ya fada
mata

ba..... To yanzu ina mafita? Tambayar da ta yiwa kanta ke nan. Wanda ba ta yi dogon nazari ba ta shawarci kanta rungumar hakuri da juriya. Abdullahi ya jima a kofar fatima yana addu'a kafin ya fara kwankwasawa.ba a jima ba ta zo ta bude,gabansa ya kara faduwa da ya ganta kace kace da hawaye. A dan tsorace ya kawar da kai kamar bai gani ba ya ce. "Kin tashi lafiya?" Ta yi gum da bakinta, sai ya canja fuska ya ce. "Lafiyaki kuwa?" A tunzure ta ce masa. "Ni ban sani ba. Ya sassauta murya ya ce. "Allah ya ba ki hakuri,ban hanya na wuce . Me kike so na girka miki?" Ta ki ba shi hanyar,sannan ta kara bata rai,(a ce. "Ba na bukatar komai,kasan matsalata, saboda haka ita ya kamata ka magance min ba wai ka yi ta faman tura min abin ci ba. Ya dube ta da kyau,ya ce. "Na zaci mun rufe wannan maganara,bana ce ki tsumaye ni zuwa gobe ba....? Ta tari numfashinsa da masifa. "Na ce maka ban amince ba..." Shi ma ya tareta da kayshin murya. "Idan kina da abin yi sai ki yi....

Abu daya zan cire miki a ciki shi ne, sanya kafa ki ce za ki fita daga gidan nan,yaji ko wata sabgar,kina faukan wannan matakin ni ma zan dauki nawa wanda na tabbatar ba zai miki dadi ba, wato zantar da kawu.... Na ce ki ba ni gobe kin ishe ni da masifa haba!" Kamar turata ya yi ta kara ruwan masifar "Ka tafi inda ranka da taskar labarai ka fada Abdul..... Bisa wacce hujjar zaka ishe ni da naka iya yin..... Dama mun yi da kai zaka dinga kafe ni da wa"azi?. Ya amsa mata kai tsaye cikin daure fuska "Aure ne hujjar! Wanda na tabbata ko giya kika kurba kin san ba a kullo shi da wasa kamar yadda lissafinku ya wallafa ke da wancan mutumin.... Ki ni ni a hankali fatima kin ganni nan? Ba ni da dadi ni ma". Bai jira cewarta ba ya ja kofar da karfi ya barta tsaye a gurin

dakin na juya mata,so ta ke ta yarda abin da
ke
faruwa a mafarki ne, amma ta gane yaudarar
kai
ne.... Wannan kalmar ta yi dai dai a wanne
nau'in
cikin masifa?. To amma ba ta son tabbatar da
ita
da nata saurin yanke kaunar bari ta yi
tsumayinsa zuwa goben tunda ya zama
kadangaren bakin tulu...... Hindatu ta gansshi
ya
dawo akan kari,kuma a birkice. Da kirkinta tare
shi, tana dannar kirjinsa ta ce. "Anya ba zaka
bi
manganar muftahuba ku kai matsalarku gu
manya?" Ya yi murmushin karfin hali, ya ce.
"Babu inda zamu Hindu,wannan yakina ne ni
kadai, don ni kadai na zunguro sama da kara,
yakamata na ji a jikina ni kadai,ke dai kawai ki
tayani da addu'a". "Kana son fatima da
yawa".
Ta fada don zolaya da bugun ciki,amma bai
tanka
ba sai ya yi mata murmushi kawai. Ta kuma

kallonsa da wutsiyar ido,ta ce. "Wannan karon

malam ya yi abin a zo a gani a zabin da yake

maka". A nan ta samu ya amsa. "Dama can

malam ba ya zabin banza". Ta ce,"haka ne, sai

dai a samu akasi shi ya yi zabi kalmar nan ta

babu ruwan so da wayo ta yi aikinta". Ya bude

ido sosai ya dubeta,ya ce. "Ke duk fa lauyarki

ba

zaki sa ni fadar abin da zan daure kaina da

kaina

ba". Kawai sai ta tuntsure da dariya,shi ma ya

tayata,sai ya ji zuciyursa tana sanyi,wato ya

rage

'yan adawa a cikin gida,Hindatu ta bi ko ba ta

taimaka da fatar baki da KWANJINTA ba, zata

taimaka ta fannin kin tuzura masa fatima.

Amma

da ya tuno kasha di da jaye jayen bala'in da

Alh

ya yi masa a waya bayan ya kira shi da bakuwar

lamba. Ya kadu da kashedin da tsoratarwar

Alh.watsar da tsaoro bayan kaunar fatima ta

yunkura ta nuna nata fin karfin. "Hum, Allah

ka

zamo gatana". Ya furta a fili,yayin da cikin

sauri

Hindatu ta dago ta sanya masa ido,shi ma sai

ya

yi tsuru yana kallonta,alamar hankalinsa ba ya

tare da ita, ko kuma fargabar Allah ya sa bai

furta abin da zuciyarsa ke karantawa ba.

Washegari ranar bai shigo gida da wuri ba, sai

daba da magarinba. A gurguje ya yi wanka ya

fice masallaci

2 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

Zuciya d kwanji

55) .bayan sallar isha sai ya kasa barin

masallacin,ya yi ta kaiwa Allah bukatunsa har

da

hawaye,tsawon lokacin sannan ya hakura ya bar

masallacin,ya siyo musu kaya motsa baki,sannan

ya nufi gida A sanyaye yake komai,yamikawa

sadiya da Hindatu nasu,sannan ya koma

dakinsa

ya shiryo kayan baccinsa set uku cikin jaka,da

kayan sawa set biyar,kannan kaya uku,manya

biyu,da duk wani abu da yasan zai bukata cikin

kwanaki biyun da zai yi a dakin fatima,ya hada

da

wasu makudan kudi da cek. Ya rufo dakinsa ya ja jakar zuwa nata dakin bai samu kofar a rufe ba, don haka ba ya bukatar kwakwasawa,sai kawai ya shiga ya yi addu'a,sannan ya murza key. Tun daga nan gaban fatima da ke zaune tana kallonsa ya fadi. Amma fuskarta ba ta nuna razana ba, kawai sai ta kawar da kai ta zubawa talabijin ido.

Shi ma bai dube ta ba,ya wuce kai tsaye dakin baccin da ya fahimci ta fi mu'amala da shi. Ya jima a tsakiyar dakin numfashisa na neman shidewa saboda kayatuwar dakin da ni'imar da ya hada da kamshi mai dadi da sanyi mai tarar da zuciya,amma ga ma'abociyarsa cikin kunci da jazawa kai tashin hankali. Ya jima zaune gefen gado ba tare da ya yanke shawarar ta inda ma zai fara abin da ya kwaso ba, a karshe ya hakura ya dora jakarsa kan chest of drawer ya kashe wayoyinsa ya zira su a jakar sannan ya fito. Nan

ma bai dubeta ba ya wuce kicin sai ita ke binsa da satar kallo kawai. Ya zubo gasassun 'yan shilan da ya shigo da shi a faranti,ya kawo fresh
milk,lemo da ruwa yana komai cikin gumin fargabar tashin hankali duk kuwa da sanyin da ke
ratsa dakin.Don haka ya zabi kum yin wani wankan,wanda ba ya nufin komai a wajen fatima
sai jan lokaci. Ya koma dakinta ya canja wasu kayan,ya yi amfani da turarenta,sannan ya fito
falon dauke da envelop Ganinsa da wannan envelop din wani matsanancin farin ciki ya daki zuciyarta har sai da fuskarta ta nuna,sai nasa kishin ya motsa, sai dai babu yadda zai yi, dole ya hadiye shi ya share. Ya ajiye envelop din kan kujera ya zauna gaban abincin anan ya dubeta kai tsaye. "Zo mu ci abinci". Ta kawar da kai tana yamustsa fuska. "Ni fa tuni na fada maka,ba
abinci ne a gabana ba". Tana rufe baki ya amsa cikin dakewa. "Ashe ke nan zamu daga tattaunawanmu zuwa wani lokaci,domin abin da

na zo da shi yana bukatar nutsuwarki da koshinki... Ko zamu daga zuwa gobe? Ni dai nasan akwai yunwa a tare da ke, har ma kin dan rame fa! Bana bukatar mutanen gidanku su ganki darama". Ya zuba mata ido kawai sai ta yunkura ta tashi zaune tana gyara riga.ta yi fuska ta ce. "Sai ka zubo min nawa,don babu dalilin da zai sa ka ce sai na ci abinci da kai". Ya ce,"na sani,amma tunda babu dalilin da zai hana mu ci tare,ina laifi don mun ci? Ranar yau ta zame mana ranar tarihi mana fadima? Zo mu ci don Allah ki yi hakuri da laifin da kike jin na yi miki,in Allah ya so zai takaita shi". Sai ta kasa tankwabe magiyar tasa, musamman da yake yayi mata magana cikin taushin harshe.Amma tana ji a ranta shakkarsa ce kawai ke dawainiya da ita,kamar ba ta son bacin ransa. Ta tashi ta shiga bandaki ta wanko hannu da baki,sannan ta

zo ta zauna gabansa ta tankwashe kafafunta

suka fara ci. Kamar dama don ita ya tashi cin

abincin,ita ya dinga yiwa hidimar zarewa kashi

yana tura mata tsokar gabanta abin da ya kara

faranta ransa ba ta takwabe kokarinsa har sai

da

ta gamsu sannan ya zuba mata madara ya mika

mata, ajiye kofin ta dauki ayaba guda ta koma

gefe tana cinyewa ta tashi zuwa kicin ta koma

gefe tana cinyewa ta tashi zuwa kicin ta wanko

baki da hannu,sannan ta dawo ta zauna tana

tsumayinsa,wanda sai sannan ya mayar da

hankalin yana cin nasa. Ya dinga yanga kamar

ba

ya so har dai ya kai ga kammalawa ya kwashe

kwanukan ya wanke nasa bakin,sannan ya cin

mata, inda kai tsaye ya zarce ya dauki envelop

din ya mika mata,bai jira ta ce wani abu ba ya

wuce daki ya dauko kudin da ya zubo a jaka.

Kafin ya fito ta farke envelop din ta zaro

takardar

da maimakon takardae saki uku sai ta tarar da

taller da copy na cek din kudin na 700,000.

Wanda cikin sakanni ta gane dangantakar cek

din

da Alh. Taller ma ta shigar da wannan kudin wani
asusun ne. Fiye da wasu sakanni masu dama zuciyarya ta tsaya da aiki cak! (0) ke nan,ta ki gana (+) ta ki baya(-),don haka ta kasa dorar da
komai bare ta yi tunanin baya.tana tsaye da takardu a hannu kamar mutum mutumi idonta akan kofar dakin da Abdullahi ya shiga,har Abdullahi ya fito,sannan zuciyar tata ta fara harbawa harta aikawa kwanyarta sakon neman dalili ita kuma ta yiwa harshenta umarnin furtawa. "Ina bukatar karin bayani Abdul". Ya yi
fuska ya ajiye kudin kusa da kujerar da ta ke zaune a hannunta,sannan ya dauki remote ya nemi guri ya zauna,ba tare da ya dubeta ba ya ce. "Kudin da Alh ya ba ni ne nake nufin dawo muku da shi don in son na mallaki 'yancina da kudin ya sarayar, hakan zai ba ni damar ci gaba da yiwa Allah biyayyar da kuke son gotar da ni,ya
kuma ba ni damar zama da abin da raina ke so ba tare da an yi min kallonm mai ci da karfin ba".

Ta mike cikin tangadin tashin hankali, sannan ta
dake ta tsaya da kafafunta tana fuskantarsa,ta
ce. "Gajarta min abin da kake nufi a kalmomi
goma zuwa ashirin idan zai samu" Tana rufe baki
ya amsa mata " Na karbi tayin auren kisan wutar
da Alh ya yi min da zummar in kubuta da ku
zaman haramcin da kuke yiwa kanku tanadi tun
kafin a sanyaki a idona. Na dauki hakan jahadi,sai
aka dace ina dora idanuna a kanki na kamu da
matsananciyar kaunarki.daga lokacin na fara
nawa acting din wanda ya sha bam ban da
naku...." Ta dakatar da shi cikin haki da neman
sarkewar numfashi,cikin kakkausar murya ta ce.
"Ya ishe ka! Zan duddura maka zagi wallahi! Bai
damu da masifarta ba,ya tari numfashinta. "Ki
zage ni mana fatima,sai me? Kin san dai zagi ba
hanya ce ta samun solution ba, kuma bai cika
zubar da kimar wanda ya yi, musamman idan

wanda ya isa ya zagi wanda bai isa ba".

Hankalinta kamar ba ya jikinta ta watsar da

takardar ta nufe shi gadan gadan kamar tana

zuwa hadiye shi zata yi. A nan zan dakata,sai a

nemi littafi na biyu don dorawa. Taku

MAIMUNATU IDRIS SANI BELI

3 · Like · React · Report · May 14, 2015

Amierah S-Man

SAI KUYI MUN UZIRI.... PART2 SAI ANJIMA KO GOBE... ASHA KARATU LAFIA

Compelled by hauwee jidderh abdulkadir AKA mssjidderh